Salmu
Hassan

Bayan wuya



ALBASA

Salmu Hassan

BAYAN WUYA ...



Wanda ya zana hotuna:
Issa Tahirou

❖

P.A.O. / Wanda ya shirya aikin bisa na'ura:
Danbourgami Magawata

❖

ISBN : 99919-0-009-8

Tous droits réservés
© 2001 Ministère de l'Education Nationale
Edition Albasa s:c GTZ - 2PEB, BP 10814, Niamey

Impression et reliure :
Imprimerie Albarka

Gabatarwa

Godiya da yabo sun tabbata ga Allah maɗaukakin sarki da Manzonmu Annabinmu Muhammadu (SAW) tsira da aminci su tabbata gare shi amin. Allah na gode maka da ka ba ni basira da hikimar rubuta wannan littafi mai suna Bayan Wuya... Na rubuta shi ne kawai don na faɗakar da jama'a maza da mata musamman ma ma'aurata, a dinga taka tsantsan a cikin rayuwar zaman duniya. Mata in an yi aure a san waɗanne irin tsofi ya kamata a bai wa amana domin ko maihaifiyarki ya kamata ki san waɗanne irin maganganu ya kamata ki faɗa mata game da rayuwar aurenki. Ciki fa ba a yi shi don tuwo da fura ba. A dinga riƙe sirrin aure. Maza in an yo wani auren to a girmama uwar gida a kuma san fa, da tsofuwar zuma ake magani, kuma uwar gida ai ita ce ginshiƙin gida. Bayan wuya ... littafi ne wanda yake tattare da ruɗani, da ban tausayi, da ban haushi da ban mamaki. Akwai faɗakarwa game da mata da maza, su yi hattara a cikin rayuwarsu ta aure, a san irin abukkan da ya kamata a bi.

Na sadaukar da wannan littafi ga mahaifina Hassan Hima tsofon soja ne da ya yi ritaya tare da mahaifiyata Bibata Kimba mai laƙabin sunan Lamisi.

Wannan littafi tukwici ne ga mata yan uwana musamman ma matan ƙasarmu Nijar, waɗanda suke faɗi ka tashi don neman halaliyarsu.Matan da suka kama darajar aure, waɗanda suka san ya kamata. Bayan wuya ... tukwici ne musamman ga matan da ke cikin ƙuncin zaman aure Allah ya warware masu Amin.

Godiya da yabo sun tabbata ga ubangijinmu Allah Maɗaukakcin Sarki, tsira da aminci sun tabbata bisa ga Manzo Annabinmu Muhammadu (SAW). Na yi godiya na kuma yi hamdala da Allah ya halice ni, ya kuma ba ni rai, da lafiya, da ilimin da na rubuta wannan littafi mai sunan Bayan wuya ... Ina addu'a tare da fatan zai zame muna mai amfani. Haka nake miƙa matuƙar godiyata ga yan uwa da aminnan arziki waɗanda suka taya ni, suka kuma taimaka min ta hanyoyi daban-daban, tun daga farko har ƙarshen wannan littafin. Ga sunayensu kamar haka:


Malam Jaharou Souley da malama Nana Aichatou Aboubacar, masu bayar da shawara da horo a fannin rubuce-rubucen hausa, da sunan gidan buga littattafai na "édition Albasa".

Mme N'Diaye Nana Hadiza, Mme Addo Lydia Ibrahim yar jarida a sashen hausa na radiyo Amfani, Sergent Issa Hassan, soji a ma'aikatar kwana-kwana ta Yamai, Mme Hassan Bibata a Yamai, Djibo Hassan a ma'aikatar ENITEX, Zainabu Saley a ma'aikatar kiyaye mahalli.

Tare da fatan Allah ya saka musu da alherinsa Amin.

Salmu Hassan

Yau tara ga watan rajab, hijirar Mazon Allah Sallallahu Alaihi wa sallama, wanda ya zo daidai da ranar juma'a sha biyar ga watan agusta, shekara ta dubu ɗaya da ɗari tara da gomiya tara ta tara haifuwar Annabi Isa. An tabka ruwan sama kamar da bakin ƙwarya. Farid mai gidana na kwance bisa manya-manyan kujerun da suke cikin falonmu, ya ɗora ƙafarsa ɗaya bisa ɗaya, yana kallon talabijin. Ya juyo ya kalli agogon bangon da ya nuna ƙarfe tara da minti shida.



Farid dai dogo ne, fari pas mai kyawon gaske mai yawan ɗumi da son ba da dariya. Haka ya sa ya yi farin jini wurin jama'a, ga shi da shiga mutane ko da yake unguwar da muke ta manyan mutane ce. Daga manyan yan kasuwa sai manyan ma'aikatan gwamnati. Ba ruwan wani da wani. Kun yi wata ba ka sadu da

maƙwabcinka, ko kuma ba ku ma san juna ba. Amma Farid ba wanda bai san shi ba cikin unguwar domin kowane daren juma'a sai ya biya gida-gida yana gaisawa da mutane. Lokacin da ya maida hankalinshi wurin film kin da yake kallo, yara suna wasansu a waje guda, suna ta kokowa.

- Kai, sai na ba ku kashi ko?, Ba ku bari? Irada kina kallon ƙannenki suna kokowa ba kya raba su, ko sai sun ji ma junnansu ciwo? Batancinku ya ishe ni hakanan. Gare ku aka fara tawaici? In na ƙara ganin ku kuna kokowa sai na ba ku kashi. Kai Shamsu dawo nan, ke ko Shamsiya tashi ki koma wurin Irada.

Ya koma ya kwanta kenan, sai aka buga wata babbar tsawa sai da aka ɗauke wutar lantarki. Yana mamakin dalilin tsawar domin ya kai minti talatin kenan da aka ɗauke ruwan. Ya tashi da sauri ya nufi kujerar da Shamsu yake zaune ya ɗauko shi ya je ya zauna kusan su Irada, ɗiyarshi ta fari, suka kankame shi don tsoro.

Bayan minti bakwai aka maido wutar har yan tawayen sun yi barci saboda tsoron da suka ji. Ya kai Shamsu cikin ɗakinsu ya shimfiɗe shi; ya bar Shamsiya bisa wata kujerar, sai in na sauko daga wurin aiki domin bisa benen muke barci.

- Irada ke ba kya barcin ne? Gobe fa kuna zuwa makaranta!
- Na sani baba amma sai mama ta dawo zan yi barci.
- To shikenan. Allah ya kawo ta lafiya.

Ina zaune cikin katafaren ofishina; ina karanta tulin takardun da mataimakina ya kawo mani. Na kalli agogon hannuna: ƙarfe tara har da ɗori. Na ga ya dace na buga ma angona Farid waya don ya zo ya ɗauke ni domin ba ni da mota, tana gareji wurin gyara.

Waya ta yi ƙara, Irada ta tashi da gudu ta je ta ɗauka:

- Inna ni ce, in kirayo baba? Ban yi barci ba… To, ga shi nan.

Farid ya karɓi wayar:

- Amarya ta ango, amarya ba kya laifi ko kin ba ɗiyan masu gida kashi.
- To rabin raina, mi ya faru?
- Don Allah ka rufa mini asiri ina ni ina amarci bayan shekara goma sha biyu da aure?!
- Wallahi Farida a gurina kullum amarya kike; na san kuwa haka nike a gunrinki.
- Gaban Irada kake waɗannan irin maganganun?
- Irada ba ta wurin kuma ko ta ji ta koyi yadda ake tattalin

miji kamar yadda kike mini. Tarbiya ai a gida ake koya ma yaro ita ko?

- To ai ba kowane maganganu za a dinga faɗa gaban yara ba mana kai kuwa Farid. Motata ta samu tangarɗa ka zo ka ɗauke ni.
- To ga ni nan zuwa yanzu insha Allahu. Kar da ki samu damuwa. Minti nawa kika ba ni?
- Kai dai ina jiran ka.
- To lumfashina, ga ni nan, ba ni da jirgi, da cikin shi zan zo. Kin san jirgi ya fi sauri.
- Kar da ka zage ni.
- Farida ai kin wuce zagi. In zage ki? Haba mana, na yarda?! Ai da kashina ya bushe.
- Farida sai na zo ko?
- To ina jiran ka.

Farid ya aje waya ya ɗauki motarshi sai gidan talabijin. Cikin minti ashirin muka dawo gida. Da shigata, na kwanta bisa doguwar kujera wadda Farid yake bisa ita kan ya je ɗauka ta. Farid ya zo ya zauna dap da ni ya ƙura mini ido ya ɗauke hannun da na ɗora bisan kaina yana murmushi, wai shi "amaryarshi" ta zo.

- Abin begena ai kin ga na ba ki wahala. Kullum a gajiye kike zowa gida.
- Wallahi Farid kamar ka sani, aikin ya mini yawa ba a yin minti biyar ban samu waya ko wani ya shigo ba. Ba ka ga ba saboda shi ne, ba na rabuwa da ciwon kai? Yanzu haka ina tare da ciwon ƙan.
- Bari na tashi zama bai same ni ba, rabina ba ta lafiya.
- Na ɓata rai.
- To shi kenan.
- Farid, lokacin da aka ba ni wannan matsayin sai na riƙa jin dadi ina gani kamar ba kamata a duniya. Yanzu ga shi nan kullum roƙon Allah nake a sauya mini wurin aiki. Wallahi Farid na gaji.
- Sa haƙuri Farida domin akwai masu neman wurin nan naki ba su samu ba. Bari ki gani kamar kin mance in dai da rai da lafiya.

Ya kafe idanunshi gare ni na ture shi ina dariya.

- Ka fara ko? Bari na tashi na je na watsa ma jikina ruwa don na ji sanyi.

Ina ƙokarin tashi sai ya ce ai shi bai gama tadî da ni ba.

- Don mi kike son taushe mini hakina? Ya rungume ni kamar an ce za a ƙwace ni daga gare shi.

Irada ta bayyana ga matattakalar benan mai kawowa ta falon da muke zaune. Na ce mashi don Allah ya san inda za ya riƙa yi mani wasa da kuma lokacin da za ya riƙa yin ta. Mu masu yara.

- Irada ba a yi barci ba? Mi ya hana miki barci?

- Ku nike jira.

- Lafiya dai ko? Diyata zo na ji.

Na zaunar da ita bisa cinyoyina na sumbace ta tana karkare "barni" da ke ga yatsunta.

- Irada ban hana ki saka barni ba ina gaya miki har kullum in kina da barni arwallar ki ba ta cika ba. In ba arwalla ai ba salla ko?

Ta sunkuyar da kai, Irada fara ce pas kamar ubanta, komi nata na ubanta ne sai dai yawan gashin kanta da wushiryar, ni ta biyo. Shekarunta goma sha ɗaya. Tana zuwa makarantar ɗiyan masu hannu da shuni. Ta fannin karatu na ƙur'ani izifinta talatin da ɗaya.

- Mi aka yi ne? Irada?

Irada? Babanta ya zauna yana kallon mu. Ta kawo bakinta har ga kunnena don kar babanta ya ji abin da za ta faɗi. Farid ya kalle mu ya girgiza kai ya yi dariya.

- Inna ina son ku saya mini yan kunnai da sarƙa na zinariya masu giwaye, waɗannan da ake yayi.

- To na ji, yanzu duk sarƙokin da ke gare ki ba su ishe ki ba? To ai duk na zinariya ne ko?

- Inna ai na giwaye ake yayi yanzu. Duk yan makarantarmu ba wadda ba ta da su.

- To na ji. Tashi ki tafi ki kwanta. Insha Allah zan saya miki shi, kin ji yar mama?!


Ta tashi tana tsalle ta haye bene da gudu.

- Kun ida da gulmar taku?

- Mun ida Farid.

Da Irada ta tafi sai Farid ya tashi tsaye. Har na fara taka matattakalar benen domin nan ne ɗakin barcina yake

sai Farid ya caɓe ni ya ɗauke ni ya rungume ni kamar wanda ya samu ɗanshi, sai cikin ɗakin barcinshi. Ya jefar da ni bisan lallausan gadon barcinshi muka fara wasarmu ta miji da mata.



Washe gari da misalin ƙarfe takwas na dare muna cikin falo muna cin abinci tare da Bashir, babban yayana da matarshi Riyanatu yar yayar babanmu. Farid ya ɗauki cinyar kaza ya fizga ya aje. Ya ba ni dariya sai na sunkuyar da kaina don kar a gane. Ya koma ya fizga ya aje. Ya shafe bakinshi da mushuwar.

- Farida wai da naman kaza da na zabo wanne ya fi dadî? Gardama muka yi, ni da Bashir jiya.

Na tunsure da dariya da ma ina neman abin dariya.

- Farid duk yanda aka yi "yasa", shi ya ce "dadî".

Na fadî haka ne domin wani girki da ake ce ma "yasa da naman kaji" na yi.

- Kina zaton santi na yi ne?

- Wa ya kawo zancen santi a nan?
- Don yana mijinki? Santi ka yi Farid? inji Bashir.
- Bashir haka yake kullum bai hira sai in yana abinci.
- Kai ku ji tonon asiri, inji Bashir wai yana maimaitawa don na ji.
- Gaskiya ne abokina, bawan ciki.
- Na ji, tarayya za ku mini Bashir?
- An yi Farid!
- Farid bari na shigar maka inji Riyanatu tana dariya.

Haka dai muka ci gaba da cin abinci ba tare da kowa ya yi magana ba. Sai can Farid ya yi gyaran murya.

- Sai da kuka tuno mini lokacin da muna Baljik.

Duk muka tuntsure da dariya.

- Wai ana magani kai yana ƙaba, na faɗa ina dariya.
- Bar shi ya faɗa Farida. Lokacin da kuna cikin gonakan shinkafa dai. To sai ka yi mi? Ka ci gaba mana Farid.
- Bashir, ni za ka mai da abin wasar ka?

Ƙarar waya ya katse musu hirar. Da yake Farid ke kusa ga wayar sai ya ɗauka, ya juyo wajena.

- Farida taki ce, daga ma'aikatarku ne.

Na karɓi wayar.

- Alo!
- "Malama darakta ina wuni"!
- Kader ne? Kader shi ne mataimakina muna zaman girma da arziki da shi.
- "Yanzu aka muna waya daga fadar shugaban ƙasa. Ya katse ziyararshi. Zai dawo nan da minti arba'in".
- Ko lafiya?
- Ban samu cikakken bayani ba.
- To ga ni nan zuwa. Kan na zo, in iske mai kyamara da ɗan jarida huɗu.
- To darakta.
- To zan bar ka nan sai na zo.

Na aje wayar, Farid na kallo na.

- Ina zuwa kuma? Na san ba banza ba.
- Filin jirgi tarbon shugaban ƙasa.
- To ban yarda ki yi kwalliya ba. Kai, Allah! kai ka ce matan mummunai su ƙoye kwalliyarsu in za su gaban waɗansu mazaje; ka taimaka mani a sauya ma Farida wurin aiki!

- Farid kana ba ni mamaki. Kar na yi kwalliya? Na tafi gajagaja? Ai sai a rena ka, a ce matarka ƙazama ce.
- Ni dai na ce miki kar da ki yi kwalliya domin kwalliyar mace tana ta da ma maza shawa, balle dai waɗannan tsofaffin kurayen.
- Kai Farid su wane ne tsofaffin kurayenka?
- Wallahi in na ji an ce ana taron da aka gayyaci yan jarida to wallahi ba na barci don na san babu irin miyagun mutanen da ba a samu a gurin.
- Don tsananin kishi dai ko? Su Farid akwai kishi.
- To ku gafarce ni zan shiga na shirya.
- Bari Bashir, wallahi. Dole na firgita. Mai mata irin Farida ai bai samu ta zama ba.
- Kishi dai ya ma yawa Farid, don kana da kishi ne Allah ya ba ka mata yar jarida.
- Kullum roƙo nike a sauya mata wurin aiki.
- To Farid ko'ina aka kai ta duk ɗaya domin karatun jaridanci ta yi.

Na fito sanye da waɗansu kaya wai su "organza", masu ɗaukar ido, masu ruwan ganye, an musu ɗinkin da ake ce ma "turwa kar". Na yafa mayafi kalar kayan takalmi masu tsinin gaske rufaffu baƙake da jikkar hannu ita ma baƙa kamar takalmin. Duk ɗiya mace kyau gare ta in har tana kwalliya. Hankalinta kwance yake in har tana da sutura da kayan kwalliya. Sai dai lalle Farid yana da gaskiya, kamata ya yi mace ta yi ado da kwalliya don ɗaukar hankalin mijinta ba don ɗaukar hankalin wasu maza ba. Na zo za ni fita, Farid ya murtuƙe fuska, ya tashi ya kalle ni sama da ƙasa.

- Wallahi Farida ban yarda ki fita da wagga kwalliyar ba.
- Farid don Allah kar ka sa ni na yi latti domin mu ya kamata mu fara zuwa.
- To tafi ki sake kwalliya.
- Wai Farid don mi kake da kishi haka don Allah Bashir ka mai magana.


Na durƙusa gabanshi na kamo hannunwanshi.

- Don Allah Farid ka bar ni na tafi lokaci ya mini.
- Tashi ki je tunda dai kin sa mayafi.

Na ɗauki motar gidan talabijin wadda gwamnati ta tanada don ni. Farid ya zo ya zauna suka ci gaba da hira, su da Bashir da Riyanatu.

- Farid wanan kishi naka har ina?
- Bashir dole na yi kishi. Amana baba malam ya ba ni ita.
- Allah sarki Farid yanzu ...
Ya katse mashi magana.
- Kai tsaya, yanzu mi? Kar ka tayar mini da zancen da ya wuce, ka ji, na san ka da tonon asiri.
Bashir ya yi dariya.
- Ni ke da tonon asiri? To a bar maganar.
Bayan kwana biyu ina cikin ofishina ina waya sai Uda ta shigo da kuka. Na yi sallama da mai mini wayar, na tashi na tarye ta, na zaunar da ita bisa ɗaya daga cikin kujerun da ke cikin ofishin nawa waɗanda na tanada don baki. Da ƙyar na lallashe ta ta bar kukan.
Uda dai balaraba ce, aiki ya kawo mijinta Taleb a Nijar, Taleb shi ne mataimakin jakadan ƙasarsu a Nijar. Wurin sunan gidan praminista muka haɗu. Mun yi hira ƙwarai da ita. Daga nan muka ƙulla abutta muna ziyartar junanmu har mazajenmu su ma suka ƙulla abutta. Uda ta mai da ni tamkar yar uwarta, ba abin da take ɓoye mini.
Wata biyu kenan da Uda da Taleb ba sa jin ɗadin zama da juna, kullum suna rikici. Tana zargin mijinta da neman auren wata yarinya.
- Uda, Uda ki saurare ni. Kishi ba hauka ba ne. An ce masifa sama take, kar mutum ya janyo ta ta faɗa bisa shi. Dibi yadda kika koma. Ba ki ci ba ki sha. Hauka kawai kike. Abin da ba ki ma tabbata ba. Jiya Farid ya kiri Taleb a waya kamin ya tafi, ya ce kishi dai ne ya miki yawa. Bai taɓa tunanin wata in ba ke ba.
- Bai gayi gaskiyar lamarin ba. Farida na rantse ne da ba na zama da kishiya sai dai na koma garinmu.
- Uda kwantar da hankalinki. Yanzu abin da nike so gare ki shi ne ki bar ta da hankalinki. Kin san sarai da ba a yo namiji don mace ɗaya ba ko? Ko zancen ya zamo gaskiya ne abu guda za ki yi shi ne ki dukufa a roƙon Allah. Ban ce ki je wurin malami ko boka ba: in kin yi salla ki roƙi Allah, kowane dare ki tashi ki gabatar da nafila ki roƙi Allah ya rufa miki asiri abin da duk wani ya ƙulla miki ya faɗa bisa kanshi kawai.
- Farida don mijinki bai auro miki kishiya ne ba kike faɗar haka? Don ba ki san halin kishi ne ba. Mu fa uwarmu kishiya ta yi mata

sammo har ta mutu ba mu gan ta ba. Farida kin yi sa'ar miji, shi ba ruwan shi da mata, wallahi in ni ce aikin gwamnatin ma sai in bari.
- Na raba ki, ni kin za ki ce ban san halin kishiya ba? Zan ce ma na fi ki sanin halin kishiya. Ba ke kin gani ne ga uwarku ba? To ni an mini ne.
- Haba Farida yanzu ke za ki ce an miki kishiya, irin yadda kuke zaman ga naku?
- Bari Uda ba ki san wuyar da na sha ba kamin wannan lokacin. Amma yan karin magana suka ce bayan wuya sai daɗi.
- Wuya kika ce fa Farida?
- Wuya Uda, bari gobe subdu ki zo na ba ki labarina.
- Ai a gidanki nike duk na kwaso kayana. Yanzu jiran Taleb nake ya dawo na koma ƙasarmu.
- Kar ki faɗi haka! Amma wallahi Uda kin cika hauka; kin san sarai da Farid bai barin ki ki zauna gidanmu.
- Farida ba zan iya zama ba da Taleb.
- To tafi ki jire ni gida, ga ni nan.
- To sai kin zo.



Ƙarfe tara daidai na dare muka mayar da Uda gidan mijinta ni da Farid, bayan mun mata nasiha. Ran asabar Uda ta zo gidana tun da safe kamar yadda muka yi alƙawali da ita.
- Uda kina iya jira na har na dawo ko? Angona zan raka filin jirgi. Ƙasar Faransa za shi.
- Ƙasar Faransa?
- E! Taleb bai dawo ba ne?
- Bai dawo ba amma ya mini waya ɗazu-ɗazun nan kamin in fito. Ya shaida mini da uwarshi ta fara samun lafiya.

- Allah ya ƙara koro mata da sauƙi. Injin dai kin shaida ma Taleb da za ki zo nan.

- Kai Farida mutumen da ba ya ma a garin ne sai na shaida mashi inda za ni?

- To in dai ba ki gaya mashi ba tashi ki koma gidanki, in ba ya ganin ki ai Allah shi yana ganin ki ko? Kuma Uda kin san zai iya ya buga miki waya in ba kya nan, kin san ba zai ji daɗi ba kuma duk hankalishi sai ya tashi in ya ji ba ki nan. Sa kanki a gurbinshi mana?

- Na ji Farida, wannan gaskiya ne.

- Balle ke mai kishi haka.

- Zan buga mashi waya yanzu na shaida mashi.

Farid ya leƙo ya kire ni.

- Farida ki zo mana ko sai jirgin ya bar ni.

- Ina zuwa Farid.

Da ya ga Uda sai ya kama zolayarta.

- A'a, Uda kar dai a ce yajin ne kuma.

- Wa ce ni. Na zo ne na muku hira.

- To madalla! Ina kaɗaici?

- Sai haƙuri Farid.

Na shiga ɗakinmu don na idar da shirya kayan da Farid zai yi amfani da su. Mun fito ina ɗauke da lehensa, yara sun zo, Farid yana sumbatar su da ɗaya, ɗaya. Suka mashi "Allah ya kiyaye".

- Irada ku ma Tantinku hira har na dawo kun ji?

- To mama.

Uda da yara suka raka mu har bakin ƙofar gida sai da na ta da motar suna ɗaga ma babansu hannu.

Na dawo daga rakiyar Farid na iske Uda da yara suna cikin gwadala suna girki. Da suka gama suka ɗauko tuwon suka yo wajena na raba musu.

- Mama ni na yi miyar, ku tambayi Tanti.

- To Irada Tantinki ta ɗora miki?

- Wai baba ya ce ban iya girki ba. Don Allah mama ku ci ku jiya.

- Bari ran da zai zo sai na bar ki kin yi girki.kar mu gaya mashi sai in ya gama ci tukuna; in yana da dadi zai faɗa, in kuma bai da dadi kin ji ya yi magana.

- Yawwa Mama! Mama kun gaya mashi kyautar da ya ce zai mini? Mama, lokacin da na zo ta biyu a ajinmu ya ce in har na zo

ta farko zai ba ni wata babbar kyauta. Ga ya nan har so biyu ni ce ta farko amma bai ba ni komi ba.

- Kina da gaskiya Irada in ya isa Paris; zai mini waya zan tuna mashi nasan dai mancewa ya yi.

- To Mama.

- Inna ni ma ina son kyautar.

- To Shamsiya.

- Mama ni ma ina so.

- To Shamsu. Ku duka za a kawo ma, kun ji?! Uda, wai Farid don rashin aiki cewa ya yi wai ya bar gidan a hannun Shamsu domin shi kaɗai ne namiji a tsakanin mu.

- To gaskiyar shi mana.

Na juyo na kalli yayanmu da ke zaune kusa da mu.

- To yara ba kun ƙoshi ba? To kowa ya je ya kwanta sai da marece ko? Ku tashi.

Bayan yaran sun tashi Uda ta matso kusa da ni.

- Farida zan miki wata tambaya.

- Allah ya sa na sani Uda.

- Wai don mi in kina gida kin fi so ki zauna ƙasa, alhali ko ga ku da kujeru "na gani a faɗa"?

- Wallahi Farid ya saba mini, ba ki lura da shi ne ba? In yana nan ko abinci a ƙasa muke ci. Haka ko cikin ɗaki ne sai barci ke hauda shi bisa gado. Sau da yawa a ƙasa yake fara barci sai in na ta da shi. Ba ki gani saboda haka ne ma ba na so abin da ya taɓa mini shimfiɗar ƙasa, kullum a tsabtace take.

- Allah sarki kuna birge ni, inda ma a ce ni ce. Ke dai Farida Allah ya ba ki miji na gari, don haka ni kullum in zan zo ina Allah-Allah in iske Farid gida. Irin wasannun nan da kuke yake birge ni sai in riƙa ji inda ma a ce ni ce.

- Kar abin da ya faru gare ni ya faru ga kowace ɗiya mace. Kai Uda har ba na so na tuna baya.

- Farida ki ba ni labarinku mana.

- Shi zan ba ki yanzu ba da ɓata lokaci ba.

Na yi tsaki na ɗauki matashin kai na zauna. Na jingina ga kujerar da nike zaune gabanta. Uda ta koma bisa kujerar da ke gabana.

- Kin ji Uda, mahaifina dai mutumen wani ƙauye ne. Garin yana cikin gundumar Kolo, asalinmu fulani ne. Mahaifina mallami ne kuma su biyu ne wurin; daga shi sai yannunshi Adamu da

Hawa. Adamun ya rasu tun kamin a yi sunansu, sauran shi da Hawa. Baba yana da shekara goma ya sabke Kur'ani, abin da ba a taɓa yi cikin garinsu ba. Don haka ya yi farin jini sosai ga mutanen garin. Yana da shekara goma sha biyar iyayenshi suka rasu. Zaman garin ya gagare shi. Sai ya fara yawace-yawacen neman ilimi da aikin yi. Ya je Sakkwato, ya je Kumasi, ya je Yamuskoro. Yana da shekara ashirin daidai Hawa ta aika masa wasiƙa, za ta auri wanda ya ba shi sadakar ɗiyarshi Kaltumi. Yanzu kai zama garin ya zame mai dole. Malamin ya ba shi gona da yan kuɗi don ya yi sana'a. Yana zuwa Yamai yana ɗauko yan kunnai da rigunan mata yana kaiwa ƙauye-ƙauye yana sayarwa.

Bayan shekara biyu ya koma da zama a Yamai tare da uwata da yayana Bashir. Ya gina yar bukkarshi cikin wata unguwa da ake ce wa "share ka zauna". Wata rana in sun ci, wata ranar sun yi kwana biyu ko uku ba su ci ba. Baba sai ya ma wani addu'a suke samun kuɗin sayen ruwa, da gari, da sauran su. Da yake lokacin siyasa ne, wani maƙwabcin su baba, mai gadi gidan wani babban ɗan kasuwa mai neman shigar takarar yan majalisa, ya shaida ma Alhaji Kasum da ya san wani malami yaro da yake koya karatu. Alhaji ya aika direbanshi a ɗauko baba don ya taimaka mashi da roƙon Allah.

Allah da ikonshi sai Alhaji ya zamo na farko domin duk cikin yan takarar ya fi su yawan ƙuri'u. Alhaji ya yi farin ciki domin jam'iyyarsu ba ta yi wata biyar da kafuwa ba. Alhaji bai yi zaton haka ba. Ya tambayi baba abin da yake so. In har kuɗi na ba mutum abin, to ya same shi. Baba ya shaida mashi da wurin zama yake so domin a "share ka zauna" yake da zama. Washe gari Alhaji ya aiko mota aka maida mahaifana wani gida ginanne mai ɗakuna uku. Alhaji ya tanada musu abinci da kayan da za su yi amfani da su. Daga nan baba ya zama malamin Alhaji, ko in ce ma ɗan uwanshi domin duk shawarar Alhaji na hannun baba.

Ko da yake baba yaro ne, shi ke ba da salla a unguwa. Yana da mutunci a idon mutane. In wata rigimar ta taso, ko ta aure ce baba ake kirowa. Kuma cikin ikon Allah ya shayo kan matsalar. Kwanci, tashi, sai aka samu cikina. Da yake Alhaji shi ne yake ma baba komi domin a kowane ƙarshen wata shi yake biyan kuɗin pampo da na wutar lantarki, ya ba da kuɗin kayan miya. Alhaji ya ɗauki baba suka je ganin Inna da abin da aka samu. Ya

yi farin ciki da ya gani mace ce aka samu. Sai ya ba da sunan Farida ya kuma shaida ma baba da ɗanshi Farid aka haifar ma mata. Ya roƙi iyayena ko ya mutu ne a aura ma Farid ni. Baba ya ce shi kuwa ya ɗauki alƙawali, ko ya mutu ne Alhaji ya aurar da mu.

Da shekarun Bashir suka kai bakwai sai Alhaji ya zo ya tafi da shi. Baba kamar ya yi kuka. Alhaji ya yi ta kawo masa dalillai masu mahimmanci. Duk maganganun da ya yi ba su gamsar da baba ba domin a zatonshi Bashir makarantar allo zai yi; ya ma fara yana da izihi biyar. Ya dai bar Bashir don girman Alhaji. Ya san da roƙon Allah za ya yi ma Bashir don makarantar ta fita daga cikin zuciyarshi. Rana ɗaya Alhaji ya kai Farid da Bashir makaranta ta biya. Farid da Bashir suka zama tamkar ciki ɗaya suka fito komi tare suke yin shi. Wanda bai san su ba zai yi zaton yan tawaye ne domin kaya iri ɗaya Alhaji ke ɗinka masu. Kullum suna tare. Farid da Bashir ba sa son abin da ya taɓa ni. Kullum ina tare da su cikin su nake wasa hakan ya sa ba na da abukkai yan mata, su suke koya mini karatu domin tun ina da shekara biyu Alhaji ya sa ni makaranta kuma makarantarmu ɗaya da su Farid. Yaro ko ya yi hauka bai taɓa ni. Ga ni ko da ɗan karen jan faɗa. Yan ajinmu ko sun yi hauka ba sa kallo na domin daga ka kalle ni zan gaya ma Farid ya zo ko ya tabka ma yaron ɗan karen kashi. Duk abin da za a yi, Farid nike gaya wa domin Bashir ba ruwanshi da faɗan kariya. Bayan Farid Hajiya ba ta sake haifuwa ba haka ya sa ya zama ɗan lele sai abin da yake so.

Ina da shekara goma ne yar baba, Hawa wadda suke da zama a Paraku ta zo ta tafi da ni don na je na taya su fidda kewa ita da ɗiyarta Riyanatu wadda ta girme ni da shekara ɗaya domin, mijinta ɗan kasuwa ne, bai kwana biyu a gida. A daidai lokacin nan kuma Alhaji baban Farid ya tafi umara. Da ya dawo bai iske ni ba ya yi faɗa kamar ya yi kuka. Ya yi ma baba faɗa don mi ya bar ni na tafi. Ya ce in a gabanshi ne da ba zai bari Hawa ta tafi da ni ba.

Tun lokacin nan ne rabo na da in ga Farid da Bashir. Amma shekarar da suka samu takardar shaidar gama babbar sakandare, Bashir ya je hutu a Paraku, ya shaida ma tanti Hawa da Alhaji cewa ya biya musu karatu a Baljik. Don haka Bashir ya yi kwana goma sha uku ya koma don shirye-shiryensu na tafiya. Ashe ni ban sani ba zuwan da Bashir ya yi, soyayya ta shiga tsakaninsu da Riyanatu. Ni dai ina ganin su suna yan wasanninsu. A kullum

sai na bar su na je na kwanta ni a ganina don Riyanatu tana tab-
bashiyarshi ne suke yan wasannun nan.

Ana sauran sati Bashir ya koma Nijar Alhaji ya ce ya shirya ya kai shi Kwatanu babban birnin ƙasar Benin don ya masa sayayya. Bashir ya yi ta roƙon Alhaji don ya bar shi su tafi da Riyanatu sai Alhaji ya amince amma da sharaɗin sai an je tare da ni. Suka yarda muka je tare. Bashir da Riyanatu suka yi hotuna iri-iri a wurare daban-daban cikin Kwatanu balle ma a bakin teku. Duk wannan bai sa na gane ba sai bayan tafiyar Bashir da wata shida.

Wata lahadi da safe ina sharar ɗakinmu, na ɗaga gadon Riyanatu in share sai na ga wata farar takarda a dunƙule na jefa ta cikin shara. Ina kwasar sharar sai na buɗe takardar na ga wasiƙa ce da Bashir ya aiko ma Riyanatu kuma wasiƙar soyayya ce. Farkon rubutun dai na karanta na ga wanda ya aiko wasiƙar. Na aje wasiƙar sai da rana muna cikin lambu muna hira sai na ba ta wasiƙar. Ba ta mini musu ba, ita da kanta ta gaya mini yadda soyayyarsu ta fara. Bashir bai taɓa rubuto mini wasiƙa ba sai dai ya rubuta ma Riyanatu ya ce ta gaida ni. Riyanatu ta yi ta mini dariya. Ta ce mini wani da kaya wani da doro. Tanti Hawa da mijinta sun yi farin ciki. Ya shaida ma Bashir da ko bayan mutu-warshi ne yana da mata a gidanshi. Tun da na koma Paraku bai fi sau biyu ba da nike samun zuwa Yamai. Ko shi ma ni da su tanti da Alhaji da Riyanatu muke zuwa. In har mun daɗe muke sati. Saboda har na mance da Farid domin tun da na tafi ban taɓa samun labarinshi ba.

Kwanci tashi, ni da Riyanatu muna jami'a ina karatun jaridan-ci ita kuma tana karatun koyarwa. A ɓangarensu kuwa Farid na karatun banki, Bashir yana karatun ofisan ɗan sanda, watau kwamsar.

Cikin shekara ɗaya ne ni da Riyanatu muka kammala maka-rantar. Don haka muna shirin zuwa hutu a Yamai. Baban Riyanatu ya hana mu tafiya ya ce mu bari sai ya dawo daga wurin sayen kaya. Muna kwance cikin ɗaki Riyanatu tana mini hirar Bashir sai muka ji ƙarar tanti Hawa.Muka tashi da gudu zuwa falo. Kan mu zo har ta suma. Na watsa mata ruwan sanyi. Ga waya yashe kusanta.

- Farida mi ya same ta ne? inji Riyanatu, ta tambaye ni cikin kuka.



- Ina ji wani mummunan labari aka gaya mata.

Ta yi wani dogon lumfashi.

Riyanatu ta kama mini muka zaunar da ita. Wayar na ta ƙara sai na ɗauka nan da nan na gane muryar mai maganar. Alhaji Salisu ne babban abokin Alhaji mahaifin Riyanatu, yana magana cikin rawan murya.

- Ku kula da uwarku kamin na zo.

Gaba na ya faɗi ras.

- Baba lafiya dai ko?

- To sai dai haƙuri babanku ya rasu cikin hatsarin mota.

- Inna lillahi wa inna ilaihi raji'una.

Na aje wayar na zauna na yi ƙoƙari na yi kuka na rasa hawaye. Tanti Hawa da Riyanatu suke ta kuka balle ma lokacin da su Alhaji Salisu suka shigo ɗauke da jikkar balaguron baban da ya riƙe ni. Haba gidan gaba ɗaya ya rikice da kuka. Nan da nan aka wa babana mahaifi waya, ya zo shi da Alhaji mahaifin Farid. Haka dai muka yi zaman makoki cikin zullumi da bakin cikin rabuwa da shi. Bayan fatiyar kwana arba'in muka tara ya namu ya namu muka dawo gida Nijar tare da jagorancin baba. A Yamai tanti Hawa ta idar da takabarta. Muna zaune cikin ɗaya daga cikin gidaje biyar da yake da su a Yamai. Kullum baba yana kan mu ya na muna nasiha domin ba mu da wani kuzari mun tsinci kanmu kullum cikin tunanin Alhaji. Balle ma ni ba zan taɓa mantawa da shi ba irin riƙon da ya mini ko iyayena ba za su mini shi ba. Alhaji bai taɓa mini faɗa ba. Haka tanti. In ya sawo muna kaya sai na zaɓi waɗanda nake so sa'annan ya ba ɗiyarshi

Riyanatu. Lele iyakar lele ko da yake yana tsare gida ni ba na ganin laifinsu domin ni ban ga abin da na rasa ba. Ko tanti Hawa da ke matarsa bai barin ta ta fita balle mu, ba ta zuwa ko nan da kofar gida, biki ma da dare take zuwa kuma tare da Alhaji ko ya samu mu raka ta. Mu kuma daga makaranta sai gida. Kafin mu tashi daga makaranta yana tsaye yana jiran mu. Ni kam ko a ka ban damu ba amma tanti da Riyanatu kullum zance suke.

Duk abin da muke so yake sayo muna ba mu taɓa zuwa kasuwa ba. Abin da duk muke so sai mu rubuta mashi ya sayo muna. Samari suna son magana da mu amma suna tsoron Alhaji. Babban dalilin shi ne baba ya shaida ma Alhaji da sun yi alƙawali da Alhaji baban Farid: ni za a ba Farid kuma soyayyar Bashir da Riyanatu ya kai ga aure. Daga Bashir ya dawo za a ɗaura musu aure. Ni ban san abin da ake ciki har zuwa wannan lokaci. Wata rana muna zaune wurin aiki cikin ɗakin da aka tanadar wa masu gabatar da labaru, ina shirya labari ni da Isaka wanda za mu gabatar da labarin yau. Ba na jin jikina. Na shaida ma daraktanmu. Ya ce in taya Isaka shirya labarun sannan na tafiyata domin ina fama ne da mura. Muna cikin aiki ne sai ga abokin Isaka, Idris ya shiga ya gaida mu. Isaka ya ba shi kujera ya zauna. Na juyo gare shi na gaida shi. Sai ya yi mini murmushi na sadda kaina ina shirya labarun.

- Yau kam na yi sa'a Isaka, kullum in na zo ba na samun ganin ta na yi mamakin jin abin da ya faɗa.

- Farida wallahi kin iya ba da labaru na zo ne don na baki ƙarfin gwiwa, muna jin daɗin labarunki.

- Na gode.

Ina magana kaina a sunkuye domin murmushinshi ya rikitani.

- Mi ya shaƙe miki murya?

- Wallahi mura nike fama da ita daga nan asibiti za ni.

- Daidai kenan. Ai ba ki sani ba Idris doktar ne. Tashi ya tafi ya samo maki magani.

Nan da nan na ji son Idris ya kama ni. Ya yi ta kama ni da hira kamar mun daɗe da sanin juna. Da na gama taya Isaka sai Idris ya ɗauke ni cikin motarshi zuwa asibitin da yake aiki. Ya mini magani ya maido ni gida. Tun daga lokacin nan soyayya mai ƙarfi ta shiga tsakaninmu. Idris ba ya da isasshen lokacin saboda muƙaminshi na doktar. Amma a kullum sai ya kiraye ni a waya

mun yi hirarmu ta masoya. Ban kai shi gurin iyayena ba domin akwai wani dare da muka yi hira ya mini zancen aure amma sai dai bai ida tara kuɗinshi ba domin na san halin baba yanzu zai ba shi kwanaki uku ya ce ya zo ya yi aure in ba hakanan ba ya shafa mini lafiya. Ni ko ga shi ina son Idris ya aure ni. Kenan doli in jira shi har ya gama tara kuɗinshi. Soyayyarmu da Idris sai ƙara ƙarfi take. Cikin danginsu ba wanda ban sani ba domin yakan kai ni gidansu. Sun karɓe ni da hannun biyu. Balle uwarshi in ba ta gan ni ba sai ta aika ƙannen Idris wurina su ga ko lafiya.

A ma'aikatar su Idris wani baturen ƙasar Japan ya kawo baburra goma, mai so ya ɗauka a riƙa fitar da kuɗin cikin biyanshi har ya zamo nashi. Idris ya ɗaukar mini moto ƙirar D.T. Na yi mamaki domin shi da yake shirin aure, bai ma sa kuɗin ga babban gidan da yake ginawa. Yanzu kam bisan D.T nike zuwa aikina kuma in kai Riyanatu. Da na gaya ma tanti Hawa wanda ya ba ni injin ba ta ce da ni komi ba sai dai ta ce: "Allah ya kiyaye." Idris bai san inda zai sa ni ba don son da yake mini. Haka ni ma, har gidan talabijin ba wanda bai san da soyayyarmu ba.



Bashir da Farid sun yi shekara shida a Baljik. Bashir ya mini waya sati mai zuwa, za su dawo Yamai. Farin ciki wurin mu kar ki so ki gani muka shiga shirye-shiryen tarbon su. Alhaji baban Farid ya gina ma kowa gidan kanshi. Ni da Riyanatu muka gyara masu gidajensu. Kayan ɗaki iri ɗaya Alhaji Kasum ya sa musu

kujerun. Har gadajensu iri ɗaya ne. Riyanatu ta matsu kamar a ce: "Yau subdu ne." Na zo gida ran juma'a domin ni zan gabatar da labarin yamma a gidan talabijin. Ina zaune kusan Inna bisa tabarma ina cin kwaɗon zogala. Baba yana zaune bisa buzunshi yana rubutu ga allo, muna hirar Bashir.

- Baba shekara bakwai rabo na da Bashir.
- Shekara bakwai? Rage dai Farida!
- To baba tun kamin ya je Baljik shekarar da ya samu takardar kammala karatun sakandare ta BAC.
- Yanzu har ya kai shekara bakwai da ya gama sakandare?
- Karya take malam shekara shida ne kawai. Jiya Alhaji Kasum ya ce shekaru shida ne.
- To Inna, ai cikin babban hutu ne ya zo a Paraku.
- Sai ki ƙaryata mu ni da babanki ko?
- Inna ba hakanan ne ba! To ... a bar zancen dai.
- Fushin ne ko? Ka ga halin fulani, saukin fushi. Da ma bafilaccen mutum in shanu sun ƙare sai zafin hassala.

Inna tana faɗi tana dariya, baba dai bai tanka muna ba. Ta janyo ni tana bubbuga ni.

- Haba yar autata kar ki yi fushi mana.
- Yawwa ci ki ƙare kar lokaci ya miki.

Sai muka ga ana ɗaga labulen barandarmu.

- Assalamu alaikum.
- Wa alaikassalamu. Bashir! Bashir!

Ina ta kururuwa na yi tsalle sai ga wuyanshi muka rungumi juna. Ina kukan ƒarin ciki ɗan uwana ya zo. Inna tana jin nauyinshi domin shi ne ɗanta na fari har sunanshi ba ta kamawa tana ce masa bebe. Ta leƙo shi ta koma ta zauna.

- Bar shi ya shigo mana Farida, inji baba.

Na kamo hannunshi sai gaban baba na shimfiɗa mashi tabarma kusan baba suna gaisawa, Inna ta lulluɓe kanta da mayafi. Bashir yana gaida ta amma ba ta kallon shi. Ta ba ni dariya.

- Inna don mi kuke kunyar Bashir? Ai an bar wannan yayin ko?
- To rishin kunya za ki mini?
- Pardon, Inna ku gafarce ni. Bashir kai da ka ce muna gobe za ka zo?

Farid ya tare ni.

- Ai tare muka zo. Alhaji kaɗai ya san da muna dawowa.

Baba ba ku ga irin ƙayataccen gidan da ya gina muna ba. Wallahi baba daga ni har kai ba mu iya biyan Alhaji.

- Da ma mana Bashir, sai dai mu masa fatan Allah ya sa ya gama lafiya. Allah ya taimaka mashi, Allah ya daɗa ƙara mashi arziki.
- Amin baba.
- Farida kawo mashi ruwan wanka, inji Inna.
- Inna tun da safe muka zo, Alhaji ya kai mu masabkinmu.
- Bashir yaya karatun ku?
- Baba alhamdu lillahi mun zo da digirinmu.
- Alhamdu lillahi, Allah na gode ma.

Haka dai muka yi ta hira har wani lokaci. Bashir ya tashi yana zagaye gidan. Na bi shi ya je wurin awaki ya tsugunna.

- Farida ina akuyata?
- Wallahi ban sani ba. Ni ma ban san nawa awaki ba. Abin shekara nawa?!
- Ban tambaye ki ba, yaya aikinki?
- Bashir na gode Allah, yanzu ina aiki ne gidan talabijin. Wallahi Bashir na yi farin ciki da zuwanka. Bari na je na gaya ma Riyanatu don na samu goron albishir. Bashir ya yi dariya ya tashi ya kakkaɓe hannayenshi.
- Tun yanzu?
- Goron albishir ni zan same shi, tun wani bai riga ni ba.
- Ina za ki yanzu?
- Wurin aiki. Ni zan gabatar da labarun yau. Lafiya?
- Da na so in aike ki wurin Farid.
- Farid, wane ne Farid?

Ya harare ni.

- Farid za ki cewa ba ki sani ba? Kai ɗan Adam! Amma Farida kin ban mamaki. Farid ɗan Alhaji abokin baba?
- Yanzu na gane shi.
- To sauran ya zo ki ce ba ki san shi ba.
- Da ma fa Bashir yaushe rabona da shi. Tun ina da shekara goma, yanzu ina da shekara ashirin da biyu. Don Allah Bashir ba ka je gidan tanti ba?
- Ban je ba kin dame ni. Na so ne ki je ki ce mashi mu gamu a filin jirgi don mu amso kayanmu ne.
- Ban ji daɗi ba domin lokacin ya ƙure wurin aiki za ni. Na je na ɗauko jikkata da yake ƙanen Idris ya zo ya ari injina. Sai na ɗauki

taksi na koma gida. Na iske tanti Hawa ta dawo daga balaguro domin kasuwanci take yi.

- A ce dai lafiya! Farida lafiya? Na faɗa bisan ta.
- Tanti Bashir ya zo. Na baro shi gida.

Tanti, har da rawa ta yi don farin ciki.

- Ina Riyanatu take?
- Yanzu ta shiga wanka.

Na shiga cikin ɗakinmu sai ta rungume ni.

- Wallahi na ji labarin da kika faɗi. Ban yi wanka ba, na zuba ruwan ne na fito.

Ta tashi tsaye tana ta dariya.

- To sa rigarki ki raka ni in ɗauki taksi, lokaci ya mini.
- Za ki samun taksi yanzu?
- Farida ba ki sha madararki ba.

Tanti ta shigo ɗauke da kwap a hannu tana ƙoƙarin haɗa mini madara.

- Kai, tanti, ai da na mance.
- Allah ya sa gwamnati ya kai ki cikin ƙaramin ƙauye inda ba a samun nono.
- Ai cikin Nijar ba ƙauyen da ba a samun nono. Muka fita daga cikin gidan muka yi minti biyar ba taksi sai Riyanatu ta ce mu bar tsayawa wuri ɗaya, mu rika tafiya. Muna cikin tafiyar sai na tuno da ina da wani littafi wanda Salmu Hasan ta wallafa mai suna "mai haƙuri yakan dafa dutsi."
- Kin san ta Riyanatu?
- Ina jin sunanta. Na ji ana yaba ta wurin rubuta littafin dandalin soyyaya na Hausa.
- Wallahi Riyanatu ki yi ƙoƙari ki karanta littafin nan. Abin tausayi in kin karanta shi ko ba kya so sai kin yi hawaye. Ina da shi ma, bari na fito da shi ki gani.

A daidai lokacin nan wani ɗan taksi ya muna oda. Yana wancan shiyyar ne. Kenan sai mun ƙetare kwalta zuwa wurinshi. Duk na mance ko bisa hanya muke. Mun kai tsakar kwalta sai na sa hannu cikin jikkata don na fito da littafin. Ban ji komi ba sai na gane ni kwance ƙarƙashin mota. Ashe Farid ne ya kaɗe ni da motarshi, bai gane ni ba. Balle Riyanatu da sai a hoto yake ganin ta. Ya kamata a ce ya gane Riyanatu amma da hankalinshi ya tashi bai ma san abin da yake ciki ba. Riyanatu ta kama mashi

suka kai ni asibiti. Ban san abin da ake ciki ba. Bayan awa uku likitoci suka fita da ni daga cikin ɗakin magani. Farid ya tarye mu ina kwance bisa ɗan gadon asibiti, duk jikina an lulluɓe shi da bandeji.



- Dokta, dokta mi ya ... mi ya ... ina ... ina...?

Dokta ya dafa kafaɗarshi.

- Kwantar da hankalinka ta samu kariya a hannunta na dama da gwarjewa da ta yi a kanta da ƙafafuwanta.

Farid ya dafe kai, ya tsuguna. Dokta ya ta da shi yana bin mu baya sai ɗakin da za a kwantar da ni. Daki mai lamba goma sha biyar. Ina ta shara barci, dokta ya shaida musu da kar su ta da ni domin an mini allurar barci. Riyanatu ta zauna a bakin gadon da nike kwance tana kallo na tana kuka. Farid ya jingina ga bango. Tausayinmu ya mamaye shi.

- Yan mata ƙanwarki ce?
- Diyar ƙanen uwata ce.
- To ba haka ba, amshi kuɗin taksi ki tafi ki gaya ma mutanen gida.

Ya sa hannu a aljihu ya fito da jikka.

Riyanatu ta karɓi kuɗin sai gida. Daga shigarta tanti Hawa ta fara mata faɗa.

- Ina kika tafi ne tun ƙarfe uku kika fita daga gidan nan. Tuno fa da abin da babanki ya gaya miki kamin ya rasu.

- To Inna ba ku bari ma na yi nawa bayani. Mota ta kaɗe Farida tana asibiti, lambar ƙofar ɗakinta goma sha biyar. Zan koma wurinta. Ku tafi ku gaya ma su tanti.

Tanti Hawa ta iske, gidan kowa hankalinshi a tashe. Baba yana ta zuwa da dawowa, inna tana tsugunne. Da tanti ta yi sallama Bashir kaɗai ya amsa. Bashir ne ke magana a lokacin da tanti ta shigo:

- Baba, yanzu daga gidan su Farid nake. Na je ne, tunda shi yana da mota ya ɗauko mu tafi neman su tare. Shi kuma an ce ya fita tun wajen ƙarfe uku ya ce wai za ya wurina. Abin mamaki Farida ba ta ma je wurin aikinta ba.

- Na samu labarinsu, mota ta kaɗe Farida suna asibiti. Kaltumi mu tafi wurinsu.

- Ki ce mini ta mutu! wayyo! wayyo ni kaina!

- To lafiya Kaltumi? Wannan haukan ba a gidana ba! In ta mutu, ke kika ba kanki ita? Ba Allah ya ba ki ita ba? Kar ki zama jahila mana. Hawa yaya take ne?

- Ta samu kariya a hannunta na dama sai gwaljewa da ta yi a sassa daban-daban na jikinta.

Da Tanti Hawa da Inna da Bashir suka ɗauki taksi sai asibiti. Kan su zo Farid ya koma gida ya ba Riyanatu jikka biyu da rabi, in na falka ta sayo mini abinci. Da suka zo suka tarar da ni ina ta sharar barci. Bashir ya tambayi Riyanatu wane mai mota ya kaɗe ni? Tace ba ta sani ba.

- Kina lafiya kuwa? Yaya za ki ce mini ba ki san wanda ya kaɗe ta ba alhali ko gabanki aka yi hatsarin.

- Kai ka bar mata faɗa kana zaro mata idanu, mine ne haka? inji Inna tana ma Bashir faɗa.

- To Inna ba gabanta aka yi abin ba. Ta ɗauki ko limaran motar mana. To in mai motar ya ƙi dawowa fa?

- Kai ba na son rishin kunya ka ji ko? Kama mini bakinka to!

- Ke Kaltumi gaskiyar ki. Riyanatu kamar wadda ba ta yi karatu ba, inji tanti tana gyara mini kwanciya.

Wajen ƙarfe takwas na safe na farka daga barci. Na buɗe idanuna; na rika jin tsoro sai daga baya hankalina ya dawo. Na fara tunanin abin da ya faru gare ni. Bashir ya taso ya zo wurina.

- Farida ina kwana?

- Lafiya lau Bashir.

- Ina yake miki ciwo?

- Duk jikina, Bashir.

- To bari na je na kirayo dokta. Ya ce in kin falka in shaida mashi.

Har Bashir zai kama ƙofar sai Farid ya turo ta duk mamaki ya kama su.

- Bashir mi ka zo yi nan?

- Kai zan tambaya ina ka samu labari?

- Kai ya kamata in gaya maka.

Riyanatu ta juya wajen su.

- Ai Bashir wannan shi ne ya kaɗe Farida.

Gaban Farid ya faɗi. Bashir bai san abin da zai faɗi ba.

- Farida? Farida ka ce fa!

- Farida mana, ga ta can kwance.

- Farida na kaɗe? Ya zauna a gigice, ya dafe kai. Bashir ya ta da shi.

- Wallahi ban ... ban ...

Sai ga su Inna da tanti Hawa. Su Bashir suka ja daga baya suka gaida su. Bashir ya shaida musu da Farid ya kaɗe ni. Yan jarida suka yi ta zuwa gani na. Dakin har ya musu kaɗan. Idris da yan uwansu suka yi ta zowa gani na. Idris ya yi ta hidima a kaina, abin har yana ba dangina mamaki.

Bayan sati ɗaya na fara jin sauƙi domin Idris ya kawo wani mutum ya mini ɗorin gargajiya. Ina zaune bisa gadona. Na jingina ga bango, Idris yana zaune muna hira. Bashir da Farid suka shigo suka gaida ni. Har zuwa yanzu ban gama ido da Farid ba. Idris ya ɗauko nono ya zuba mini cikin kwap. Ya miƙa mini na karɓa na sha. Bashir da Farid duk suka yi sanyi ganin yadda Idris yake kula da ni.

- Farida yanzu kam kin ji sauƙi ko?

Na waiwaya, muka gama ido da Farid. Ya mini murmushi na kauda kaina. Haushinshi na ji domin shi ya kawo ni kwanciya a asibiti.

- Yaya, an sallami Farida, inji Idris. Ga takardunta. Kamin hannun ya ɗoru, sai in rika zuwa gida ina sauya mata bandeji.

Farid ya murtuƙe fuska yana jin haushin Idris, kamar ya shaƙe shi, don kishi.

- To mu tafi, mu fita tare ko?

Farid da Bashir suna gaba da kayana ni da Idris muna bin su baya muna takawa ɗaya-ɗaya muna hira. Idris ya buɗe mini ƙofar motarshi. Farid ya buɗe mini tashi. Ni ban san abin da ake ciki ba domin ni na ɗauki Farid tamkar yayana. Kuma shi da Bashir duk ɗaya ne wurina. Ina kiranshi "grand frère" ma'ana yaya.

- Yaya ku bari na shiga motar Idris.

Ban tsaya jiran amsarsu ba, na shiga motar Idris muka nufi gidan tanti Hawa. Tanti Hawa ta tarye mu domin mun rigai su Bashir. Muna zaune cikin falo sai ga su Bashir, Farid yana tafiya kamar wanda babu lakka a jikinshi. Ya zauna gabana, ya tsare ni da kallo sai na riƙa jin tsoro. Tunanin yarintarmu ya riƙa zo mini. Yanda Farid yake tsare ni da kallo yana tsawata mini sai na iya darasi, ko za mu kwana a nan ne. Akwai wani dare da na gaza hardace karatu, da na fara sai ya kubce mini. Bashir na kallon mu. Farid yashiga matsa mani, dole sai na iya karatun.

- Ke! renin ya ishe ni haka nan kin ji! Yau sai mun kwana a nan. A kan darasi ɗaya za ki ɓata awa huɗu. Ragguwa!

Yana mini faɗa yana zaro mini idanu; ya yi jifa da littafina har sai da ya rabu biyu. Na fashe da kuka. Na tashi zan je daukar littafin, ya buga mani tsawa.

- Ke dawo ki zauna. Ba kya ji ko?

Ya tashi ya jayo ni da ƙarfi, ina kuka domin na san halin malamarmu, in har ta gan ni da littafi cirarre. Na dawo wurina na ƙi karatu. Ya yi ya ya yi da ni, na ƙiya ya tashi ya fito. Jim kaɗan ya dawo da tsuma biyu na dalbejiya.

- Ki karanta na ce! Da ke nike!

Na yi banza da shi ya fara kishina da tsumar. Bashir yana zaune yana kallon mu. Bai ce da shi uffan ba sai da tsumungun suka kaririye. Sannan ya daina ba ni kashi. Ina ta kuka jikina duk ya gwalje. Ya zauna yana ta huci. Bashir ya tashi ya ɗauki buta har ya dawo ban bar kuka ba.

- Farida ba ki raba mutane da kuka ko? Farid ko gobe in ta ƙi karatu ka ba ta kashi. Ba ka ma ba ta kashi ba. In ta sha kashi ko an ce ta yi kuka ba ta yi. Yanzu na ba ki kashin da ya fi na Farid.

Ya aje butar ya nufo ni. Sai Farid ya tarye shi. Nan da nan na fara haɓo. Jini na fitowa daga cikin hancina. Tausayina ya kama su, suka yi ta zuba mini ruwa bisa kaina suna ɗaga mini fuska.

Da jini ya tsaya ba su yi barci ba sai da suka sake mini littafi. To tun ranar na fara jin tsoron Farid. Daga ya shigo gidanmu sai na tashi tun bai sani ba har ya gane da ina jin tsoron shi. Ya yi, ya yi da ni, in bar tsoronshi. Amma, ban bar tsoron nashi ba har Tanti Hawa ta zo ta tafi da ni.

Farid ya katse mini wannan tunanin na da wanda na shiga ciki.

- Farida tunanin mi kike ne?

Na sunkuyar da kaina. Idris ya yi sallama da mu ya fita. Na tashi na shiga ɗakinmu. Na bar su suna hirar Auren Riyanatu da Bashir.

Kwana biyu zuwa kwana biyu Idris yana zuwa don ya sake mini bandeji ko ya aiko wani. Yau Idris ya zo da kanshi yana tsakar sake mini bandeji sai ga su Bashir da Riyanatu da Farid. Riyanatu ta kawo musu ruwan sha. Na gaida su cikin ladabi.

- Sannunku!
- Sai kin ga dama za ki gaida mu ko? inji Bashir.
- Ba ta kyauta ba yaya, inji Idris.

Na harari Idris, yana dariya yana mini gwalo. Fitar Idris ke da wuya suka mini kya da faɗa kowa na faɗin ta bakinshi. Suna ta zagin Idris. Wai ba faɗan da suke mini ke sa ni kuka ba. A'a ɓaci, da zagin da suke ga masoyina Idris. Ina tambayar kaina don mi suke zagin Idirs. Ni dai ban ga laifin da ya musu ba.

Bayan sati uku na murmuje kamar ban taɓa samun hatsari ba. Har na fara zuwa wurin aiki ni da Idris kullum sai mun ma juna waya. Auren su Bashir yana sauran kwana biyar, ina shirin zuwa gida bayan na ba da labaru, sai Aishatu wata yar jarida ta zo wurina.

- Farida ana neman ki. Wani ɗan gayi ne wallahi kin yi sa'ar samari. Da a ce ni ce da kun ga ɗaukar kai. Son kowa ƙin wanda ya rasa.

Ni a zatona Idris ne.

- Idris ne ba ki sani ba?
- Ba shi ba ne. Wannan ya fi Idris kyawon halitta. Mamaki ya kama ni.
- Ba Idris ne ba? To wane ne?
- Ya ce a ce miki Farid ne.
- To, Farid ne? Ai yayana ne, kuma abokin Bashir ne.
- Amma Farida a ganina Farid ya fi Idris in zaɓe za ki yi.

- To! Aishatu ba ki ji Farid yayana ne?
Na iske Farid zaune bisa motarshi ƙirar marsandi masara.
- Salamu alaikum!
- Wa alaikumus salam. Farida, kin sauka ko? To mu je in kai ki gida.
- Na gode Farid. Ba gida za ni ba. Za ni rabon katunan gayyatar Auren su Bashir ne.
- Daidai kenan. Taho in kai ki.
- Na gode yaya. Ku tafi, domin ba wuri ɗaya ba za ni ba kuma taksi zan ɗauka.
Duk maganar da muke, kaina a sunkuye saboda ina jin kunyar Farid.
- Ga dawo an ce "yunwa". Ga ni da mota za ki ce ki shiga taksi. Kina tsoron kar dokta ya gan ki cikin motata ko?
Ya buɗe mini ƙofar motarshi na dai shiga ba don da sona ba; ya kai ni duk guraren da ya kamata in kai katunan. Yana ta mini tambayoyi don ya samu ya sa ni hira. Ran auren mun sha shagali.
Bayan sati da auren su Bashir, Farid ya gayyaci amaren a otel su ci abinci. Farid ya mini waya ya sanar da ni. Na ce mashi ba zan je ba. Ya yi, ya yi da ni ban amince ba. To "da walakin" goro a cikin miya. Farid yake roƙo na kamar yaro ƙarami. Ina kwance cikin ɗaki domin yanzu ɗaki ya zamo nawa tun auren Riyanatu.
Riyanatu ta shigo.
- Wane irin ƙauyanci ne wannan, ba kya sallama?
- Miji gare ki cikin ɗaki ko mi? Ni ba na sallama in za ni shiga ɗakin gwabruwa.
- Na ji, mu ma auren sai mun yi shi.
- Allah ya sa a yi da mu. Farid dai ya matsu.
Gabana ya faɗi. Na tashi zaune.
- Wai mi kike tun ɗazu kun sa ba mu yi girki ba. Ke, tashi ki shirya.
- Riyanatu? Na kamo hannunta. Ban ji abin da kika faɗi ba!
- To! Ba ki ce mini ba ki san abin da ake ciki ba, haba. Ai ba yarinya kike ba. Yanzu abin da Farid yake miki baki ce mini ba ki gane ba. Idanuna suka cika da hawaye. Kuka za ki yi? Ai tuni su baba sun aje zancen. Sai ga Bashir ya turo ƙofar.
- Kai ba jiranku muke ba? Farida, mi kike jira ne?

- Bashir kaina ke ciwo.
- Tashi shirya, mun kai ki asibiti.
Na tashi na bi su. Suna hira ni ban san ma ko ina tare da su ba. Muka zauna teburi guda, aka kawo muna abinci kala-kala. Farid ya zaƃo muna abinci ni da shi ya aje faranti gabana, na ci. Suna hira. Tun da na kafe idanuna ga farantin da ke gabana ban ɗauke su ba sai da Farid ya mini magana.
- Farida ki ci mana. In har ba ki ci to ni ma ba na ci. Ko na ba ki a baki ne?
- Wallahi Farid ba ka san kunya ba, inji Bashir.
- Don Allah bari na tambaye ka Bashir in an kawo zancen kunya kana da bakin magana kai?
- Ai dai na fi ka, kuma ai so ba hauka ba ne.
- Kai ku ji kai Bashir! Kana so in gaya musu abin da ka yi a Beljik ne?



- Mi na yi? Faɗi mana!
- A bar kaza cikin gashinta.
- Fige ta, maras kunya. Farid ya ƙyale shi ya juyo gareni ya ƙura mini ido na sunkuyar da kai.
- Farida mi yake damunki ne? Kar ki tayar mini da hankali mana.
Haushi kamar na mutu.
- Ka ga, shafa mata lafiya. Tana fama ne da ciwon kai.
- Ai ban sani ba, tashi na kai ki asibiti. Tashi mu tafi, Farid ya tashi ya kama hannuna.

- Na ji sauki.
- Karya take. Tashi ku tafi. Inji Riyanatu tana mini gwalo.
Na tashi na bi shi. Muna cikin tafiya sai ya kashe kaset tana cikin wata wakar soyayya kau. Ya juyo gare ni ina ta kuka don bakin ciki.
- Farida ciwon kan ke sa ki kuka? Bari yanzu za a shawo kanshi, kin ji!
- Farid kai ni gida.
- Bari sai mun fito daga asibiti.
- To aje ni nan.
Ya yi banza da ni.
- Ka aje ni nan don Allah.
Ina kokarin budе kofar sai ya jayo ni har motar ta saki hanyar. Da kyar ya samu ya tsai da motar. A zatona kashi zai ba ni domin na so in sa shi hatsari. Sannu-sannu ya hauda motar bisa hanyar. Bai ce da ni komi ba sai gida. Na fita sai cikin dakina na fada bisa gado ina ta kuka tunanin Idris ya zo mini. Tausayinshi ya kama ni. Shi kenan ni da shi domin in har baba ya sa baki to shi kenan. Juyawar da nike sai na bugi Farid na yi sauri na tashi. Ashe ya biyo ni ni ban sani ba duk kukan da nake yana zaune.
- Farida na san na yi kuskure domin ban bayyana miki asirin zuciyata ba tun shekarun baya. Farida wallahi, wallahi ina son ki. Yanzu haka na fi son ki da kaina. Na san zai yi wuya domin na iske ki da wani amma in kin ba ni hadin kanki za ki manta da shi.
- Ba zan taba ba ka hadin kai ba domin ba ni iya cin amanar Idris irin yadda yake kashe kanshi saboda ni. Haba, sa kanka a wurinshi mana.
- Farida, ki ceci rayuwata mana. Son ki ya mamaye birnin zuciyata, wallahi zan rike amana, ba za ki taba "da na sani" da aure na ba.
Tanti Hawa ta kwala mini kira. Na tashi na je wurinta. Ta sa ni wankin magewayarta. Ba ta san cewa muna tare ne da Farid ba. Da na ida, tanti ta ce mini baba na son ganina gobe da safe. Na ishe baba yana karatun Kur'ani. Na zauna sai da ya ida muka shafa fatiya.
- Ina kwananku baba?
- Alhamdu lillahi. Kaka na gan ki haka? Ba kamar kullum ba, in kin zo nan kina fara'a, yau sai tagumi?
- Ba ni da lafiya ne baba.

Na boye gaskiyar jiya da dare ban rufe ido ba barci ya gagare ni kwana na yi ina kuka. Kuma na san dalilin kiran da ya mini.
- Allah ya saukake.
- Amin baba.
- Farida, Allah ya miki albarka, Allah ya taimaka miki, Allah ya kara daukaka ki, Allah ya sa ki gama lafiya. Na gode ma Allah da ya ba ni diya kamar ki. Domin da wuya a samu diya irin ki balle ma cikin zamanin ga da mu ke ciki. Farida kullum na yi salla ina ta sa miki albarka.
- Na gode baba Allah ya kara muku tsawon rai don ku yi ta sa muna albarka.
- Farida na san zabina shi ne sabinki. Na san da ba za ki taba ba ni kunya ba a rayuwata. Kuma Farida ki san da sani abin da babba ya hango yaro ko ya hau tudu bai hango shi. Farida son da nake miki ba zan taba zabo miki abin da zai rushe miki rayuwa ba don haka kin san matsayin da Alhaji Kasum ke da shi a wurinmu. Alherin da ya muna zan ce kin fi ni sanin shi. Tun ranar da kika zo duniya muka ba junanmu alkawali. Shi ya ba da sunan da kike da shi. Ya ce muna ke za ki zama matar danshi Farid. Ga dai uwarki shaida. Kuma gaban Alhaji mijin Hawa aka yi. Na amince. To ga ranar cika alkawali, Allah ya kawo ta. Yan karin magana sun ce kyan alkawali cikawa kuma alkawali kaya, in an cika an sabke. Ko ba haka ba Kaltumi?
- Haka ne malam.
- Yanzu ke nake saurare.
Kaina ya yamutse. Hankalina ya gushe daga gare ni, duniyar ta fita daga raina. Wace amsar zan ba baba? Shi dai bai san da soyayyarmu da Idris ba. In amince da bukatar baba in ci amanar Idris? To in na amince da bukatar baba ai ba na son Farid. In na guje ma baba, mi zan zama domin namiji bai da amana. A zo rana tsaka Idris ya wulakanta ni. Ina za ni? Wata zuciyar na zuga ni, in guje ma baba, wata zuciyar na ce mini in bi bukatarshi komi ya same ni shi ya zabo mini. Don dai shi ba zai yarda ya zaba mani abin da zai cuce ni ba.
- Farida ba ki ce da ni komi ba.
- To baba ai ban isa na ki bukatar ku ba.
Baba ya yi farin ciki ya yi ta sa mini albarka. Na koma gida na ma Idris waya. Cikin minti ashirin sai ga shi gidan mu mun

koma ƙalƙashin iccen mangwaro da ke cikin gidan. Na kwashe labarin duk na gaya ma Idris. Hawaye suka riƙa kwararowa daga idanunshi kamar yadda nike kuka tun jiya.

- Farida shikenan na rasa ki? Kin san abin da za mu yi? Kan a yi bikin zan nemi a tada ni daga garin sai mu gudu tare.

- Idris, ina son ka fiye da kaina, amma ba zan iya gudu da kai ba. Mu tafi mu yi zaman shashanci ko? Kuma auren da ba iyaye ciki ko mun yi shi rushewa zai yi. Mu haƙura mu bar ma Allah zaɓi Idris. Ina tsoron fushin iyayena.

- To ina da shawara. Ki yarda in sa miki ciki kan a yi aurenku. In mijinki ya san da cikin ba nashi ba ne sai ya rabu da ke kin ga sai mu samu damar yin aurenmu.

- Allah ya Kiyaye yanzu shawararka kenan? Ni musulma ce. Kai ma ɗan musulmi ne. Allah ya raba ni da cikin banza.

- To na ba ki zaɓi gobe ki ba ni amsa. Na tafi sai da safe.

Maganar da ya yi ta razana ni ƙwarai kenan Idris don shashanci yake so na. Allah sarki. Allah ka mini zaɓi mafi alheri. Cikin dare na kwana nafila ina roƙon Allah ya mini zaɓi mafi alheri. Washe gari ina wurin aiki Idris ya zo ya ɗauke ni sai gidan abokinshi. A zatona zancenmu na jiya za mu tattauna a kai ya shiga cikin ɗaki ya bar ni zaune cikin falo. Jim kaɗan ya ƙwala mini kira. Na tashi na tafi wurinshi yana kwance bisa gado daga shi sai ɗan kaliso, har na hirgita. Ya tashi ya rufe ƙofar ɗakin. Mi zan gani? Ya jayo ni gare shi. Na fizge shi yaya zan yi da raina Allah ka kubtar da ni.

- Na ɗauki aniyar sai na kwanta da ke. Dama ba son arziki nake miki ba.

Sai daga baya na san da giya ya sha. Na ture shi, ya faɗi bisa gado, na buɗe ƙofar ɗakin zan fita sai ya kamo ni. Na ture shi. Ashe ƙofar falo ya kulle. Na rasa ganin makullai ya nuho ni, ina baya-baya yana bi na kujera ta kaɗe ni na faɗi. Yana tsaye kaina idanunshi sun koma kamar garwashin wuta.

- Ba ki amince da shawarata ba ko? Ki yarda na miki ciki! Tashi ki zo mu koma ɗaki.

- Idris ka wa Allah ka bar ni na koma gida, Idris ka mini afuwa.

- Kenan in na gane ba kya so na ko? Son ƙarya kike mini ko?


- Wallahi Idris ina son ka amma ba na iya ...

Kan na ƙare magana tuni ya tallabo ni, na sulluɓe mashi kokowa ta shiga tsakanin mu. Sai Allah ya taimaka mini na kada shi.

Ashe bai fidda makullan daga ƙofar ba. Hankalina ya tashi na ture ƙofar bai ma kulbe ta ba. Na fita da gudu na baro takalmina da jikkar hannunna. Na tsai da taksi na roƙe shi ya kai ni gida sai an je in biya. Bai yi gardama ba ya kai ni na kuma yi sa'a tanti Hawa ba ta nan da na sha tambaya. Ina kwance cikin ɗakina tunanin abin da ya faru tsakanina da Idris ya yi ta kai kawo gabana.

- Da na yarda da Idris da ya kai ni ya baro. Kuma ko aure na yi ba ni da muntunci a idon mijina sai ya ɗauke ni kamar karuwa sannan ga laifi na tsakanina da ubangiji. A! Maza! Haka kawai na bar ƙaton banza ya yaudare ni in yi biyu babu, in rabu da mijina ya kuma ƙi aure na. Maza akwai yaudara. Allah ya tsare kowace ɗiya mace da sharrin maza. Ashe haka suke ma mata su kai su baro. Ashe Idris ba son arziki yake mini ba ...

- Lafiya? Tunanin mi kike haka ne da zai hana ki jin kiran da nake miki?



- Ban ji ba ne tanti Hawa. Tunanin irin zaman da za ni yi da Farid nike tanti Hawa. Ba na son Farid. Na yarda ne domin ina tsoron in saɓa ma baba ne. Kun san fushinshi ba zai haifar mani da alheri ba.

Na yi tsaki hawaye suka cika mini idanu. Tanti Hawa ta zauna dap da ni, ta kwantar da ni bisan cinyarta tana shafar mini hawaye da ce kwararowa daga idanuna.

- Farida ba na son na gan ki kin shiga hali na damuwa. Ba komi, daure ki so shi domin Farid kam yana son ki kamar ya mutu. Wallahi jiya da kika ce ba kya son shi har kuka ya ɾiƙa muna kuma gaban iyayenshi. Abin da ban tausayi babanki ya ce a kirayo ki domin ya tambaye ki kika ce kin amince. Haba Farida ki ji tausayinshi mana.

- Tanti Hawa ... abin ne ya fi ƙarfina, kawai dai ba na son shi.

- Abin da ba na so in ji kenan.

Haka dai tanti Hawa ta yi ta rarrashi na sai da ta shayo kai na na amince. Sau uku ana ɗaga ranar aurenmu domin da zaran an aje ranar sai in kamu da rishin lafiya. Sai da baba ya yanke shawarar a ɗaura auren ko zan bar duniyar ne ranar.

Ran wata alhamashi aka ɗaura aurena da Farid. A kwana na uku ban san abin da na ke ciki ba domin kullum safiyar Allah sai an sa mini serom saboda zazzaƃi da ciwon kai. Ni ma ban san dalilin rishin lafiyata ba. A kwana na biyar na fara jin sauƙi. Da ma baba ya ƙayyade kwana bakwai zaman amarcinmu, kamar yanda musulunci ya ce a yi. Hankalin Farid ya yi mummunar tashi. Don ko abinci sai su Bashir sun matsa mini in ci.

Rishin lafiyata ta sa ba a yi wani abin a zo a gani ba ga aurenmu. A rana ta bakwai na zo gida a mini kitso kamar yadda ake yi a a'aldarmu. Da daren ya yi aka maido ni gidan Farid wani babban gida. Tanti Hawa da abukkanta suka shirya gidan tsap abin gwanin ban sha'awa. Bayan da yan rakiyarmu suka watse ina kwance bisa gadona, na dibi agogon da ke aje bisa kwaba. Ƙarfe goma sha ɗaya da rabi na dare na tashi na yi wanka na yi alwalla na shiga salla nafila. Domin kamar yanda baba ya koya muna kullum daren Allah, in har za mu shiga barci, sai mu yi nafila. Na yi raka'a goma sha uku na zauna ina jan tazbi sai na ji sallama, an turo ƙofar ɗakina. Na waiwayo tare da amsar sallamar. Sai muka yi ido huɗu da Farid yana sanye da rigar barci da gajeren wando mai tsayawa ga gwiwarshi. Bai sa tankiyon rigarshi ba yana shartar gashin kanshi da alama daga wanka ya fito. Ya tsuguno-uku ya yi dariya ya tashi ya sa tankiyon rigarshi. Ya je ya kwanta bisa gadona.

- Amarya ina wuni? Ba ki amsa mini? Ko ban biya kuɗin sayen baki ba ne?


- An bar yayin sayen baki. Zancen da ne wannan. Kar a ce sai yanzu kike sallar isha? A gidana ba a wasa da salla fa. Gyara darduma mu yi salla.

- Ai na yi.

Ya harare ni, ya dungure ni cikin wasa yana dariya.

- Kar ki ce mini ba ki san cewa ana salla raka'a biyu ba ta ango da amarya zo, zo.

Ya jayo ni. Farid ya shiga gaba muka yi sallar. A zatona Farid bai san karatun alƙur'ani ba. Sai da ya fara jan ayoyi, ya ɗauko alkur'aninshi ya fara mini wa'azi bisa dokokin aure. Wa'azi ya ratsa ni na ɾiƙa jin tsoro har da kuka na yi lokacin da yake faɗar hakin namiji a kan matarshi domin in ba da wa'azin da na ji ba da ba shakka wuta zan shiga in na mutu domin na shirya mai azaba da makirci wanda sai ya yi "da na sani" da aurena. Na yi tagumi kaina a sunkuye hawaye na ta zubo mini. Ya dibi agogonshi: ƙarfe goma sha biyu da minti uku. Ya rufe wa'azin da addu'a.



- Farida wa'azin ya razana ki haka? Alhamdu lillahi haka ake so. Duk musulmi, ya kamata in ana wa'azi ya natsu ya ɾiƙa jin tsoron Allah.

Ya ɗaga kaina ya janye hannuna wanda nike tagumi da shi, ya shafe mini hawaye. Jikina ba lakka, duk ya mutu. Ba ni da wani kuzari, ya ɗauke ni ya rungume ni kamar uwa da yarta ya kai ni bisa gado.

Ya tallabo kaina yana kiran sunana a hankali:

- Farida, Farida, Farida.

Da na yi zaton mafalki ne nike sai na ji an sumbace ni bisa goshina sai na buɗe idanuna muka yi ido huɗu da Farid yana mini murmushi.

- Za ni masallaci, ki tashi ki yi salla.

Ya tashi ya fita. Na yi ƙoƙari na tashi, tashi ya gagare ni duk jikina ba inda bai mini ciwo kamar an saɓe ni cikin turmi. Na dibi agogo lokacin ya nuna ƙarfe shida da minti ashirin. Da kyar na samu na jingina ga kan gado. Na kafe idanuna a kan wani hotona ni da Farid wanda aka yi ana sauran kwana uku a ɗaura muna aure shi ko Bashir ya matsa mini muka ɗauki hoton. Farid ya shigo dardumarshi ta salla a maƙale cikin hammatarshi, ya nufo ni.

- Farida kar a ce ba ki yi salla ba?

Na fashe da kuka ya yi jifa da dardumar shi ya hau bisa gadona ya rungume ni.

- Farida bari kuka mana. Ya kamata a ce kina farin ciki, kar ki maida farin cikinmu baƙin ciki mana. Farida Allah ya miki albarka, Allah ya rufa miki asiri domin ban yi zaton haka ba. A ce budurwa kamar ki ... Amma na yi farin ciki. Allah na gode ma kai da ka zaɓo mini mata yar mutunci. Tashi na taimaka miki ki yi wanka.

A taƙaice dai, a ranar shi ya mini wanka. Kuma ya mini kyautar yan kunnai da sarƙa kala biyu na zinariya da kuɗi jikka ɗari. Farid bai son abin da zai ɓata mini rai ko tagumi na yi in ina kallon talabijin sai ya tambaye ni abin da yake damuna. Farid shi ke kai ni wurin aiki ya maido ni, komin dare sai ya tsaya jira na kamar ni kaɗai ce cikin duniya. Domin a ganina ba abin da zai dagula mini rayuwa. Komi da sauƙi yake zo mini. Ga ni da aiki, ga kuɗi, uwa uba ga miji, domin Farid ya fi so na da kanshi kayan jikina ma wata rana Farid ke wanke su. Haka muke tafiyar da zaman aurenmu cikin jin daɗi da lumana duk ran da ba mu zuwa aiki sai mun je yawo. Farid ya koya mini hawan doki, ran nan muna zaune muna hira sai ya ce mini.

- Farida kin iya mota amma tsoro yake hana ki ɗaukar ta. Mutuwa kike tsoro ko?

- Ai, ko na ji tsoron mutuwa, sai na ɗana.

Ya jefo mini makullan motarshi.

- Tashi ki raka ni wani waje. Ɗauki motar mu gani ko kin gwanance.

Muka je filin sukuwa inda ake kiwon dawakai. Na yi mamaki zuwanmu wurin sai wani ya shiga gabanmu na bi su baya sai wurin dawakai.

- Farida sai ki zaɓi cikin su, sukuwa za mu yi da ke.


- Farid kana son na mutu ne? Ni da ban taɓa hawan doki ba? Ya yi dariya.

- Na zo ne na koya miki.

Na nuna wani farin doki.

Farid ya koya mini yadda ake hawa. Ya shiga gaba yana jan dokin ina riƙe da linzamin. A shigarmu ta biyu ni da Farid har yar sukuwa muke yi. Farid ya koya mini ƙwallon teburi. Kowane marece wajen ƙarfe shida muke zuwa filin ƙwallo inda ake wasanni iri-iri. Nan muka gamu da Zainabu da mijinta Ali. Har Ali da Farid suka ƙulla abutta. Haka ni ma da Zainabu. Ni da Zainabu muke takara da su Farid da Ali. Duk ran da muka wuce su da yawon ƙwallo to sai mu yi ta musu dariya da gwallo. Farid bai tanka muna amma Ali sai ya biye muna mu yi ta surutai. Ali dai tare suka yi makaranta da su Bashir yanzu haka Bashir ne babbansu a ma'aikatarsu ta yan sanda.

Akwai wata rana da misalin ƙarfe uku na marece, ni da Farid muna kallon bidiyo an nuna wata mace cikin teku tana neman waɗansu itace. Sai na kada baki na ce ma Farid: "Wallahi ni ko cikin isa ne sai an rufe mini idanu domin ruwa suna ba ni tsoro." Da muka ida kallon bidiyo sai Farid ya ɗauke ni sai isa ya yi hayar kwalo-kwalo ya yi ta yawo da ni bisa ruwa. Da fari na kama shi



ƙanƙan don tsoro. In kwalo-kwalon ya girgiza sai na yi ƙara. Har ya kai inda na sake shi na zauna daidai har da wasa da ruwa. Duk muka jiƙe garin wasa da dariya.

Aurenmu na da wata shida na fara samun damuwa ta ɓangaren lafiyar jikina. Na tsinci kaina cikin raggwanci da yawan barci. A kullum sai na kwana da zazaɓi da ciwon kai. Ina kwance cikin falo tsakanin kujeru ina neman barci da ƙarfi Farid na zaune yana kwaɗa mini zogala don shi kaɗai ne nike iya ci sai Hajiya uwar Farid da abukkiyar Hajiya Kadi ungozoma suka shigo suna gaisawa da Farid.

- Farid ina Farida ta tafi ne?

- Hajiya, ga ta nan kwance.

- Farida ...? Lafiya?

Na tashi zaune.

- Hajiya wallahi jiya da dare ba mu yi barci ba. Ta kwana amai ban san abin da ta ci ba. Ga yawan barci. Na ce ta je asibiti ta ƙi zuwa. Na rasa shayo kan lamarin. Yanzu ba mu ma hira komi na ce mata sai ta maida shi faɗa ta aza mini kuka. A gaskiya Hajiya na rasa abin da yake damun ta.

Hajiya da kadi suka kalli juna suka yi dariya.

- To Farida tashi mu je asibiti dama daga wurin suna muke. Tashi mana Farida.

Na tashi na bi su sai asibiti, suka ba ni kujera na zauna. Kadi ta fara mini tambayoyi, na sunkuyar da kaina. Ban ba ta amsa ko ɗaya ba ga tambayoyin da take mini. Sai da Hajiya ta gane da saboda tana a wurin ne na kasa magana. Sai ta fita ta bar mu sannan na dinga ba Kadi amsoshin tambayoyinta. Ta ɗauki fitsarina ta shiga wani ɗaki. Bayan minti talatin ta dawo ta fara rubutu bisa waɗansu takardu.

- Hajiya albishirinki!

- Goro fari pas zan ba ki.

- Sai kin ba ni goron albishirin zan ba ki labarin da nake ɗauke da shi.

- Zan ba ki zane uku ɗan Holand. Mi aka yi ne?

- Nan da wata biyar za ki samu miji ko kishiya.

Hajiya ta yi guɗa cikin asibiti, kunya ta lulluɓe ni har gaza tashi na yi. Hajiya da direbanta suka raka ni gida. Takardu suna hannun Hajiya. Ta tsaya cikin falo wurin Farid. Na yi sauri na shiga ɗaki kar ta ba da labarin a gabana don kunyar da nake ji. Na

sauya kayan jikina. Na kwanta bisa gado ina tunanin yaya zan yi randa zan haifu. Labarin da Riyanatu ta ba ni a kan nakuda ya razana ni Farid ya turo ƙofar ɗakina sai da na zabura. Ya hau bisa gado, da gudu yana rawa bisa gadon, saura ƙadan da ya faɗi bisa ni ya tallabo ni ya rungume ni yana ta sumbata ta. Ya ɗauka hannunshi biyu yana ma Allah godiya.

Cikina na da wata bakwai na tuntuɓi Farid a kan zancen zuwana gida shan kunu. Ya game fuska ya ɗauko alƙur'ani ya ce in nemo mashi ayar da aka yi zancen shan kunu. Ya ce mini shan kunu al'ada ce don haka kar ya sake jin na mai zancen shan kunu.

Ina kwance bisa doguwar kujera. Na aje kaina bisa cinyoyin Farid yana wasa da ni na lumshe idanu ina neman yin barci sai muka ji Hajiya ta turo ƙofar, ba ta ma yi sallama ba. Gabana ya faɗi, na tashi zaune. Ba ta ma gaida mu ba sai ta ce:

- Kai yaka nan, amma ba ka san kunya ba! Gare ka aka fara aure? Sannu mai mata. Ina take ne?

Na taso har zan durƙusa na gaida ta.

- Tashi mu je!

Farid ya taso cikin ruɗani.

- Hajiya ai na gaya ma baba malam ya shaida mini da in ta sabka ya turo tanti Hawa ta kula da ita.

- Kai ar! Na rena halinka. Ke wuce mu tafi.

Hajiya ta kai ni gidan tanti Hawa. Washe gari abukkiyarta Hajiya Kadi ta kawo abin da duk ya kamata a kai ma amarya in ta je haifuwar fari. Da misalin ƙarfe tara Farid ya kawo mini lehena. Kullum safe kamin ya je wurin aiki sai ya biyo, haka da marece. Gida yake cin abinci haƙa da daren ma domin tun da na komo gidan tanti ni nike dafa ma Farid abinci, yau Farid bai ma koma gida ba. Da ya ci abincin rana sai ya kwanta bisa kujera ya yi barci. Sai wajen ƙarfe biyu in ta da shi ya yi wanka ya yi salla ya tafi wurin aiki. Har na shirya, na yi shirin shiga gwadala don na ɗora ma Farid abincin dare sai na ji abin da yake cikin cikina kamar yana yawo. Sai da na zauna jim kaɗan marata ta fara mini mugun ciwo. Ina jin fitsari. In na shiga ban ɗaki ba na samun fitsari. Ciwon ya addabe ni. Har zan buga ma Farid waya sai na daure. Tanti Hawa ta je wurin aure tun da safe sai ni kaɗai cikin gidan. Har na fara barci sai na ji leɓɓan Farid bisa goshina yana sumbata ta. Na buɗe ido, ya mini murmushi.

- Sannu. Gajiya ko? Tashi ki ba ni tuwona yinwa nake ji.
- Ban samu na yi girki ba.
- Lafiya?
- Ciwon marar ya dawo har ya fi na ɗazu.

Na kama hannun Farid ƙanƙan. Ya rikice, bai san inda zai kama gare ni ba. Ina ta zufa kamar an zuba mini ruwa. Ina ta nishi.

- Farid zan mutu, wayyo marata, Farid marata.
- Farida ki yi haƙuri. Bar na kai ki asibiti.

Ya ɗauke ni sai asibiti. Da isarmu likitoci mata suka tarye ni. A zaton Farid rishin lafiya ne ya zauna a ƙasa ya gama kai da gwiwa sai wata likita ta fito.

- Malam kai ne Farid?

Ya taso da sauri.

- Ni ne, lafiya?
- Barka matarka ta haifu kawo zane. Farin ciki da mamaki suka hana shi magana.
- Malam da kai nike, matarka Farida ta sauka, ka kawo zane.
- Sai na koma gida Farida ta haifu? Ina zuwa!

Da gudu ya shiga motarshi sai gida ya iske tanti Hawa tana tambayar kanta inda na tafi. Ina kwance bisa gadon asibiti sai wata ungozoma ta kawo mini jaririyar.

- Madam ga abin da aka samu, mace ce. Ɗan gurgusa na kwantar da ita kamin na kawo ɗan gadon ta. Ban tambaye ki ba inda yake miki ciwo ko?
- Ba inda yake mini ciwo. Sai gajiya.

Farid ya shigo ɗauke da kaya, tanti na bin shi baya ya ɗauki ɗiyarshi yana fara'a ya yi addu'o'i irin waɗanda musulunci ya ce ama jariri tun ranar da aka haife shi. Ya tofa ma jaririyar.

A rana ta bakwai Farid ya raɗa ma yarinyar suna Irada. Kusan barci kawai ke kai Farid gida. Da na yi wata biyu a gidan tanti sai aka maida ni gidan Farid. Farid ba ya son abin da ya taɓa mu ni da Irada. Farid kamar shi yake renon, domin cikin dare in Irada ta yi kuka shi yake kula da ita. In fitsari ta yi shi yake rigai ni tashi ya sauya mata kwanci. Saboda yawan aiki na je ƙauyenmu na ɗauko Sadi ɗiyar wata tabbashiyar baba, yar shekara goma sha biyar don ta kula da Irada.

Irada tana da shekara biyu aka ƙara ma Farid girma. Sai bankin nasu ya ba mu wani gida. Haka ya sa muka ƙaura zuwa



sabon gidanmu da yake gidanmu shi ne na ƙarshe cikin jerin gidajen. Hanya ta raba mu da wata unguwa da ake ce ma: "More rayuwarka." To cikin unguwar akwai wata mace da ake ce ma: "La maman watau wai inna uwarmu kenan da hausa." Mijinta ya mutu shekaru da dama da suka wuce. Tana da ɗiya mata su huɗu: Salamatu da, Maimuna da Aishatu da yar autarsu Fatsuma.

Goma ga watan zul hijja, ranar sallar layya, ban je ma'aikata ba. Ina zaune cikin falo ina ma Jamila matar abokin aikin su Farid waya. Sadi da Irada sun shigo, Irada ta nufo ni da gudu ta faɗa bisa ni lokacin da na aje wayar.

- Mama ina baba?
- Yana barci.
- Mama wata tanti ta ba ni mangwaro. Mama ina tuwona?
- Sadi wa ya ba ta mangwaro?
- Yan matan gidan "la Mama".
- Wa ce ce kuma "la Mama"?
- Waɗanda suke bayan gidanmu. Tsofuwar da kika ce in riƙa kai ma tuwo.
- Ita ake ce ma "La Mama"?
- Sunanta kenan. Wai sun ce in tambaye ku ko su zo kallon talabijin?
- Su zo mana. Ba komi. Tele zan hana musu kallo? Ai mu ma Allah ya ba mu. Ba ƙwace muka yi ba kuma ba halinmu ya ba mu shi ba.

Duk cikin su, Fatsuma ta fi yawan zakkuwa. Har ma Irada ta fi shaƙuwa da ita, kuma in ta zo ta iske ni ina aiki sai ta karɓi aikin

ta yi. Tun ina fidda ma "la Mama" tuwo har ya kai inda a kowane ƙarshen wata sai na saya mata buhu biyu da jikka biyar na kayan miya. Ina haka ne ko dan tausayi. Domin wata rana na fito gari na iske ta a bakin ƙofa tana jirana. Na shiga da ita cikin falo. Ta fara ba ni tarihinta, ta ce mini mijinta ya mutu ya bar mata ɗiya mata huɗu. Sun ƙi makaranta, kuma ba aure. Ita ke faɗi ka tashi ta na ciyar da su da yayansu domin a cikin su Fatsuma kaɗai ce ba ta haifu ba. Tana sai da mangwaro da ayaba da sauransu don su samu abinci. Ta roƙe ni in ɗauki Fatsuma ta mini aikin gida don su samu abin sawa ga bakinsu. "La Mama" ta ba ni tausayi. Na shaida mata da Farid ba ya son girkin yar aiki, na kuma shaida mata in don abinci ne kar ta damu na riƙa taimaka mata. Da na gaya ma Farid sai ya ce ba damuwa domin Allah ya ce ka taimaka ma ɗan uwanka in kana son ya taimaka maka. Bayan buhunna da nike kai mata kullum sai na fidda ma "la Mama" kwanon tuwo. Sai in ban ɗora ba.

Kowane ƙarshen wata "la Mama" na da zane uku a wurina kamar yadda da nike kai ma Inna. Domin tanti Hawa ita ke sayo mini tufafi ni da Riyanatu. Ba ta dibin mun yi aure, hakin mazan-mu ne su yi muna sutura. Abin da nake ma "la Mama" ba na yi ma Innata. Fatsuma ta zama kamar ƙaunata, ko'ina za ni tare muke zuwa: wurin biki, wurin suna, wurin aure. A cikin abukkaina ba wadda ba ta san Fatsuma ba. Yadda ake ma amarya lehe haka, na ma Fatsuma lehe. Biya na wata biyu, na tara, na mata lehe. Zannuwa tsadaddu kuma wanda ake yayi da takalma, da jikkar hannu. Da na ga ba ta komi sai na biya mata makaranta don ta bar tallar. Makarantar koyon na'ura mai ƙwaƙwalwa na biya mata.

Irada tana da shekara uku. Ta yi wayo kamar yar shekara biyar. Ganin haka muka ɗauki shawarar sa ta makaranta. Bashir ya koma karatun shekara biyar a turai. Haka ya sa Riyanatu ta dawo gidan mahaifiyarta. Da Fatsuma ta gama karatu sai na nema mata aiki a ma'aikatar su Zainabu matar Ali abokin Farid. A ma'aikatar su Farid aka ba shi mota ƙirar marsandi don haka ya bar mini motar tashi ƙirar Starlat.

Duk da ma'aikatar su Fatsuma na da nisa da tamu, ni nike kai ta ma'aikatarsu na kuma maido ta gida. "La Mama" ta zamo kamar uwar da ta haife ni. Su Salamatu da Maimuna da Aishatu yannen Fatsuma sai abin da suke so suke yi cikin gidana. Tanti

Hawa ta kawo yan kunnen zinariya, na ɗaukar ma kaina na ɗaukar ma Fatsuma.

- Wallahi Farida ki yi hankali da tsofuwar can da ɗiyanta, inji Riyanatu.
- Mi kike nufi Riyanatu? Ai ba komi, akwai Allah.
- To na ji, Allah ya raba ki da sharrinsu.
- Amin Riyanatu.

Na fara ganin canji wurin Fatsuma da yannenta. Sun rage yawan zuwan da suke yi gidana, kuma Fatsuma da muke hira da ita yanzu in har Farid yana zaune Fatsuma ba ta zama kuma in ta zauna ba ta hira. In za mu wurin aiki sai ta ɓata lokaci sannan take fitowa don na yi fushi na tafi na bar ta. Domin ta san da ba na son makara zuwa wurin aiki. In an sauko ba na tarar da ita, kamin na zo ta taho gida. Na kirai ta don na ji dalilin canjin, sai da ta ɓata awa biyu kan ta zo. Ita da a da in na aiko ta zo tare da ɗan aiken take zowa. Da ta zo sai ta ce samari ɗan taksi ta samu shi yake maido ta gida.

Farid, da ba ya fita da dare, yanzu ya fara fitar dare. Wani gamin, ko ya sauko bai zowa sai ya cika dare. In na tambaye shi sai ya ce baƙi ya yi, wajen su ya tsaya. Ya tsaya aiki ne. Kuma ya bar cin abincin dare sai ya ce mini da baƙin suka yi abinci. Shi da bai cin abinci sai wanda na dafa. Haka in na aika a kiranyo Fatsuma in Farid bai dawo ba don ta fidda mini kewa sai a ce "yanzu ta raka abukkanta", "ta yi kwana ta ce kar a tada ta", "tun da ta tafi wurin aiki ba ta dawo ba".

Wata rana Zainabu ta iske ni wurin aiki ta ce mini maigadin ma'aikatarsu ya ce Farid yake zowa ɗaukar Fatsuma. Ban kama ba sai da na sauko daga wurin aiki da wuri don ba na jin jikina saboda ciki na wata biyu da nike ɗauke da shi. Da na shiga falo sai na ji dariyar Farid. A zatona shi da Irada ne. Na shiga sai na iske shi suna girki tare da Fatsuma suna hira. Washe gari na shaida ma tanti Hawa abin da na gani. Sai ta kauda mini tunani.

- Farida yi hankali kar ki sa kanki cikin damuwa. Waɗanda suke hira kullum har wasa suke da junansu. Mi nene na damu-wa? Kar na ƙara jin kin kawo mini wanga irin maganganu da ba su da manufa. Farid ya canza mini, ga laulayin cikina, ga sabon salon rayuwar Farid. Ina kwance cikin ɗakin, Irada na wasa sai

na ji an ƙwankwasa mini ɗaki na amsa. Ashe Salamatu ce yar Fatsuma ta shigo tare da sallama. Na amsa mata, na tashi zaune.

- "La Mama" ke son ganin ki.

- Tare kuke ne?

- Tana gida.

- To har Farid ya dawo daga wurin aiki ki ce mata ga ni nan.

Bayan minti talatin ta koma turo Salamatu.

- Lafiya dai! To bari na tashi.

Na rubuta ma Farid yar wasiƙa na ɗauki mayafi na rufe jikina muka fita ina kame da hannun Irada. Na tarar "la mama" da yarta Safiya suna hira. Na gaida su cikin ladabi, Salamatu ta ba ni wurin zama na ɗora Irada bisa ƙafafuwana.

- Safiya, ga uwata Farida. Ita ce komi nawa. In ba don ita ba da mun mutu.

- Allah ya miki albarka, Allah ya taimaka miki yanda kika taimaka musu.

- Amin.

- Farida in jin kina sa ma mijinki maganin da boka ya ba ki? Kin san mazan yanzu sai da asiri inji "La Mama" tana tambaya ta.

- Har ya ƙare ma, na faɗa.

Karya ko nike domin boka ta kawo gidanta wai saboda ni ta kawo shi. Da na shaida ma tanti Hawa ta mini faɗa har ta gaji. Ta ce abin da duk suka ba ni in zubar da shi cikin salanga. Ni ɗiyar babban malami zan shiga harakar boka. Ta ce in har ban daina ba, ta gaya ma baba.

- Albishrinki.

"La Mama" ta matso kusana.

- Goro "La Mama"!

- Kaunarki ta samu sadaki jikka ɗari uku. Ga su nan ƙilga. Ki gani. Ta miƙa mini ambulap, na karɓa na ƙilga kuɗin da ke ciki. Ga kuma wata jikka ɗari uku ta lehe.

- Alhamdu lillahi "La Mama". Wane ne zai aure ta?

Suka kalli juna ita da Safiya.

Wani tabbashinta wanda yake karatu a turai.


- Kin ga ko ba ta taɓa mini zancen shi ba.

- Auren gaugawa za a yi. Subdu mai zuwa za a ɗaura auren. yanzu na ba ki yuƙa na ba ki nama. Aje kuɗin lehen wurinki. Ku kuka san abin da za ku saya.

- To Farida zan ɗora miki nauyi domin ke za ki shugabancin auren. Mu kallo ne namu.

- To na ji. Na gode. Insha Allahu zan yi iya ƙokarina "La Mama".

Da na dawo gida na kwashe labarin na gaya ma Farid. Ya ce mini ya yi farin ciki. Na rasa gindin zama. Ina ta kai da kawowa ganin na fidda "La Mama" kunya. Na kawo buhun shinkafa biyu. Na sayi ɗan sa a jikka talatin sannan na ba da jikka hamsin na kayan miya don a dafa ma baƙi abinci. Ana sauran kwana uku a ɗaura auren, ni da Fatsuma muka je kasuwa na mata lehe. Duk zanen da ta ce tana so sai na saya mata shi har mai kayan ya biyo ni jikka ashirin.



Ana sauran kwana biyu a ɗaura auren Fatsuma, Farid ya zo cikin dare ya tada ni daga barci ya ce mu tashi daga gidan, mu koma wata unguwa. Da na tambaye shi dalili ya ce wanga gidan ya muna kaɗan.

- Farid ba ka bari har a kammala auren Fatsuma! Farid in ka shawarce ni da ba za mu ƙaura ba. Farid nan fa ba mu biyan kuɗin haya, da na wutar lantarki, da na ruwa.

- Ni gobe zan ƙaura. Ki zauna ke sai an ida auren. Yanzu son zuciyarki za ki bi, ba ni ba ko? Ko an ce miki kuɗin da nike samu bai iya biya mini abin da kika faɗa ne?

Washe gari na shaida ma "la Mama" bukatar Farid sai ta ce kar na saɓa ma mijina saboda auren Fatsuma. Fatsuma da Salamatu da Maimuna da Aishatu su suka kula da kai kayana

sabon gidan, kuma sun shirya mini kayan yadda ya kamata. Gidan na da babban falo da ɗakunan kwana huɗu da mangaza, da gwadala. Dakin da yake liƙe ga mangaza cikin shi Farid ya ce a sa kayanshi. Abin ya ba ni mamaki ƙwarai domin Farid da bai ma son mu raba ɗaki da shi yanzu shi ya koma ƙauye ɗaya? Ban ce komi ba. Na bi umurninshi. Na komo gida wajen ƙarfe ɗaya na rana. Farid bai zo gida ba. Na zauna har wajen ƙarfe biyu da rabi. Sai na yi waya a ma'aikatarsu, ba wanda ya ɗauka. Abin ya ban mamaki sai na koma gidan "La Mama". Da yake Farid bai dawo ba sai zaman gidan "La Mama" ya gagare ni na koma gida har yanzu Farid bai dawo ba. To yaya aka yi haka? Ko Farid yana fushi da ni ne? Na buga mashi waya sakatariyarshi ta ɗauka ta ce mini yanzu ya fita. Na shiga zurfin tunani. Na tashi na yi arwalla na yi sallar la'asar, na rasa abin da yake mini daɗi.

Ƙarfe shida da rabi ina zaune ina tunanin irin zaman da muke a halin yanzu da Farid. Na tashi na fara girkin marece. Ina cikin gwadala ina yankan nama sai na ji tsayuwar mota cikin gidanmu. Wai "La Mama" ta aiko su Salamatu wai na bado jikka goma sha biyar kuɗin hayar kujeru da rumfa. Na ɗauko kuɗin na miƙa musu. Farid, bai dawo gida ba sai wajen ƙarfe huɗu na dare. Ina zaune cikin falo domin na yanke shawarar na tambaye shi dalilin rishin jituwar da ke tsakaninmu. Ya shigo na tare shi don na karɓi jikkar hannunshi kamar yadda na saba. Sai kawai ya ture ni, da kaɗan na faɗi.

- Tafi ki ba ni wuri. Ke kuma mace ce? Ina amfani zaman aure da ke? A ce ina da matar aure ashe munafuka? Bace mini da gani shashashar banza.

Ya wuce ya shiga ɗakinshi ya kuble. A zato na mafalki ne nike domin ban taɓa tunanin ko gardama za ta shiga tsakaninmu ba. Na rasa abin da zan yi. Mi ne abin yi? Ba ni da mafita sai kawai na rarrashe shi. Na tambaye shi laifin da na mashi don in gyara kurena. Na je, na ƙwanƙwasa ƙofarshi tsawon minti goma. Ya yi banza da ni. Na zo na zauna sai da aka yi kiran sallar safe. Na tashi na je na yi wanka tare da arwalla don gabatar da sallar safe. Na shirya na zo falo don na dafa shayi. Na iske shi har ya dafa ma kanshi yana sha. Na durƙusa gabanshi na gaida shi. Ko kallo ban ishe shi ba, ya yi banza da ni. Ya yi tsaki. Baƙin ciki da kunya suka hana ni tashi. Hawaye suka cika mini idanu. Da kyar na

tashi na je na dafa shayi. Na zo na zauna bisan teburin cin abinci. Shan shayin ya gagare ni ya taso ya zo wurina.

- Ina kike shirin zuwa ne? Ke, da ke nike, ina zaki ne?

- Wurin aiki za ni, don na dawo wurin auren Fatsuma.

- Kar na ga kin fita daga cikin gidan ga kina ji na?

- Farid kana iya hana ni zuwa wurin auren amma ba wurin aiki ba domin ba mu yi haka da kai ba.

- Haka za ki gaya mini? To na ji wurin aikin ma kar na gan ki, kin tafi.

Yana magana yana zaro mini idanu.

- Farid ba mu yi haka da kai ba, wurin aiki Allah ɗai ke hana ni zuwa.

- To na ji ni da ke an ga mai gaskiya. In ni na auro ki, ko ke kika auro ni.

Na tashi na ɗauko jikkar hannuna da makullan motata yana tsaye ƙofar gidan.

- In ce kar ki fita ki ƙi bin umurnina ko? To in har kin je wurin aiki to a kan aurenki.

- Na ji.

Na fita na bar shi cikin gida. Ina ta kuka har na wuce wurin aikin da nisa ƙwarai sannan kaina ya kawo. Na shiga ofishina ina zaune aikin ya gagare ni. Ina ta tunanin faɗanmu da mijina? Sakatare ta turo ƙofar birona.

- Na'am na amsa mata.

- Ana kiran ki a waya.

Na ɗauki wayar sai na ji muryar Alhaji surikina. Gabana ya faɗi ras muka gaisa da shi.

- Farida ina so ki koma gida ga ni nan.

- In ce dai lafiya Alhaji?

- Lafiya lau Farida, ina son magana da ke ne.

- To Alhaji ga ni nan.

Na ɗauki motata na koma gida, na tarar da Alhaji da Hajiya da baba da tanti Hawa, Farid yana tsaye. A zato na Farid ya je ya gama ni da su. Na durƙusa na gaida su cikin ladabi da biyayya, na dawo kusan tanti Hawa na zauna a ƙas domin na san ita kaɗai za ta mara mini baya. Alhaji ya juyo ga Farid.

- Mutumen banza, rishin kunyar za ka gwada mini ko? Fita daga kaina maza kar na tattake ka yanzu. Farid ya samu wuri ya

zauna. Kanshi a sunkuye abin ya ba ni mamaki Alhaji yake zagin ɗan gatanshi haka?

Kenan zancen bai shahe ni ba. Ni na yi zaton daga shigata baba zai hau ni da faɗace-faɗace don haka ya sa na zauna kusan tanti Hawa. Alhaji ya juyo gare ni gabana ya faɗi na sunkunyar da kaina.

- Farida.

- Na'am Alhaji.

Na amsa cikin fargaba kai na a sunkuye.

- Ina son ki saurare ni da kunnen basira. Shi al'amari na duniya sai haƙuri kuma in Allah ya gama ka da mutum maras mutunci shi ma sai haƙuri.

Duk Alhaji ya rikita ni domin ban ce ya fahinci abubuwan da yake so ya faɗa ba. Yana ta mini nasiha.

- Abin da zan gaya miki bai da daɗin faɗa amma sai ki ɗauki haƙuri domin Farid in har ni na haife shi ba zai gushe maganganuna ba kuma ba zai ƙi abin da ba na so ba.

Nan da nan baba ya katse mashi maganarshi.

- Haba Alhaji ka bar faɗar haka mana Farid ba ɗanka ba ne? To ɗan wanene ne? Alhaji ai namiji mijin mace huɗu ne ba don mace ɗaya aka yi shi ba. Alhaji ƙaddara ce.

Gabana na dakan uku-uku mi zan ji ne?

- Na san da wannan. Amman malam Musa ai abin da Farid ya yi ai bai kamata ba. Ta yaya zai yi neman aure ya ƙi gaya mata. To wane irin zama ne suke da ita?

Na ji wani abu ya mini lum, sai na daina gani har tsawon minti huɗu.

- Kuma ya rasa wadda zai auro sai yarinyar maras mutunci. Ya ci amana. Ai wannan cin amana ne.

- To Allah ya ce matarka kabarinka. Ko ina take za ka neman ta.

- Amma "la Mama" ta cika yar cin amana, sai Allah ya fidda miki alhakinki a kanta...

Na zaro idanu mi zan ji ne?

-... Farida kar ki ji komi. Ki maida komi ba komi ba. Auren cin amana ai ba ya ƙarko. Tashi ki koma ɗaki ki rungumi ƙaddara. Allah zai saka miki a kansu daga shi Farid har "la Mama".

- Hawa wai mine ne sunan yarinyar ma? Tanti ta yi sanyi kamar an aiko mata da mutuwa.

- Fatsuma! tanti ta faɗa cikin sanyin jiki.

Sai lumfashina ya ɗauke amma da yake suna zance ne sai ba su gane abin da yake faruwa ba. Sai da lumfashina ya dawo. Hajiya da tanti suka raka ni cikin ɗakina suka ta yi mini nasiha har na ji ban damu ba. Tanti ta buga ma Riyanatu da Jamila da Zainabu da Umu waya, don su zo su taya ni hira. Su Hajiya da tanti Hawa sai wajen ƙarfe biyar na marece suka tafi gida da sharaɗin su dawo in an jima. Duk tsawon lokacin da suka yi suna ta mini nasiha, Riyanatu da Umu suna ta kuka don tausayi. Umu ita ta yi mini gorar amarya lokacin aurena. Ƙarfe shida da rabi suka umurce ni na yi wanka don na tsala ado. Domin ba inda Fatsuma ta fi ni.

Na yi wanka na shirya ado gwanin kyawo. Na sa wata doguwar riga shadda masara wadda ta sha aiki da zare mai walƙiya. Suka gyara mini gashina, na ɗaura adiko. Sarƙa ta zinariya huɗu na jera ga wuyana da hannuwana, kowane na da warwaro gomagoma yatsuna takwas duk suna da zabba. Na sanya takalmin da Bashir ya aiko mini ni da Riyanatu. Ɗakina sun gyara mini shi sai walƙiya nike. Nan da nan gidan ya cika maƙil da yan uwa da aminnan arziki. Haka ɗakina ba ka samun inda, za ka soka kara. Abukkaina wanɗanda muka yi makaranta tare da matan abukkan aikin su Farid da matan tsofuwar unguwarmu, ko makiyina ya gan ni sai ya yaba. Sai walƙiya nike. Muna ta hira kowa na faɗar albarkacin bakinshi. Riyanatu da Zainabu suka yi ta hidimar ciyar da baƙi. Balkisa maƙwabciyata ta tsohon gidanmu ta shigo.

- Kai yan uwa in ba abin namiji ba, kana da mata kamar Farida mi za ka nema ga wata? In da ni ce …, amma maza akwai butulci.

Yanzu kam mata sun shiga gonar maza ba wadda take yaba su sai da suka sanya duk na mance da damuwar da nake ciki.

Ƙarfe tara da rabi aka kawo amarya. Ga al'adarmu dai in an kawo amarya dole ne sai an kai ta ɗakin uwar gida amma su sun ƙi kawo amaryar ɗakina. Suka aiko Salamatu ta shaida muna da kar mu sa rai za a kawo amaryar ɗakina. Har Umu ta fara rigima da Salamatu sai aka raba su. Riyanatu ta ce a ƙyale su kunya za su yi. Dangin su Fatsuma mata suka cika muna ɗaki wai sun zo gani na. Har Jamila ta hana su, suka fara faɗa. Da ma shi suke nema. Sai Balkisa ta tashi.

- Jamila bar su su wuce. Ku zo ga ta, son kowa ƙin wanda ya rasa. Watan salla sha kallo, ba yaudara, ba cin amana, ba ƙwacen miji.

Sun fara faɗace-faɗace sai Hajiya ta raba su. Ko kitson bai sa aka maida Fatsuma gida ba. Washe garin auren ba kunya ba tsoron Allah Fatsuma ta karɓi girki a hannuna domin da safen na fito don na ɗora shayi sai na tarar da Farid da Fatsuma suna zaune a teburin cin abinci suna karin safe. Abin mamaki, na durƙusa na gaida Farid da kyar ya amsa. Na koma ɗaki don na yi shirin zuwa wurin aiki. Har na fito na tuno da ban karɓi kuɗin kayan miya ba. Na ƙwanƙwansa ƙofar ɗakin, Farid, ya amsa. Sai na shiga na iske su kwance, Farid yana rungume da Fatsuma. Raina ya ɓace. Yanzu Farid ya san yana kwance da matarshi, ya sa na shiga?

- Lafiya?

- Kuɗin kayan miya, ba ka ba ni ba.

- Fatsuma za ta yi girki yau.

Na fita. Na je wurin aiki. Da rana kan na dawo Fatsuma ta gama abinci. Suka ci. Duk gidan "la Mama" ba wanda aka bari. Suna nan na shiga na gaida su. Ba wanda ya amsa mini daga Farid har yan gidan su Fatsuma sai ma dariya suka ɓata mini. Na shiga ɗaki ran nan ban ci abinci ba. Fatsuma sai da ta yi kwana goma sha biyu tana girki ni dai ina kallon su. In ta yi kuwa ba ta ba ni abin da ta dafa. Abin ya yi matuƙar tada mini hankali. Yanzu Farid yake wulaƙantar da ni haka? Ina mafita? Farid in gan shi ma sai in zan fita ko shigowa cikin gidan. Amma bai kamata in shaida ma wani ba domin za a ce ba ni da haƙuri, kuma a ce kishi ne gare ni. To zan bar ma Allah zaɓi. Na tashi, na yi raka'a biyu ta nafila, na gabatar da buƙatata ga Ubangijin da ya halicce mu. Ina tashi sai ga Farid ya shigo ɗakina ya zauna bisa gadona. Na juyo gare shi na gaida shi ya amsa sama-sama ya tashi tsaye ya zuba hannayenshi cikin aljifun wandonshi.

- Ba zama na zo ba don na shaida miki ne na raba muku girki. Ki fara girki yau. Kuma batun zuwa ɗakina ni zan neme ki. In ban kiraye ki ba kar na gan ki kin taka ɗakina. Ga jika hamsin ki aje don kayan miya. Domin ba na son ki ɓata damuna in muna hutawa, kin ji ko?

- Na ji Farid!

Ya wuce ya bar ni ina ta tunani. In ranar girkina ne Farid da Fatsuma ba sa zama a gida kuma ba sa cin tuwon da na ɗora. In

ta ɗora kuma, ba ta fidda mini. Ina zaune cikin falo na gama girki ina kallon talabijin sai waya ta yi ƙara. Na ɗauka. Babban su Farid ke neman shi. Na tashi don na kirayo shi. Na turo ƙofar na shiga a hankali sai na iske Fatsuma da Farid kwance. Na yi nadama zuwa ɗakinshi domin ban so na tarar da shi a cikin halin da na iske su ba. Kai duniya! Har ran girkina Fatsuma tana shiga ɗakin Farid? Na koma ɗakina ina tunanin abin da na gani, ai wannan cin amana ne. To yanzu na gane abin da ya sa Farid ya ce na bar zuwa ɗakinshi ko ni ke da girki ashe Fatsuma ke kwana ɗakinshi. Wanga abin ya kamata a ce na shaida ma ko da tanti Hawa ne. Farid ya shiga ɗakina yana huci. Ya zaro bulala ban ji komi ba sai ya fara ba ni kashi tun ina kuka har na yi sanyi. Ko motsi ba na yi sannan ya daina bugu na. Kukan ma ya gagare ni da kyar na tashi zaune. Ga ni da cikin wata biyu. Kukan da nake ya sa Irada ta shigo:

- Mama mi ya ji muku? Kuna kuka ne? Mama ina jin barci.

Nan da nan marata ta fara mini ciwo har ban san abin da da nake ciki ba. Na zo falo ba kowa cikin gida. Farid da Fatsuma suka fita yawo kamar yadda suka saba. Na ɗauki makullan motata na fita na bar Irada tana kwana. Awa guda na yi kan na kai gidan haifuwa. In ina tuƙi, in cikina ya murɗa, sai na kashe motar. Na kwanta bisan sikiyarin motar. In ciwon ya rage na tada motar. Haka na yi ta yi sai da na isa a asibiti. Tsayuwata goma kan na kai asibitin. Daga zuwana likitoci suka tare ni. Ba wanda bai san ni ba domin ina ba da labaru. Babbar su ta shaida mini da cikin zai zube nan da awa ɗaya. Na umurci a kawo mini waya na buga ma tanti waya. Ni kam na ga lokacin da tanti ta shigo. Ban san abin da ya faru daga baya ba kuma sai da na yi kwana uku sannan na fara sanin abin da nake ciki. Na buɗe ido tanti da wata likita suna tsaye a kaina sai daga baya na tuno da sanadiyar kashin da Farid ya ba ni ya sa aka kwantar da ni a asibiti. Na yinƙura na tashi tanti ta hana ni domin akwai roba gare ni ta ƙarin jini. A kwana na biyar na samu kaina na warke ṣarai. Muna hira da tanti sai Hajiya da Inna suka shigo. Bayan mun gaisa Hajiya ta tambaye ni.

- Farida likitoci suka shaida muna da ban kashi ya zubar miki da ciki. Ba mu bayyani.

Kaina ya zan ganga don kunya da nauyin Hajiya da nake ji.

Ko na gaya masu gaskiyar lamarin? Wata zuciyar tana raya mini kar na gaya musu.

- Farida da ke nake domin tun da aka kwantar da ke Farid bai taka ƙafarshi a nan ba daga shi har matarshi.

Da na ga sun matsa mini sai na gaya musu zaman da muke ciki.

Da na dawo gidan Farid ya amshe girki daga hannuna. Na zamo kamar hoto a cikin gidan. Wata rana ina kwance cikin ɗakina, na sauko kenan daga aiki sai Farid ya turo ƙofar ɗakina ya shigo.

- Allah waddan wannan hali naki. Ina kika kai buhunnana ne? Buhunna sun kai ashirin cikin mangaza yanzu ba ko ɗaya. Gidan uban wa kika kai su?

- Farid kar ka zage ni, na faɗa cikin ɓacin rai.

- An zaga. Tafi ki gaya wa uban da kike so. Barauniya!

- Yar aikin Fatsuma ta ce ke kika zo da mota kika kwashe su.

- Na bar ta da Allah. Na san iyayena talakkawa ne amma na fi inda zan satar abinci na kai musu. Kenan ina amfanin biyan da nike ɗauka ne? Ka sani da Bashir a hannunka yake aiko mini jikka ɗari kowane ƙarshen wata, to ban ga abin da zai sa in ma sata ba.

- Ba na son surutu. Ki biya ni ko na kai ƙarar ki gidan alƙali zaɓi ɗaya.

- Farid ka lura fa da abin da kake yi. Ni za ka kai ƙara gidan alƙali.

- Ba kya biya na ko? To zan gaya ma daraktanku daga an yi biya a ba ni biyanki.

Na sha kuka har na gaji, na ɗauki shawarar biyan shi domin in har ban biya shi ba, to zai ɓata mini suna. Na ɗauki takarda na rubuta mai yar wasiƙa don ya gayi nawa zan biya shi. Na ba Irada ta kai mashi ya rubuto mini jikka ɗari biyu da hamsin da bakwai. Na yi sa'a Bashir ya aiko mini kuɗi na gama da nawa da suke aje. Na ba Irada ta kai mashi ya karɓi kuɗin ya ba Fatsuma kuma a gabana.

Wata rana da safe ban je wurin aiki ba, da yake zaman ɗaki ya ishe ni sai na zo cikin falo na zauna. Irada ta ce mini tana son madara. Na ƙyale ta. Abinka da yaro sai ta aza mini kuka. Na tashi na shiga gwadala don na kaɗa mata madara sai Fatsuma ta iske ni ta ture ni tana ƙoƙarin amshe mini gwangwanin madarar.

Sai na bankaɗe ta.

- Maigida ya ba ni izinin hana ki shiga gwadala.

- Amma Fatsuma ba ki san kunya ba. To bari na gaya miki ba ki isa ki hana ni shiga gwadala ba tunda ba gidanku ba ne maciyar amanar banza.

Kan na rufe baki sai ta duro mini ga wuya tana ƙoƙarin shaƙe ni. Habba ban san lokacin da na yarɓo ta a ƙasa ba. Na hau ta da kishi sai ga Hajiya mahaifiyar Farid ta shigo.

- Inna lillahi wa Inna illaihi raji'una. Mi zan gani ne? Farida, Farida?

Ta tada ni daga bisa Fatsuma. Tana ta shasshekar kuka.

- Farida? Farida mi nene haka? Tafi ɗakinki, tafi mana.

Na tashi na koma ɗakina sai Hajiya ta iske ni ina zaune bisa gado ina kuka domin na yi nadamar aurena da Farid. Da man, ban so auren ba kawai umurnin iyaye na bi. Ga abin da ya haifo mini. Ba na ci, ba na sha gidan miji, alhali kuwa a zamanshi nike. Hajiya ta zauna dap da ni.

- Farida ina roƙon ki ne don Allah faɗan ku bar shi domin komi aka yi ke za a ba rashin gaskiya domin ke ce babba. Na durƙusa gabanta.

- Hajiya ku gafarce ni. Ni ma ba na son faɗan ita ta fara bugu na. Kuma na fi son in bar ta da Allah domin biyan Allah ya fi na rama ma kaina. Na kwashe duk labarin na gaya ma Hajiya.

Hajiya ta ce: "Ya sa ki biyan abinci?" Na kuma ba ta labarin yadda aka yi, Hajiya har kuka ta riƙa yi don tausayi.

- Kar ki ce komi. Za mu yi maganin abin. Kin ji.

- To Hajiya.

- Zan tafi.

- Hajiya ku tafi da Irada domin Fatsuma ta hana ta zuwa falo kullum in ta je falo sai ta shigo mini da kuka ta ce Mama ta ba ta kashi. Irada ba ta zama a ɗaki daga na kulle ɗakin ta fara mini kuka. A dole sai na bar ta ta fita.

- Wanga rishin imani har ina? To in sun tsaneki ai Irada ɗiyar-su ce. To zan gaya ma Alhaji. Mun san abin da za mu yi in ya so shawarar da muka ɗauka zan sanar da ke ta waya.

- Kar ma ku wahalar da kanku ko kun yi waya ba na ji domin ba ta shaida mini.

- Allah sarki. To don Allah Farida ki rika cin abinci. Dibi don Allah yadda kika koma. Sai ka ce icce. To Farida kar ki gaji da nafilfilunki kin ji. Allah zai kawo sauki ga lamarin. Yi zamanki. Ba na son rakiya.

Za ta fita sai ga yan gidan su Fatsuma sun shigo kowa da makaminsa daga mai icce sai mai tabarya wai sun zo su kashe ni domin na so na kashe musu kanwarsu. Suna kokarin ture Hajiya da ke tsaye kofar daki, Salamatu a gaba.

- Hajiya ba mu wuri mu kashe ta.

- Ku kashe ta? Ku ko ai ba haka ba ake yi! Ita ma tana da yan uwa in sun taso su ma fa? Mi kuka san za a yi? Kenan fadan ya koma yaki? cikin aure ba a daukar fansa. Yanzu abin da nike so gare ku fadan nan a bar shi ku koma gida har mijinsu ya zo shi zai dauki matakanshi domin shi ya auro su. Salamatu ta yi kara-rap ta shiga maganar.

- Ba auro ta ba ya yi, sadaka aka ba shi ita.

- Sadaka? Kenan ke ba ki da labari? Guduwo ta yi daga wurin iyayenta ta zo ta zauna da shi. Wa ne bai sani ba? Inji Maimuna.

- Gaskiyar ku in ba haka ba ai da irin wulakancin ga da take gani ai da ta koma gidansu.

Hajiya na ta kokarin fidda su daga cikin gidan sai Salamatu ta dawo.

- Kar ki yi zaton mun bar fadan ne; don sarakuwarki muka kyale.

- Ba kun san hanyar da nike bi ba in za ni wurin aiki? To in har kun isa ku tare ni ku duka ba wanda na fidda. A kasa zan je wurin aiki yau ina jiran ku. Ku har kuna da bakin magana ku? Albarkacin auren sadakar dai na ciyar da ku har aka gan ku aka aura. Cin amanar ne kun gada, ku yi ta yi. Ku kai makura.

- Ke rufe mini bakinki maza. Gabana za ki biye musu kuna cacar baki ko? Wane irin rishin kunya ne wannan? Inji Hajiya

Kunya ta kama ni domin na bata ma Hajiya rai. Ta fita da su jim kadan sai ga ta ta dawo ina ta kuka. Ta yi ta ba ni magana ta yi tafiyar ta. Ashe da Fatsuma ta tafi gida ba ta dawo ba. Shigar Farid cikin gidan su "la Mama" ya kai sau uku. Ta ce sai ya kore ni za ta bar Fatsuma ta koma gidanshi. Farid ya turo kofar dakina da karfi sai da na firgita. Ji kake gam!



- Zaman aure ba dole ba ne ko? Kuna da gida? To abin da nake so gare ki tashi ki koma gidanku, ba zan taba yarda na auro mace ki rika gallaza mata ba ke, ko ba ku da gida ne?

- Wai ba ba mu da gida ne ba, ba zan fita ba in har ba ka ba ni takardar rabuwa ba.

- In wannan ne ta kwana gidan sauki. Gobe insha allahu na aiko ta har da kayan dakinki.

- To don Allah ka mini aikin gafara da abubuwan da na maka.

- Ba komi.

Daga zuwa na gida na kwashe labarin na gaya ma tanti. Nan da nan ta ma Hajiya waya. Muna tsakar cin abinci sai ga Alhaji da baba da Hajiya. Baba ya yi ta mini fada wai ni ce ba ni da hakuri, kuma ba ni da biyayya, Alhaji ya dauki magana.

- Malam kar da ka yi haka mana. Farid ne bai da gaskiya. Ba kiran shi muka yi ba ya ki zuwa. Sai da mu da girmanmu, muka je gidanshi. Ban san har Farid rishin kunya gareshi haka ba. Gama cin tuwonki sai ku maida ta gidanta ke da Hawa.

Cin tuwon ya gagare ni don bakin ciki, ina ta kuka.

Da muka zo Farid yana kwance bisa cinyoyin Fatsuma bai ma san ko mun shigo ba ko uwarshi bai gaida ba.

- Farid wace irin rishin kunya ce wannan? Ashe ba ka da mutunci ne? Allah ya waddan halinka, Hawa mu tafi.

Na yi kuka har na gaji sai na tafi na yi wanka tare da arwalla don na gabatar da nafilar da na saba. Har na shiga cikin bargo.

Sai Farid da Fatsuma suka shigo ɗakina Farid ya jayo ma Fatsuma kujera ta zauna yana tsaye a kanta na tashi zaune.

- Munafuka kin gama ni da iyayena ko? Daman na auro ki ne saboda gudun fushin iyayena, daga yau a zaman kanki kike ba ni cida ki. Ko ruwan gidana kika sha to ban yafe ba. Daga duniya har lahira. Zaman gidana kuwa yanzu na gane da a gidanku babu ɗakin da za ki zauna ne. Zan buɗa miki ƙofar baya domin ba na so na dinga ganin ki kina shiga ta falo.

Na girgiza kai: "Yanzu Farid yake wulakantar da ni haka? Duniya kenan. Allah sarki wai kuma gaban Fatsuma yake wulakantar da ni. In na koma gida baba ya maido ni. Yanzu haƙuri zan yi. Domin an ce mai haƙuri yakan dafa dutsi har ya sha romonshi. Kuma an ce bayan wuya sai daɗi, yanzu ƙoƙari zan yi da roƙon Allah. A ce na bar ma Fatsuma mijina ai wannan kasawa ce. Na ɗau aniyar komi zan gani haƙuri zan yi na zauna."

Ali abokin Farid, da matarshi Zainabu sun zo ganin mu sai Ali ya tambaye ni. Farid ya yi ta zagi na wai ya kore ni na ƙi tafiya. Ali da Zainabu suka mushi nasiha ya tuna baya, kuma irin su Fatsuma don abin hannunshi suke son shi. Yanzu in ya koma ba ya da ko dala, tana rabuwa da shi. Da alama wa'azin ya razana Farid. Ina zaune ina kallon talabijin da Tanti Hawa ta sayo mini domin kallon tele kawai yake kai ni falo. Sai na ji an turo ƙofar ba. A zato na su tanti ne. Sai ga Farid da Ali da Zainabu. Suka zauna muka yi yar hira da suka tashi tafiyarsu muka raka su har gindin motarsu. Wurin dawowa na bi ta ƙofar da Farid ya buɗe mini sai ya kirayo ni.

- Farida ina za ki?

Na yi banza da shi.

- Farida ina za ki?

- Daki ne za ni, na faɗa cikin fushi.

- Da kike bin baya fa?

- Baya ya kamata na bi mana; kai fa ka ce in riƙa yin hakanan.

Ashe duk maganar da muke Fatsuma tana kallon mu. Da yake ƙofar baya na bi duk wanda ya bi ta falo zai rigai ni. Da na shiga ɗakina sai na tarar da Farid a kwance bisa gadona tare da Irada. Na zauna na ci gaba da kallon talabijin. Farid ya taso ya yi ta ba ni haƙuri. Har kuka ya riƙa mini domin ba da son shi ne ba. Ya raba muna girki tsawon kwana bakwai, ya koma yana shiga

ɗakina kamar a da. Amma a lokacin duk da na yi girki sai Fatsuma ta ɓata shi da gari ban gani ba. In na ida sai na aje tuwon bisa teburin cin abinci sai ta cika mini gishiri, ko wani abu kamar haka. Da yake kwana huɗu Farid yana cin tuwona amma in ta yi girki Farid bai ci domin ba ta iya girki ba. Saboda haka ne Farid ya ɗauka mata mai yi mata aiki. Kwana biyu daga ni har shi ba mai cin tuwon. Duk tsawon kwanakin ga, Fatsuma ba ta fito-wa ko falo. In na tafi aiki "la Mama" take zowa tana binne layu da magunguna.

Akwai wata rana, na fito daga wurin aiki da misalin ƙarfe shida sai na iske ƙofar ɗakina a buɗe alhali ko na kuble ta da makulli. Na shiga sai na iske duk kayan ɗakina an yi ɗaya-ɗaya da su. Katifar da take bisa gadona an kece ta kashi shida. Talabijin ɗita an fashe ta. Duk inda ke da madubi cikin ɗakin an farfashe shi. Fatsuma ba ta gidan don kar a ce ita ta yi shi. Da yake lokacin zuwa aiki ya yi sai na aje tufafin da na amso daga wurin mai wanki bisan gado. In na sauko da dare na sa su cikin almuwar. Sai na iske duk an tattale su yanda ko an ɗimka su ba su sanyu-wa. Na ma tanti waya don ta zo ta gani da idonta kar a ce ƙazafi ne. To da na gwada ma Farid sai ya ce mini.

- Kin san da gidan haya ne ko? To kisan dubarar da za ki yi ki meida maduban tagoginsu domin kar ma ki yi zaton zan biya su.

Ya wuce ya bar ni tsaye tsakar ɗaki. Ya sake dawowa tare da Fatsuma. Na fara ganewa da sammace shi suka yi.

- Kar ki sake biya ta falon matata. In har ta ce mini ko wuce-wa kin yi cikin falo to ki kuka da kan ki. Ba ni makullan motata.

Na tashi na ɗauko mashi ya karɓa ya ba Fatsuma.

- Ina takardun?

Ya juyo gare ta.

- Sheri daga yau na mallaka miki motata.

- Daga yau ma na fidda matata daga aiki. Yanzu ke kuma ba na son na ga kina aiki.

Ya fidda Fatsuma daga aiki. A kowane ƙarshen wata sai ya linka albashinta sau biyu.

- Ina amfanin zaman aure da ke? Ba ki san ma yadda ake riƙe miji ba. Yanzu na san na yi aure.

"Allah na gode ma!" Yadda na ga ranar, haka na ga dare. In ba kuka ba ba abin da nake yi. Tunani ya zo mini. Na tuna,

lokacin da ana sauran sati a ɗaura muna aure. Duk mun gamu a gidan da baba da Alhaji da Hajiya da tanti Hawa da Bashir da ni da Inna da Farid. Ina ta kuka.

- Baba wallahi ba na son Farid, kun san da ina da wanda muka yi alƙawali da shi Idris.

- Na sani Farida amma ai ni ma mun yi alƙawali ne da Alhaji tun lokacin da kika zo duniya.

Na ƙara fashewa da wani sabon kuka.

- Baba ya kamata a bar wanga auren tunda ba na so, Farid ma ba ya so.

Sai ya yi kararap ya karɓi maganar.

- Farida wallahi ni kam ina son ki, kuma Alhaji in har ban auri Farida ba to ba zan yi aure ba har duniya ta naɗe. Na rantse har da karatun alƙur'anin da na yi. Farida mi na yi miki ne da kike ƙyama ta?

- Kawai don ba so a tsakaninmu. Ba abin da ka mini son ka ne ba na yi.

- Kar ki faɗi hakanan ni kam ina son ki. Da girmanshi yake kuka da kyar tanti ta rarrashe shi. Su baba suka mini ca har na yarda.

- To Farid ka ga ta yarda kar dai ka je ka ci amanarta, inji Alhaji.

- Alhaji wallahi ba zan ci amanarta ba in na ci Allah ya saka mata.

Wani tunani na wani lokaci ya zo mini: Bayan wata uku da yin auren mu muna kwance bisa gado Farid na ta wasa da gashin kaina, muna ta hirar duniya irin ta mata da miji.

- Farida mine ne ba ki so a cikin zaman aurenmu wanda in na miki zai ɓata miki rai?

- To Farid ni komi za ka mini ban da wulaƙanci balle a gaban kishiyata ko ɗiyana.

- Har kin ban dariya kishiya kika ce fa Farida? Ai ni na ƙare aure a duniya, to mi zan yi da wata mace alhali duk abin da ake so ga matar aure kina da shi, biyayya, tarbiya, ladabi, girmama-wa, addini ... kai in na ce in zana za mu kwana a zaune.

- Kai Farid akwai cika baki. Har ka ce mini ba ka aure? Sam ban yarda ba domin namiji mijin mace huɗu ne. Kuma ni ba na fidda shakku domin tun da na zo na san akwai waɗansu baya. Sa'ar mace mijinta ya samu kuɗin yin aure. Zancen kishiya a bar

shi. Na san komin daɗewa za ka ƙara wani auren amma ni kar ka wulaƙantar da ni gaban ta.

- Farida in na wulaƙantar da ke ai na zan butulu ko? Wallahi ba zan miki kishiya ba ni da ke sai in wani ya mutu. In kin riga ni mutuwa haka zan zauna har ni ma wa'adina ya cika ko? Alƙawali na ɗauka.

- To hausawa suka ce alƙawari kaya ne ko?

Da na gama tunane-tunanena, na shafe hawayena na kwanta.

Ba shakka al'amarina ya koma gidan jiya. Ya maido dokar hana ni zuwa falo, ya kuma karɓi girki daga hannuna yanzu har ya fi da tsanani. Na shaida ma tanti, ta ce na ɗauki hakuri.

Bayan wata biyu na fara samun matsaloli. Na je asibiti likitar ta shaida mini da ina da juna biyu na wata biyu da rabi. Hankalina ya yi matuƙar tashi ni da nike cikin wanga mawuyacin halin za a ce ciki ne da ni. Kukana ya koma mini sabo sai da ya kai ni kwance. Laulayin cikin na damu na. Da alamu wanga cikin zai wahalshe ni domin tun yanzu na fara amai da sauran ciwace-ciwace. Na yi rishin lafiya, Riyanatu ta zo jinya ta domin a gida nike, likitar tana zowa yi mini magani. Duk tsawon kwanankin da na yi a kwance Farid bai ma san ko ina rishin lafiya ba. Daga shi har matarshi. yan gidan "la Mama" kwana ɗai ke maida su gidan-su sai su yi ta yi mana habaici. Riyanatu ta ce kar na tanka musu. Da kwanciyar ta ishe ni sai na umurci Riyanatu mu fita waje don na yi yawo. Muna takawa ɗaya-ɗaya muna zagaye gidan sai na ji zuciyata, tana tashi na fara amai. Farid da Fatsuma suka shigo cikin gida sun dawo daga unguwa. Fatsuma ta ɗaga kanta ta wuce. Riyanatu ta gaida Farid ya amsa cikin zuciyarshi bai ma kalli wajen da muke ba. Riyanatu ta je ta kawo mini ruwa na sha muka koma cikin ɗaki. Farid ya iske mu muna zaune muna hira, ba ko sallama, yana ta huci.

- Kar a ce ciki ne gareki? In ciki ne sani abin da za ki yi, domin in har matata ba ta haifu ba to ba na son na gan an haifu a gidana. Cikin nan ki san yadda za ki yi da shi. Ni na ce ina son na haifu da ke? Na gaya miki, ina ƙara gaya miki ki san matakin da za ki ɗauka, ya fita ya bar mu.

- Farida? Anya Farid yana a kan hankalinshi kuwa? Wanga abin ba banza ba. Mine ne nufinshi?

- In zubar da cikin mana.

- Ko kusa, Farid anya ma? Lallai Farida ashe cikin wagga azabar kike ne? Gwara rabuwa da wannan bala'i, ki zubar da cikin don matarshi ba ta haifu ba.

- Yanzu kam rabuwarmu za ta tabbata domin Allah na tuba, Allah ka yafe ni, yau ko cikin shege na yi ba zan zubar da shi ba balle cikin da na yi cikin aure.

- Ni wallahi ban yi zaton Farid zai miki haka ba ganin wahalhalun da ya sha kamin ya shayo kanki a yi aurenku.

- To ya ci moriyar ganga ba dole ya yada korenta ba.

- Ki san "la Mama" da ɗiyanta sun ci amanarki ko?

- Na bar su da Allah.

- Shi kenan kuwa. Ni barci ma nake ji. Kwanta ki huta Farida.

Fatsuma na ta ƙoƙarin fidda ni daga cikin gidan. Salangar Farid, ruwan bai wucewa don haka ya kawo masu gyaran salangar. Da suka buɗe ashe layu suke hana ruwan wucewa. Fatsuma ta ce ta taɓa iske ni ina sa layu cikin salangar har muka yi faɗa da ita. Farid ya kire ni. Gaban masu gyaran salangar ya fara zagi na.

- Allah ya waddan halinki, ku diba wai kamar ita ba kunya ba tsoron Allah tana sa mini magani. Wai don na so ta. So dole ne? Ba ta son ta ga matata cikin gidan. Ina korar ta, ta ƙi tafiya gidansu. Gaya ma bokanki wanga maganin bai ci ba.

- To masoyina ba ta zuwa domin ba wurin zama a gidansu. Ba su samu abin sawa a baki ba bale ɗakin zama. Don Allah abin ƙaunata ba na so kana yawan ɗumi kar ka gajiyar da kanka, zo ka je ka huta.

Ta kamo shi suka shiga ɗakin, kunya da baƙin ciki suka hana ni shiga ɗakina. Sai da mutane suka yi ta ba ni haƙuri suna min nasiha. Na yi godiya na koma ɗakina.

Ina wurin aiki sai Farid ya mini waya yana son ganina da gaugawa har na so kar na je domin na san wani sharrin aka ƙulla mini. Sai na ari motar wata abukkiyar aikina na je gida daga shigata Farid ya share ni da mari.

- Ina kuɗina? Tafi duk inda kika sa su ki fiddo su. Miliyon uku na aje cikin jikka ta ke kika ɗauke su. Tafi maza ki fiddo su. Yanzu sata kika shiga kuma.

Fatsuma da "La Mama" suna tsaye gefe ɗaya.

- To Farid a tafi a binciki ɗakinta domin mu ba mu gadi sata ba. Ba ka binciki ɗakin Fatsuma ba?



- To mu tafi.

Mun shiga ɗakina sai ga tanti Hawa da Hajiya sun shigo cikin ɗakina. Farid yana yin jifa da kayana ina tsaye ina kuka, Fatsuma da "La Mama" suna kallon mu.

- Mine ne? Mi aka yi ne, kai maras kunya?

- Hajiya, sata ta yi mini kuɗina ta sata. Har miliyon uku.

- Inji wa?

- An gan ta lokacin da ta shiga ɗakina, kuma jikkar an gan ta da ita ta shiga da ita cikin ɗakinta.

- Hajiya ƙazafi suka mini ni da ba na shiga ɗakinshi!

- "La Mama" ku fita ku bar mu ɗakin, inji Hajiya.

Tanti tana tsaye ta kama baki ba ta ce komi ba.

- Ba ni fita domin a ce ɗiyata ta yi satar! Mu ba mu gadi sata ba, Farida ta sace kuɗin.

- To don Allah "La Mama" wa ya gaya miki da ita ta sace kuɗin? Allah ya saka mata a kanku inji tanti Hawa.

- Hawa bari maganar. Ku dai ku ba mu wurin.

"La Mama" da Fatsuma suka fita.

- Farid ka yi hankali da abin da kake yi fa. Ka yi taka tsantsan da duniya fa. Kuma Farida ba ta shiga ɗakinka ba. Ba ta da makullan ɗakinka yaya za ta yi ta sace kuɗin ka. Kuma wa ya gaya maka ita ta ɗauki kuɗin?

- Fatsuma.

- Farid in ban tashi tsaye ba, sai sun haukata ka.

Farid yana ta nema ya jayo armuwar kita, sai jikkar kuɗin ta faɗo. Na ɗora hannuwana bisa kai ina ta kuka. Tanti ta tashe ni tana kuka ita ma.

- Kai wanga irin zaman auren Hajiya gara su shafa ma junansu lafiya domin ni ma na gaji. Yaya za a yi aure kullum cikin bakin ciki, kullum ita ta yi? Ai ba haka ake yi ba. Hajiya gara a sake shiri domin ni ba zan bar ta ta hallaka a kan banza ba.

- Haba Hawa kar da ki ce haka mana.

- To Hajiya ni zan rantse da alƙur'ani ba ta ɗauki kuɗin ga ba.

- Ai cikin ɗakinta na samu kuɗin, kuma ita ta sato su zancen wahala ai batunta ne wannan, domin na sallame ta ku kuka maido ta.

- Haka za ka gaya mini Farid?

- Hawa ƙyale shi. Fita maza, maras kunya Allah ya wadan halinka ɗan iska maragaici sammatacce. Fita na ce maras wayo.

Farid ya fita yana ta gunguni.

- Hajiya wallahi ba ni na ɗauki kuɗin ga ba.

- Na sani Farida su suka sa shi ɗakinki.

Baba da Inna sun tafi aikin haji. Alhaji ya biya musu. Na dawo daga wurin rakiyarsu sai Farid ya tare ni ya miƙa mini wasiƙa. A zatona a cikin abukkaina ne wata ta zo, ba ta iske ni ba ta rubuta mini wasiƙa. Na karɓi wasiƙar, na shiga ɗaki. Ga abin da wasiƙar ta ƙumsa: "Sallama zuwa gare ki masoyiyata. Ina fatan kina lafiya kamar yadda nike lafiya. Yaya zaman aurenku da ke da sakaran mijinki? Kin sa mai gubar da na ba ki jiya? In ba ki sa ba to ki yi sauri domin kar jirgin da zai kai mu Jamus ya bar mu. Mu haɗu da dare ƙarfe goma sha biyu. Na san dai lokacin nan ya yi barci. Jiya da dare da na kwana ɗakinki wallahi na ji daɗin

kwana har da mafalki. Ba don da za a gane mu ba wallahi da ba na fita. Kar ki mance mu gamu inda muka saba haɗuwa kamar kowane dare. Ni ne masoyinki mai ƙaunarki."

Na fashe da kuka yayin da na kammala karatun wasiƙar. Ƙazafin ne kuma na faɗa? Farid ya shigo ɗauke da sauran wasiƙu.

- Farida Allah ya saka mini, da abin da kike yi mini. Yanzu karuwanci kika shiga kuma? To Allah ya tona miki asiri domin a kullum in ya aiko miki wasiƙar sai ta faɗo hannun matata.


Da safe na kai ma Alhaji wasiƙun ya karanta. Ya kira Farid ya mai faɗa har da dukan shi.

Da yake ni nike gabatar da labaru sai cikin dare na zo gida. Ashe wajen ƙarfe bakwai wani yaro ya shigo ya tambaye ni Farid da Fatsuma suna cin abinci. Sai Farid ya tambayi yaron dalilin nemana yaron ya ba Farid wata wasiƙar ya ce wanda ya ba shi wasiƙar yana waje. Farid ya buɗe wasiƙar. Tana ɗauke da maganganu na soyayya ne. Ya tashi don ya ga mutumin. Da ya tsinkayi Farid sai ya tada motarshi amma Farid ya ɗauki lambar motar da kalar. Ashe duk wasiƙun ƙarya ne. Maƙwabcin "La Mama" ne da ɗiyarta Aishatu. Su suke rubuta wasiƙun. Na shigo sai na tarar akwatunana aje ƙofar ɗakina. Farid ya taso.

- Karanta ki ji wallahi kin isa mutumniyar banza. Amshi karanta. Na karɓi wasiƙar na karanta kamar haka: "Masoyiyata na gama shirye shiryena, yanzu ke nike jira, kar ki kuskura ki bar mini ɗiyata Irada. Kin san sarai da ba ɗiyar Farid ce ba. Ɗiyata ce ni na miki cikin ko? To ku zo tare ni ne mai ƙaunar ki."

- To ɗauki ɗiyarki ku bar mini gidana.

Ya janyo Irada tana barci har ta farka tana kuka ya ture ta. Sai da ta faɗi gabana. Na ɗauki Irada na goye ta na fita, akwatina a hannu. Ƙarfe ɗaya da minti uku na dare na zo bakin hanya don in ɗauki taksi. Motocin guda-guda suke wucewa. Duk wanda na tsai da ba su ma kallo na. Na yi minti ashirin a tsaye bakin hanyar ban samu mota ba. Ba ka jin komi cikin dare sai haushin karnuka. Ba ni iya zuwa gidan tanti Hawa a ƙafa saboda nisan wurin. Na yanke shawarar tafiya ɗaya-ɗaya. Na san dai kan safe na kai. Ina cikin tafiyar ne sai na ji tafiya bayana. Waiwayawar da nike sai na ga an sa ni tsaka mutum shida ɗauke da makamansu. Babban su ya matso kusa da ni.



- Kibiya kamo ta kar ta yi kururuwa. Dankunama amshi akwatin kai "da guba" ku tafi kamin mu zo.

Kibiyar ya ko rufe mini baki. Babban su ya kunce lrada ya aza ta bisa kafaɗarshi.

- Ku ko sauran ku kaita "maison blanche" ku gyara kanku ko? Allah ya ba ku.

Ya juya baya zai tafi da lrada sai na fara ƙoƙarin ƙwace kaina domin na fi son su kashe ni su bar lrada. Ina kokowa da su sai wata motar ta tsaya gabanmu. yan sanda suka yi ta dirowa. Babban ɓarayin ya yi jifa da lrada ya ce ƙafa mi na ci ban baki ba. Yan sanda suka kama mutum uku cikin ɓarayin. Babban yan sanda ya ɗauki lrada, ita kau tana ta kuka ya nufo ni ya ce.

- Madam ga ta.

Zan karɓi lrada sai muka yi ido huɗu da Ali ɗan sandan nan, abokin su Farid, abin mamaki.

- Farida? Farida ina za ki ne war haka?

Sai na fashe da kuka. Farida mi ya faru ne? Mi ya fito da ke wajen ƙarfe biyu ba minti goma.

- Za ni ... za ni ... za ni ...

Kukan ya hana ni na ba shi amsa.

Suka sa ni cikin motarsu sai gidan tanti Hawa domin ya san da su baba sun tafi ƙasa mai tsarki. Tanti ta ji tsoro da ta gan ni tare da yan sanda. Ali ya kwashe labarin inda suka gan ni ya gaya ma tanti. Na faɗi bisa cinyoyin tanti ina ta kuka. Ita ma tana kuka Riyanatu ta karɓi lrada tana rarrashin ta.

- Farida yaya aka yi ne?
- Ya koro ni ne.
- Da ma na sani.
- Ga abin da ya sa ya koro ni.

Tanti Hawa ta karanta wasiƙar da na miƙa.

- Riyanatu, tafi ki aje wasiƙar inda kika aje sauran. Farida da ma ban naɗe gadonki ba tafi ku kwanta. Ba ki komawa gidanshi, sai dai in rabuwa za mu yi da malam. Amma ba ki komawa. Shi kaɗai ne namiji? Kwantar da hankalinki za ki gan shi wata rana ya dawo yana neman ki ba dai gidan "La Mama" ba ne?

Da su baba suka dawo, Alhaji ya kwashe labarin ya gaya mashi. Baba ya yi, ya yi ya maida ni, Alhaji da tanti da Hajiya suka ƙiya. An ce sarkin yawa ya fi sarkin ƙarfi. Sai da na yi wata bakwai a gidan tanti, Farid bai ma san inda nike ba. Na shiga cikin watan haifuwata sai tanti ta ma Farid waya don ta sanar da shi ya shirya bikin sunan; ya saurare ta sannan ya aje waya. Bai ce da ita uffan ba. Ganin haka tanti ta shaida ma Alhaji. Alhaji ya kiri Farid a waya. Ya ƙi zuwa, domin gidansu ma ya bar zuwa. Daga ya je sai iyayenshi su mai faɗa, don haka ya daina zuwa gidan iyayenshi. Alhaji ya ce a ƙyale shi ya yi sunan, washe gari Farid ya ma tanti waya ya ce mata cikin ba na shi ba ne. Mu nemi wanda ya mini cikin. Tun dare bai muna ba. Haka ya gaya ma Alhaji da Hajiya.

Da safen sai ciwon naƙuda ya kama ni. Nan da nan tanti ta kai ni asibiti. Ban samu wata matsala ba wurin haifuwa. Na haifi ɗiya biyu mace da namiji. Alhaji da malam suka yi sunan. Alhaji ya ba da sunayensu: Shamsu da Shamsiya. A watan su na bakwai suna tafiya har da gudu amma har yanzu Farid bai ma san har na haifu ba. Da suka yi shekara ɗaya tanti ta shirya masu bikin zagayowar ranar haifuwarsu. Shamsiya ta fara magana. Amma Shamsu bai da yawan surutu. In ka ji ya yi magana sai in yana jin yunwa, ko in ya ga na fito daga wurin aiki ya mini sannu da zuwa. Sun yi shekara ɗaya da rabi duk a wannan lokacin ina gidan tanti. Ni da Riyanatu muna zaune cikin falo muna hira, lrada da yan tawaye da Aziz ɗan su Riyanatu da Bashir suna wasa a gefena, mu sai muka ji sallama.

- La! Zainabu, lalenki. Sannu da zuwa, lale, lale ...
- Yawwa Farida, Riyanatu ina kwana?

- Lafiya lau Zainabu. Zauna mana. Ina mijina da yarana?
- Lafiya lau Riyanatu. Irada, ku zo tantinku ta zo.

Yaran suka rugo da gudu Zainabu ta ɗauki yan tawayen, ta ɗora su bisa cinyoyinta Irada ta zauna kusan ta. Muna hira sai na kori yara da na ga Zainabu ta fara hirar aurena.

- Irada a tafi a yi wasa ko?

Suka tashi suka koma ɗakinsu.

- Yanzu Farida zaman mi kike ne haka ba aure?
- To yaya za ta yi Farid ya ƙi ba ta takardar rabuwa. Alhaji ya yi ya yi da shi ya ƙiya.
- Amma Farid bai kyauta ba. Kun san wallahi asiri ne matarshi da uwarta suka yi mashi.
- Kun san abin da nake so da ku? Ku sauya hira kuna ji? In har kuna son na zauna ba na son ku rika tado mini ciwon da na manta.

Haka dai muka yi ta hirarmu sai wani lokaci.

Allah dai ba azzalumin kowa ba ne zaman auren Farid da Fatsuma ya fara taɓarɓarewa. A da dai Fatsuma ta mallaki Farid. Bai da bakin magana, komi sai Fatsuma ta shaida mashi. Ko wurin aiki sai Fatsuma ta so yake zuwa. Albashi ma in ya ɗauko "La Mama" yake kai ma. Ita ke ba shi na kashewa da sauran su.

Aishatu da Maimuna da Salamatu suka koma ɗakina da zama. Farid ke cida su yana sayo musu kayan sawa. "La Mama" har boka ta kawo gidanta saboda Farid. Abin da duk ya samu yana hannun "La Mama" Farid, har kayan da zai sa "la Mama" take zuwa kasuwa ta sayo mashi.

Ya zamo kamar ɗan aikinsu shi ke zuwa kasuwa ya sawo kayan miya ya zo ya yi girki domin Fatsuma da yannunta suna zuwa gari ne ran futu kamar asabar da lahadi. Sai su gayyato maza su zo su cika gidan. Farid ke zuwa kasuwa ya yo sayayya ya zo ya musu girki in ya ida sai Fatsuma ta aike shi ko ta ce ya fidda katifa ya kwanta kusan maigadi. Mazan a nan suke kwana sai da safe kuma bai da bakin magana. Fatsuma gaba take sa Farid ta yi ta mai faɗa, sai ka rantse ɗanta ne. Domin sai ka ga Farid ya sunkuyar da kanshi ya durƙusa yana neman gafara. Kullum yana zaune kusan maigadi bai da izinin fita. Abin yana damun maigadin. Sai ya ce ma Farid asiri matarshi ta mashi. Da

yardar Farid, Maigadi Sule ya kawo wani malam-boka gidan Farid ba su san ba ni ma ina ta nafilfilina na roƙon Allah dare da rana, Allah ya kawo sauƙi. Aka yi katari ran nan Fatsuma ta yi balaguro, ƙaryar da ta saba yi. Domin in har mazan ba su samu zuwa ba to su Fatsuma su suke zuwa sai ta ce ma Farid balaguro za su na kwana biyu. Malam boka ya wuni yana fiddo layun da "la Mama" da ɗiyanta suka binne. Haka cikin matashin kan Farid da ƙalƙashin gadon ya fiddo layu. Ya ba Farid magungunan da zai rika wanka da sha. Bayan sati biyu Farid ya fara ganin canji. Domin tafiyar Fatsuma na damun shi. In ta fita tun da safe sai ƙarfe goma sha biyu, ko ƙarfe ɗaya na dare in ta dawo. Yau dai Farid ya gaza barci yana ta zagaye falon shi. Ya diba agogo ƙarfe ɗaya da minti shida. Ya zauna.

- Yanzu wagga macen aure ce? Tun fitar safe ƙarfe ɗaya ba ta dawo ba? Ko ni da ke namijin na kai ƙarfe goma balle ƙarfe ɗaya? Yana cikin tunanin ne, sai ya ji tsayuwar mota. Fatsuma ta shigo sanye da wando "jin" da riga shamis. Ta tanke. Lokacin da ta shiga falo take ƙoƙarin fidda su ta sa zane da riga ba ta san ba har Farid yana zaune yana kallon ta.
- Ashe Fatsuma haka kike mini? Kullum ni in ce kina gidanku ashe kina biyar maza? Yanzu fa ƙarfe ɗaya. Haba Fatsuma, a yi matar aure da sa wando da riga kamar budurwa?
- Kai bari na gaya maka ba ka isa ba ka hana ni cin duniyata. Halan ni zan zauna da namiji ɗaya? In ka ba ni kuɗin zan kai ma saurayina, masoyina madubin rayuwata.
- Haka za ki gaya mini? Ba ni makullan motata.
- Na faɗa sai kuma mi? Zancen motar ka bar shi domin na yi kyauta da ita. Na ba wanda son shi ya mini ƙululu cikin zuciyata har ya maida ta taksi. Da ita yake yawo.

Farid ya saki kanshi bisa kujera. Ya dafa kanshi. Yana zaune har safe. Da ya je ya yi salla ya ɗawo ya iske Fatsuma har ta shirya.

- Ina za ki?
- Wurin saurayina, yau bai zuwa aiki.
- Ke diba wulaƙanci ya ishe ni, kin ji ko?
- Wulaƙanci, yanzu ma ya fara. Ba ni wuri. Malam ka sani inda dare ya maka.
- Kar ki mini rishin kunya kin ji ko? In kin fita a kan aurenki.

Ta yi sowa:

- Ayyuri! Na ji baba, ba ni fita. Wai aure, yanzu kai ko ana batun aure ka ce kuna da aure? Namijin kwabo.

Farid ya tashi ya mare ta. Ta fita da kuka sai gida. "La Mama" ta aika a kirayo Farid. Bai je ba sai da dare. Farid ya yi sallama ba wanda ya amsa yana tsaye ba a ba shi wurin zama ba ya tsugunna gefe guda.

- "La Mama" ga ni. Ta yi tsaki ta kauda kai.

- Kar na sake jin ka kama sunana, maras mutunci. Ina amfaninka, kamar ka ke bugun matarka? Ba ka ko jin kunya? Tafi na rena wayonka wawan banza.

- "La Mama" mi na muku da kuke zagi na haka? Wallahi ku daina zagi na domin ko iyayena ba su zagi na haka.

Ta ɗibi ƙasa ta watsa mashi.


-Ar, kai har wani iyaye gareka? Sakaran banza maras wayo.

- Ba dai saboda Fatsuma kuke zagi na ba haka?

Yanzu fa "La Mama" da ɗiyanta suka mashi ca da bugu, sai Maimuna ta ɗora hannu biyu-biyu bisa kai ta fara kururuwa.

- Maza ku zo ku agaje mu, ɓarawo; wayyo ɓarawo!

Nan da nan mazan unguwar suka taru cikin gidan. Suka amshi Farid daga hannun su "La Mama". Aka fara tabka mashi kashi. Sai da yaron da "La Mama" ta biya don ya dinga kai wasiƙun da suka yi sanadiyar rabuwar su Farida ya ce ma mutane ba ɓarawo ba ne mijin Fatsuma ne, suka daina bugun Farid. Sai da suka bar shi kwance jikinshi duk jini, sun yayyage



rigarshi. Yaron ya taimaka ma Farid zuwa wurin motarshi. Farid ya tada motarshi zuwa gida da ya isa sai ya ma likita waya ya rika zuwa gida yana mai magani domin ya yi kwana shida a kwance. Likita zai tafi kenan "La Mama" da ɗiyanta suka shigo ko sallama babu.

- Yaya za ki shigan mini cikin ɗaki ba sallama?

- Kama muna bakinka, mutumen banza mutumen wofi. Mun zo ne don ka ba ɗiyata takardar rabuwa.

- In wannan ne ta kwana gidan sauƙi. Ya rubuta mata "saki uku" ya ba "La Mama", ta fizge takardar daga hannun Farid.

- Mayaudarin banza, maciyin amana.

- Ku, har kuna da bakin magana? Ai ku kuka ci amanata da amanar Farida sai Allah ya saka muna a kanku daga ke har Fatsuma. Na rabu da ita in na ƙara ganin wani cikin ku a gidana to ku kuka da kanku.

- Mun dai ci arziki. Ko yanzu kasuwa ta watse ɗan koli ya ci riba. Da ma abin da muka nema kenan. Arzikin ne muka nema mun same shi. Mu tafi. Don kana sakare, mun raba aurenku; da ma haushin zamanku muke ji.

Suka kwashi dariya har da guɗa. Farid ya fi dare uku ba ya barci. Bayan tunanin zamanshi da ni sai yadda ya yi ya ɓata da iyayenshi da malam, balle uwa uba tanti Hawa. Yana cikin tunanin ne sai yaron da "La Mama" take aikowa ya shigo ya gabatar da kanshi ya kwashe labarin duk ya gaya ma Farid. Shi yake rubuta wasiƙun da ake kawowa kuma shi yake kawo su. In ya rubuta wasiƙa duk jika biyar suke ba shi ƙazafi kawai suka mata. Cikin daren nan Farid kwana ya yi yana kuka yana neman mafita?

- Yanzu na ce Irada ba ɗiyata ba ce. Na kuma kori Farida da cikin. Na ce ba nawa ba ne cikin. Ko mi ta haifa?

Ya ƙara fashewa da kuka ya tashi ya shiga ɗakin don ya ga ko da kayana domin sannan ban zo na ɗauki kayana ba. Su Salamatu sun ɓata duk kayan da ke ɗakina. Ya zauna tsakar ɗaki yana ta kuka kamar wani ƙaramin yaro. Yana ta zargin kanshi da kanshi.

Washe gari ya tafi wurin aiki jikinshi a mace ya nemi hutun kwana biyar. Duk tsawon hutun yana cikin gida bai fita ba. Allah, Allah yake dare ya yi don ya gane ni na gabatar da labaru. Farkon dare bai fiddo ni ba domin na ƙara haske da kyawo. Son

kowa ƙin wanda ya rasa. Ai ba don da ya ga an rubuta suna ƙasa ba Farida Malam Musa da ba zai gane ni ba. "Yanzu Farida ta fidda ma sunana? Da in ana rubutawa sai a sa Malama Farid Farida Malam Musa. Farida na cuce ki na cuci kaina na san Farida ba za ta taɓa yafe mini abubuwan da na mata ba. Yaya zan yi na ga Irada da ɗan ko ɗiyar da ta haifa mini?"

Da ya gama kallo ya ɗauki salula kin shi ya buga waya gidan tanti Hawa. An yi katari zan wuce sai waya ta yi ƙara na ɗauka.

- Alo, alo.

Ban ji amsa ba sai Riyanatu ta fito.

- Na san dai yara ne. Sai sun bari iyayen sun fito su kama wasa da waya ko talabijin.

- Wannan duk laifin iyayen ne.

- Bari Riyanatu. Ka haifi ɗanka ka ce ya fi ƙarfinka? Ko kuma ka ce ba ka sa shi kuka. To in ba ka sa shi kuka ba kai ya sa ka kuka.

- Amma Farida kin iya tarbiya. Wallahi zaman ga da muka yi ya sa na gani yadda kike tarbiyantar da yara. Wai har su Shamsu sun san ana sallama in za a shiga ɗaki. Diyanki suna ba ni sha'awa domin kina koya masu tarbiya ta gari. Ina za ki haka?

- Gari za ni, ni da rabin raina, madubin rayuwata.

- Iye? Ahayye.

- Da ma na ce Allah ya kai mu. Allah ya sa a yi da mu wallahi komi wuyar zaman aure ya fi zaman gidan iyaye. Irada in Allah ya yarda kamar kun koma gidan ubanku. Haka kawai ke da Farid kun mayar da yara marayu. Kin ga yanzu hankalin yaranku zai kwanta.

- Ke kin san abin da nike nufi kuwa? Ni da Abdul za mu ganin yarshi.

Ta dafe ƙirjinta.

- Farida, Farida wallahi ki rufa ma kanki asiri ki san da sani, kina da igiyar aure fa, domin Farid bai ba ki takardar rabuwa ba, kuma kin san halinshi.

- To ka ji, sannu Inna. Gobe zan kai ƙararshi gidan juju domin na gaji. Ga ni da wanda zai aure ni, Abdul.

- Farida? Farid, Fa ...

- Ba ta ida zancenta ba sai Abdul ya yi sallama ya shigo.

- Hira ake ne? Ina wuninku? Cica uban karatu, yaya aiki?

- Lafiya lau Abdul, inji Riyanatu, ta tashi ta shiga ɗaki.

- Gimbiya ina wuni? Ba kya amsa mini? Mi na yi ne?

- To har ba ka san abin da ka yi ba ne?

- Sai an gaya mini.

- Karfe nawa ka ce mini?

Ya dafe kai.

- Gimbiya a mini afuwa. Wallahi kuskure na yi, gimbiya a yafe mini.

- Sai ka yi kason tsugunni sannan zan huce.

- In su Irada sun tarar da ni fa ina tsugunne?

- Ba laifi ka yi ba ne? Dole a hukunta ka ko?

Ya tsugunna ya kama kunnunwanshi.

- To ya isa, tashi mu tafi.

Ina ta mashi dariya.

Muna nan sai Farid ya ɗauki wayar. Da ya ji muryata sai ya gaza cewa komai.Ya yi jifa da salula, ya buga kanshi ga bango har sau uku. Ya daki bango, litattafan da ke cikin kwaba duk ya zubar da su. Teburin da ke tsakar kujerun ya yi jifa da shi. Ya yi jifa da kwanon tuwonshi, ya daki madubin da ke ƙofar ɗaki. Ji kake kwaram, kwatsam. Hannunshi na ta jini. Bai ma san ko madubin ya yayyanke mashi hannu ba. Kamar wanda yake hauka.Ya ɗauki kwap na ruwa ya jefa shi ga bango. Har zai sake ɗaukar wani sai Ali ya riƙe mashi hannu. Duk ya ɓata rigarshi da jini, wajen ƙoƙarin ƙwato hannuwanshi.

- Lafiya? kai Farid, lafiya? Kai ji nan!

Ya zaunar da shi, hawaye waɗansu na korar waɗansu.

- Farid? Farid ji nan, mi ya faru ne? Haba Farid da girmanka? Mi ya yi zafi haka? Kana kuka haka kamar wani ƙaramin yaro? Ko mi ya same ka ka dogara ga Allah, ka bar ma Allah zaɓi. Mi ya faru ne? Tashi mu je asibiti. Amma don Allah ka daina kuka. Tashi mu je.

Da kyar Ali ya samu ya shayo kanshi suka tafi asibiti.

Kwana uku Farid ya yi kwance a asibiti. Ali yake jinyarshi ana mai ƙarin jini. Cikin kwana uku ba ya aikin komi sai tunanina da na ɗiyanshi. Har mafarki yake yana kiran sunana.

Da suka dawo gida daga asibiti sai Farid ya umurci Ali ya kunna mashi talabijin.

- Don ka ga Farida ko? inji Ali.

Da Ali ya kunna mashi talabijin sai aka gwado wani yana labarun a harshen turanci. Yana shaida ma masu kallo cewa gwamnati ta naɗa Farida Malam Musa yar jarida, a matsayin shugaban gidan talabijin na ƙasa gaba ɗaya. Sai aka gwado ni cikin kaya tsadaddu. Zinariya ko'ina ga jikina. Sai walƙiya nake da ƙyalli. Ina ta fara'a. Ɗan jaridar ya juwo wajena yana tambaya ta a kan nauyin da aka damƙa mini na shugabacin gidan talabijin na ƙasa a matsayina na mace. Na yi dariya na gode mashi da damar da ya ba ni ta magana.

- To Majid, namiji da mace duk ɗai ne a ganina. Domin namiji ya yi karatu ne ya samu takarda, haka macen ita ma. Ni abu guda na sani shi ne shugabanci babban nauyi ne da Allah ya damƙa ma mutum kuma don ya ga ka iya ne don shi ya ba ka shi. Kuma za ni cika gurina na ɗaukaka aikin jarida a ƙasarmu.

- Malama darakta kamar ƙasar ga tamu mutanen karkara suna zargin gidan talabijin nan namu da laifin ba mu ba da labaru gamsassu kuma sauran labarun sai dai su ji su a waɗansu kafofin labaru.

- To wannan gaskiya ne domin gidan talabijin a zaman gwamnati yake. Amma yanzu mun gode ma Allah da yake yanzu cikin demokaraɗiya muke. Ma'ana kowa na da yancin faɗar albarkacin bakinshi. Kuma mai girma shugaban ƙasa ya tara yan jarida ya shaida muna da kowa na da yancin faɗin labarun da yake ɗauke da su in har ya tabbata gaskiya ne, kuma ya tabbatar da labarin yana haɗa kan yan ƙasa ne. Daga yau na ɗauki alƙawalin shaida ma yan ƙasa abin da ƙasartamu take ciki. Da ma aikin ɗan jarida shi ne labartar da ɗiyan ƙasa abin da kasarsu take ciki. Haka dai ɗan jaridar ya yi ta mini tambayoyi. Farid ya yi zugum yana kallon talabijin har Ali ya tashi za ya koma gidanshi bai da labari.

- Farid? Farid! To! Ka kurunce ne?

Ya game fuska kamar wanda aka ta da daga barci.

- Farida mi nene?

- Ali ne ba Farida ba. Zan koma gida. Farid ganin Farida ya sa ka cikin wannan halin? To ni na tafi.

Farid bai ma san ko Ali ya fita ba.

Da na fito daga gidan talabijin sai na taho gida da gudu na shiga falo. Ba kowa! Za ni shiga ɗakin tanti Hawa sai ga ta mun gamu a bakin ƙofarta muka rungume juna.

- Farida na ji daɗi. Allah ya ƙara arziki, Allah ya taimaka miki.

Riyanatu ta fito daga cikin ɗakinta.

- Lafiya? Ko za a maida ta gidan mijinta ne? Na ga fara'ar ta yi yawa. Na ji ko Farid ya gina sabon gida mai bene. Haka fa, sabon gida, sabuwar amarya.

- Riyanatu kin san tun da muke ko gardama ba mu taɓa yi ba ko? To wallahi sai mun buga, in dai ba ki bar mani irin wannan tsokanar ba.

- Ayyuri! Don za a mai da ki gidan miji. Ai ba abun kunya ba ne.

Na wuce na shiga ɗakina domin in har ta ƙara magana zan mare ta. Ina kwance bisa gadona sai Riyanatu ta turo ƙofar ɗakin ta shigota ce mani:

- Abdul yana falo.

- Ina zuwa!

Na tashi na canza kayan jikina. Na sanya wata doguwar riga baƙa mai duwatsu masu ƙyalli wadda Abdul ya fito mini da ita daga Dubai. Na tarar da shi yana raba ma su Irada biskit da bambo. Ko da na fito sai yaran suka tashi. Na gaida shi.

- Assalamu alaikum.

- Wa alaikumus salam, darakta barka! Barka!

- Barka kade. Na gode.

- Na yi farin ciki, Allah ya ƙara buɗi.

- Amin Abdul.

- A radiyo na ji... Na ce bari na tashi zama bai same ni ba. Wanga abin farin cikin ai ya kamata kar na zauna da shi. Na shirya maki wannan babbar kyautar. Amman sai da safe.

- Allah ya kai mu.

- To Farida na ce yanzu dai aski ya kawo gaban goshi. Yaya zancen aurenmu ne? Ina tsoron kar Farid ya dawo ya ce yana so a mai da aurenku.

- Ai na kai ƙararshi don ya ba ni takardar rabuwa tun jiya. Gobe za mu gaban alƙali.

- Allah ya sa mu dace Farida.

- Amin. Ka san ko lauyan ɗan abokin baba ne. Ya ce zai taimaka mini shi ma ya kai ma Farid takardar ƙarar.

Muna cikin hira ne sai baba ya shigo ba ko sallama. Gabana ya faɗi. Na san ba banza ba. Yana huci, bai ma bari mu gaida shi ba.

- Ina Hawa take ne?

Tsoro ya hana ni in ba shi amsa. Ya ƙara sawa na firgita.

Ashe tanti Hawa tana jin shi. Ta fito daga cikin ɗakinta.

- Malam lafiya? Ka amsa mini! Lafiya?

- Kin san da lafiya ba ta kawo ni gidanki saboda yar rishin mutuncin ga na zo...

Yana nuna ni da yatsarshi.

-...Yanzu Farida a ce kin tasa cikin gidan mutunci, a ji kina wannan irin munmunar tabi'a? Yaushe har za ki kai ƙarar mijinki? Jujun ya ɗaura muku aure? Wane irin tonon asiri ne wannan? Gaban dubun jama'a, a kire ku a ce za a raba muku aure, sai kowa ya san abin da ku ke ciki? Aure fa don rufin asiri Allah ya umurce mu mu yi shi. Farida a matsayinki na darakta a ji ki da mijinki kun tafi gaban juju za a raba muku aure? Haba Farida! Mine ne amfanin ilimi ba aiki da shi ba? In na ƙara jin kin tado zancen nan sai na halaka ki. Har yanzu a zaman matarshi kike fa, domin bai ce ya sake ki ba ko?

' Na sunkuyar da kaina hawaye suna ta kwarara daga idanuna.

- Da ke nake, ko ya faɗi ne? Farida kina ba ni mamaki kin yi karatun alƙur'ani, a matsayinki ta musulma kina da igiyar aure, kuma kina hira da wani wanda ba mijinki ba?! To bari na gaya miki: in na ƙara tarda ki da wani namiji to ki kuka da kanki. Amma Hawa laifinki ne wallahi.

- Na ji, na ɗauka. To shi ba ya auren takuma ya hana ta aure? Sam ba zai yiwu ba. Ban yarda ba. Shekara biyu ta yi a gida bai ɓaba ko aike ba! Kuma dibi irin ƙazafin da ya yi mata, har da cewa cikin da ta yi ba nashi ba ne. Ya kumyatar da ita, ya zubar da mutunci zuriyarmu. Allah ya saka mata a kanshi, kuma auren ta fasa.

- A'uzu billahi! Hawa a matsayinki na ...

Ta katse mashi magana.

- Ni fa babu abin da za ka gaya mani in yarda. Kawai ba ka son gaskiya. Farida tashi ki koma ɗakinki.

Na tashi na koma ɗakina ban san lokacin da Abdul ya fita daga cikin gidan ba. Bayan tafiyar baba da minti goma, tanti Hawa ta shigo ɗakina ta zauna ina kallon ɗiyana duk suna barci. Tausayinsu ya kama ni domin sun zama kamar marayu. Kai duniya! Ba su san babansu ba. Irada da dama. To su Shamsu da Shamsiya fa. Sai na tuno da wata rana muna cikin ɗaki, ni da ɗiyana, sai Irada ta mini wata tambaya da ba zan taɓa mancewa ba da ita a rayuwata:

- Mama ina babanmu? Muna da baba kuwa? Mama a maka-rantarmu kowa babanshi yake kai shi. Ni kaɗai ce mammata ke kai ni. Mama ina babanmu? Ko ya mutu ne?



- Bai mutu ba. Ya yi balaguro ne.

- Mama wasa kuke mini ko? Ai baban su Aziz da ya yi bala-guro kullum sai ya yi musu waya.

Sallamar tanti ta katse mini tunanina.

- Farida ashe Farid ya kai kwana uku yana zuwa gidan malam, wai yana son a maida aurenku.

Na ɓata rai na tashi, kamar an soke ni da allura na dafe ƙirjina.

- A yi mi tanti? Sam ba zan je ba, sai dai mu ɓata da baba ko kuma a kai gawata gidanshi. Ai abin kunya ne a ce na koma na yi zaman aure da shi bayan wulaƙancin da ya mini.

- Farida in akwai wani da ya ji ciwo bayanki yake. Amma ki ji tausayin yaranki mana kun maida su kamar marayu. Yanzu ya mini waya har kuka yake mini. Ya ba ni tausayi ba kaɗan ba. Ya yi nadama. Farida da ma haka duniya take. Sai haƙuri, na san ya yi laifi ƙwarai da gaske amma ...

Kan ta ƙare maganar har na fita waje saboda ɓacin rai. Yanzu tanti da ke mara mini baya ita ke faɗa mini waɗanga irin maganganu? Shikenan komawata gidan Farid ta tabbata. Da ma tantikawai ke goyon bayana. Yanzu da ta fara kware mini baya shi kenan. Agogon hannuna ya nuna ƙarfe goma na dare. Na fita waje na je cikin wata ma'aikatar buga waya mai zaman kanta. Na buga ma Abdul waya.

- Alo, alo.
- Alo Farida? Lafiya?
- Abdul, don Allah ka yi haƙuri da abin da ya faru ɗazu ... Ya katse mini magana.
- Farida ba komi, mi nene na kuka? Kar ki tayar mini da hankali mana. Ba komi in Allah ya ce, ke matata ce ko ana ruwa, ko ana iska sai na aure ki. In Allah ya ce ke ba rabona ne ba ce to sai mu dogara ga Allah ko? Ni yanzu abin da na gani, tunda ba ki son shi, zan kawo nawa sadaki. Ko ya ce a biya shi ne, to ni zan iya biyan shi sadakinshi.
- To ka yi sauri domin nan da kwana shida Bashir zai dawo. Na san ko ba zai yarda ba domin ko gardama ba ta taɓa shiga tsakaninsu ba. In har Farid ya shaida mashi buƙatarshi to shikenan.
- Kar ki ji komi; Allah ya sa mu dace.
- Amin Abdul.
- Ki ba ni kwana uku zan kawo sadaki da kuɗin aurenshi in har ya tambaya. Ki kwantar da hankalinki, in rabon a yi ne sai an yi. To zan bar ki a nan.
- To Abdul mu kwana lafiya.

Da na dawo, na zo na tarar da tanti Hawa da Riyanatu tsaye bakin ƙofa suna jirana. Na wuce gabansu ban ce da su komi ba.
- Farida duk kin tayar muna da hankali, ba mu san inda kika shiga ba, inji tanti.

Ta bi ni tana ta ba ni magana.

Washe gari da dare Ali ya je gidan Farid yana zaune ya gama kai da gwiwa. Ya yi sallama har sau huɗu sai da ya ƙaraso gurinshi ya girgiza shi sannan ya zabura.
- Ali ina wuni?
- Lafiya! Zauna mana.
- Ba ni zama. Za ni ɗaukar matata tunda safe ta je ma Farida hira.

Farid ya zaro idanu.
- Farida? Ina take ne? Ko jiya na tafi gidan Malam ba ta nan. Don Allah ka taimaka mini, ina son ka raka ni na gano Farida da Irada.
- To sauran fa?
- Su wa kenan?

- Su Shamsu da Shamsiya yan tawayen da Farida ta haifa. Farid ya tashi tsaye ya kamo hannun Ali. Farin ciki da mamaki ɓuka hana shi cewa komi. Ya ƙura ma Ali ido.

Yan tawaye? Tawaye ka ce fa? Allah sarki.
- Amma yanzu Farid da wane ido za ka kalli ɗiyanka? Farid ka yi babban kuskure. Shekaran jiya da muka yi hira da Farida ta ce duk wulaƙanci da ka yi mata ba wanda ya mata ciwo kamar da ka ce cikin ba naka ba ne. Da tana maimaita mini zancen har kuka ta riƙa yi. Ka san ko tawayen kai suka biyo. Kamarku ɗai da su. Balle Shamsu, kamar dai ka yi kakinshi ne.
- Don Allah Ali bari zancen da ya wuce, na san na yi laifi. Abin da za a yi shi ne ka bari mu je tare. Don Allah Ali ka taimaka mini mu je tare.
- Mu je amma wallahi ni dai ba zan yi magana ba a kan zancenku. Wannan sai ka ga tsofi.
- Na gaya ma Malam da tanti har da Bashir. Ya ce na bari har ya dawo.

Ina kwance bisa doguwar kujera mai ɗaukar mutum uku. Zainabu matar Ali da Riyanatu suna zaune. Kowa bisa manyan kujerun da suke cikin katafaren falon ɗin tanti Hawa, suna cin dambu. Muna hira, yara suna wasa gefe ɗaya sai muka ji sallamar Ali. Na tashi zaune na amsa sallamar.
- Ali shigo mana. Ali shigo!

Ali ya zauna.
- Shan ƙiba suke, Ali, irin ciye-ciye da shaye-shayen nan masu ƙara ma mace kyawo da ƙiba.
-To ita Rayyanatu saboda mijinta ya dawo ne.Zainabu ke fa? Ke mi ya kai ki shan ƙibar?
-To! Ga ni! Ai ni take ma ko? na ce ma Ali.
- Ashe? Allah sarki. To ku maida niyya.
- Ai ya kamata ke ma ki sha mana. Domin ke ma za mu maida ki gidanki ko? Kai, na yi mantuwa...

Ya tashi ya fita. Jim kaɗan sai ga shi ya dawo tare da Farid. Gabana ya faɗi ras. Yaran da suke wasa, daga shigar Farid duk suka tashi da gudu suka dabaibaye shi. Ya zo ya zauna ya ɗora yan tawayen bisa cinyoyinshi. Irada ta zauna gabanshi yana ta sumbatar su kamar yaran sun taɓa ganin shi ne, alhali ko ba su san shi ba sam. Allah kenan. Bakin ciki kamar ya kashe ni. Na

tashi a fusace, cikin hushi na je gabanshi na ɗauki yan tawaye-na. Na fara fizge lrada. Suka gama baki suna ta kuka. Na shiga da su cikin ɗakina na kuble kanmu. Sai da na fiddo masu jan ido sannan suka bar kukan.

Washe gari, da na je ɗaukar su lrada a makarantarsu, sai maigadi ya ba ni wata wasiƙa. Na buɗe sai na gane rubutun Farid ne. Wai shi ya zo ɗaukar ɗiyanshi. Haushi kamar na kashe kaina. Yaya zan yi. Ranar kuma ran laraba ce. Kenan ba zai maido su makaranta ba domin ba a zuwa makaranta laraba da marece. Sai na riƙa kuka don baƙin ciki; na ɗauki motata na koma gida. Na shiga falo ina ta kuka. Hajiya da Inna sun zo ma tanti hira, na san ko bai wuce zancen maida ni gidan Farid. Na wuce cikin ɗakina ban ko gaida su ba, hankalin tanti ya yi mummunan tashi. Ta bi ni har cikin ɗaki.

- Lafiya? Farida lafiya? Mi ya faru ne?

Sai da ta kwantar mini da hankali tana rarrashi na sa'annan na gaya mata da Farid ya zo ya tafi da yara gidanshi.

- Ap, Farida ya maida su mana. Bai zuwa da su ko'ina. Ai ɗiyanshi ne ko.

- Tanti ba ɗiyanshi ba ne. Ai shi da kanshi ya faɗa, kuma gabanku ya faɗi haka ko?

Da na tafi wurin aiki da marece tunanin su ya hana ni aiki, sai da kowa ya san da ina cikin damuwa. Har na ɗauki niyyar zuwa gidanshi amma sai na yi zaton ko yana son na je gidanshi ne don shi ya zo ya tafi da su. Ai ko na ce na je gidanshi ban san wurin



ba, domin Ali ya shaida mini da ya koma sabon gidan da ya gina. Na buga waya ma'aikatarsu har sau uku aka ce mini bai zo ba. Haba! hankalina ya tashi kar a ce ya je ya musu wani abu. Zama wurin aiki ya gagare ni. Na ɗauki motata wadda gwamnati ta mal-laka mini, na koma gida. Tanti ta yi ta ba ni magana. Na yi salla raka'a biyu na roƙi Allah ya maido mini su lafiya, kar ya je ya kashe su ko ya gudu da su. Karfe takwas na dare bai maido su ba. Abin da ke kai ni ƙofar gida shi yake maido ni cikin ɗakina. Karfe tara, ba alamarsu. Yanzu kai tanti Hawa da Riyanatu su ma sun shiga damuwa kamar ni. Kukan da nike shi ya hana tanti zama.

- Kai abin na da ban mamaki, yanzu Farida ba kuka za ki yi ba, roƙon Allah za mu yi, ya dawo da su gida lafiya. Ni ma ban san sabon gidanshi ba. Ɗazu na ma Ali waya, ba kowa a gidan, domin ba wanda ya ɗauka. Da sai ya mini kwatamcin gidan. In ya so in je in ga ko lafiya.

Na tashi na koma cikin ɗaki don na yi alwalla. Karfe tara da rabi sai na ji tsayuwar mota. Jim kaɗan sai na ji dariyar Shamsu, Riyanatu ta turo ƙofar ɗakina.

- To barkarmu, ya dawo da su.

Ta fita da gudu sai falo duk suna sanye da sabin kaya. lrada da Shamsiya duk an musu sabon kitso Shamsu kau da sabon aski. Suka tare ni da gudu. Na ɗauke su na kamo hannun lrada na shiga da su cikin ɗaki. Jim kaɗan sai tanti da Riyanatu suka riƙa shigo da kayan yara. Ni kayan ba su ishe ni kallo ba. Kowa na nuna akwatinshi kowanensu kwampile goma-goma, kuma tsa-daddu, da takalmi taki biyar-biyar. Ɗan aiki ya shigo da akwati guda ya ce na Aziz ne ɗan Bashir. Farid ya ce a shaida muna da ya mance shi ne cikin mota sai da ya je gida ya tuno da shi. Kayan da ya sa cikin na Shamsu shi ya sanya cikin akwatin Aziz. Biskit da bambo sun kai wata biyu ba su ida cinye su ba. Kamar na kunna ma kayan wuta.

- Tanti, ban yarda ba ya riƙa tafiya da su gidanshi.

- Farida, Farida! Mutum ya miki laifi, ya komo da kanshi ya nemi gafara. Mi kike so kuma? Ai ɗiyanshi ne ko?

- Kuma Farida ai laifinki ne. Domin duk abubuwan da ya miki cikin bai sani ne ba. Ke ma kin san da sun magance shi ne. Ke fa kika kawo su gidanki har suka samu damar tsubbace Farid, ko

Mama? In ba ki shaƙu da Fatsuma ba ina za su ga Farid, har su samu damar yi mashi asiri? Ke Farida duk laifinki ne ba ruwana. Ba ku san irin mutanen da kuke ja ga jiki ba.

- Riyanatu, Riyanatu ki fita daga harakata kin ji ko?
- Ai gaskiya in ta zo, sai a faɗe ta ko?

Ta tashi ta fita, tanti ta ce na ƙyale ta.

Bayan tafiyar su tanti sai Irada ta taso ta zauna gaba na.

- Mama ashe muna da baba? Ya ce bai yi balaguro ba, ku kuka hana mu zuwa wurin shi. Baba ya koma sabon gidanshi inda za mu koma. Gida mai bene. Mama ya gwada muna ɗakin-ku, da nawa, da na Shamsiya. Mu ne bisa. Shi da Shamsu ne ƙasa. Mama wallahi kamar irin gidan da ake nunowa a talabijin. Ni Mama ban taɓa ganin irin gidanan ba. Kyawo! Ko'ina madubi ne. Mama don mi muke gidan tanti? Baba ya ce in tambaye ki. Mama mu koma gidanshi mana.

- Ke kina son gaskiya? Tashi ki je ki kwanta. Ba kuna zuwa makaranta gobe ba?
- Muna zuwa.
- To zo ki kwanta.

Ƙarfe tara, waya ta yi ƙara, na ɗauka. A lokacin ina tsakar sa hannu ga waɗansu takardu.

- Alo! Ba na jin ku.
- Ni ina jin ki.
- La! Bashir! wayyo! Bashir ina kwana? Ko ina wuni ne a wajenku?
- Mu yanzu ƙarfe tara ne da minti biyu na safe. Farida don na shaida miki ne muna a kan hanyarmu ta dawowa gida. Kwana biyu ina neman ku a waya don na shaida muku, na gaza samun Nijar. Daga Faransa nake miki waya. Kenan ku tare ni a ƙarfe huɗu da rabi a filin saukar jirgi na Yamai.
- To Bashir Allah ya kawo ku lafiya. Insha Allahu, mun je.
- To zan bar ki nan. Ki gaida mini yan uwa kan na iso. Na bar ki lafiya.

Na aje wayar na nufi gida. Na tarar da Riyanatu tana shirin zuwa wurin aiki.

- Riyanatu albishirinki.
- Goro! Za a maida ki gidan Farid ne? A lalle kin isa goro. Sai ga tanti ta dawo daga cikin gari.

- Tanti albishirinku.
- Goro, mi ya faru ne?
- Sai an ba ni goro tanti.
- Zan ba ki goron.
- Bashir yana tafe, yana a kan hanyarshi ta dowowa. Yanzu ya mini waya. Riyanatu ta kwashi gudu ta shiga ɗakinta ta faɗa bisan gadon ta.
- A! Diyan yau babu ko kunyar tsofi!



Ba wuya na ɗauki motata sai gida na shaida ma Inna da baba. Ƙarfe huɗu muna filin sabkar jirgi. Mun jingina ga motar Bashir. Riyanatu ta zo da ita da yake motata tana wurin gyara. Inna ɗauke da Shamsiya. Aziz da su Irada da Shamsu suna wurin su Hajiya da su tanti da Inna. Sai ga Abdul mun koma gefe ɗaya muna hira; domin ya mini waya, aka ce da shi ina filin saukar jirgi shi kuma ya iske ni. Muna cikin hira sai ga Farid ya nufo mu. Muka yi sallama da Abdul, Farid ya game fuska da ya gane ni tare da Abdul. Na koma kusan Riyanatu, ya bi ni. Da ya muna sallama Riyanatu kaɗai ta amsa mashi ya ce zai karɓi Shamsiya na ƙiya. Na kwaɓe mai hannu.

- Mi za ka yi da dīyar mutane? Tafi ka nemi dīyarka, dīyar da ba taka ba ina ruwan ka da ɗaukar ta. Bari na gaya maka, in ka sake tafiya da su sai gidan shara'a a raba mu, domin zan kai ƙarar ka. Ina kai ina tafiya da dīyan da ba naka ba?

Duk faɗace-faɗacen da nike yi, ya kama baki yana kallo na yana dariya. Da yake ba mu da nisa da su baba, har ya ji maganganun da nike faɗi. Ya kewayo ya zo inda muke.

- Mi ya faru ne? Farid, da ku nike.

Sai Riyanatu ta amsa mashi.

- Wai ta hana shi ɗaukar Shamsiya.

- To taki ce ɗiyar? Ba shi ɗiyarshi maza kar na yi ɗaya-ɗaya da ke yanzu. Masifar da kike yi a gida ba ta ishe ki ba sai kin yi cikin taro? A san da kin iya ko?

Haushi ya sa ni kuka. Farid ya ɗauki Shamsiya duk yaran suka bi shi zuwa wurin da aka keɓe don shaƙatawa. Haushi ya hana ni ji, ya hana ni gani, har jirgin su Bashir ya sauka. Riyanatu ta tafi da gudu suka rungumi juna suna ta sumbatar junansu sai da Farid ya je wurin su.

- Kai wane irin rishin kunya ne wannan tsofi na kallon ku. Sa'annan suka saki juna, Bashir ya yi ta gaida mu da ɗaya-ɗaya. Bashir bai san ba cikin yaran wanda zai ɗauka. Abinka da yaro, kowa na son a ɗauke shi. Har su Shamsu da ba su ma san ko wane ne ba. Domin Bashir na wurin karatu lokacin da na haife su. Da muka gama gaishe-gaishe sai baba ya shiga motar Alhaji, Hajiya da Inna suka shiga motar tanti Hawa. Ni ban zo ba da mota domin tana wurin gyara. Da ma cikin ta Bashir na zo. Riyanatu take tuƙa mu ni da Shamsiya, domin su Irada da Aziz da Shamsu suna wurin Hajiya tun jiya. Farid ya jingina ga motarshi, ya ɗora Shamsiya bisa kan motarshi. Riyanatu ta shiga motarsu ta ta da lokacin nan Bashir yana wurin Farid suna zance. Na je na ɗauki Shamsiya cikin fushi. Ta yi kuka na fizge biskit kin da ke ga hannunta, na yi jifa da shi. Har zan shiga motar Bashir sai ya dakatar da ni.

- Kar na ga kin shiga motata kina ji? Ba mijinki ya zo da mota ba? To fita.

Na yanke shawarar ɗaukar taksi sai Bashir ya tilasa mini sai na shiga motar Farid. Na shiga gidan baya ina ta kuka.

- Farida ki komo gaba mana, ko kin maida ni direbanki ne?

Na yi banza da shi, da na ga motar su Bashir ta yi nisa da mu sai na ce mashi ya aje ni.

- Kai malam in kana wa sarkin da ya halice ka ka aje ni nan. Ya bushe da dariya.

- Farida ni kike ce ma malam? Don mi ba kya kama sunana? ya kamata ki mance. Abu ya rigai ya wuce ko ba hakanan ne ba. Shamsiya gaya ma mamarki. Ni ba komi daga wajena.

Yana magana yana kallo na cikin madubin motar.

- Wallahi in ba ka tsai da motar ba na fita ko motar na cikin gudu ne.

- Ki kashe kanki, a matsayinki na musulma?

Yana cikin maganar ne sai muka zo daidai magamar hanyoyi mai wuta. Sai jar wuta mai tsai da motoci ta zo. Na samu damar fita daga cikin motar. Abin ya ba Farid mamaki domin bai taɓa zaton na iya mashi haka ba. Na tsai da taksi, na shiga. Shamsiya na ta kuka, tana nuna motar babanta. Ɗan taksi ya aje ni ƙofar gidan tanti Hawa. Ina shiga, ba kowa. Da ma mun aje magana a gamu sabon gidan da Bashir ya aiko a gina mashi. Jiya a can muka wuni ni da Riyanatu da yara. Ranar nan mun wuni girki. Albarkacin dawowar Bashir mun gayyaci duk abunkanshi da matansu. Na ma Bashir wani babban abincin yan birni na barka da zuwa. Na kashe maƙudan kuɗi wurin yin shi. Kuma na yi niyyar ba shi ne da hannuna. Yanzu gaya nan wanga mutumen nan maras kunya ya zo ya rusa mini tsarina.

Na zauna cikin falo na kunna bidiyo, ina kallo. Har yanzu Shamsiya ba ta bar kukan da take yi ba. Na kwantar da ita bisa cinyoyina ina rarrashin ta, ta bar kuka.

- Mama ina zuwa wurin su Shamsu. Mama kai ni wurin su Irada.

Tana magana cikin kuka har tausayinta ya kama ni. A gaskiya na zalunce ta, da na bar ta wurin Farid ya kai ta gidan Bashir. Yanzu duk yara sun taru a can, ita kaɗai ce ba ta cikin su. To ni dai ba zan je ba. Wata zuciyar tana raya mini in kai ta bakin gidan in aje ta, in dawo. To in wani ya gane ni sai su ce sai na shiga cikin gidan. Ni ko ba komi ba ya sa ba na son na je, illa sai don Farid yana a wurin. Ni ko na tsane shi. In na gane shi kamar na kama da wuta don baƙin ciki.

Na tashi na shiga ɗaki na ɗauko mata kayan wasarta, da bambo, don ta daina kukan. Na bar ta kwance bisa kujera. Na sa kamar minti takwas kafin na samu ɗiyar robarta wadda ta fi so duk cikin kayan wasanta. Na dawo falo, ban tarar da ita ba. Na ƙwala mata kira ban ji ta ansa ba. Na fita waje, ba ta nan, duk ɗakuna a kuble suke. Sai nawa da na buɗe ɗazu. Na dawo cikin falo hankalina cikin mummunan tashi. Na kalli inda na bar ta kwance. Sai na ga wata takarda, na ɗauka sai na shaida rubutun

Farid ne ya shaida mini da shi ya zo ya tafi da ɗiyarshi domin abukkanta suna neman ta.

"Amma wallahi bai san kunya ba, wai har da cewa ɗiyarshi. Kai da nan ka ce na nemi wanda ya mini cikin domin kai ba naka ba ne."

Yaya aka yi ban ji tsayuwar motarshi ba? Ƙarfe bakwai na dare tanti ta dawo ta shaida mini Bashir ya ce a bar yara su kwana a gidanshi. Ta ce kuma abukkaina suna ta tambaya ta. Farid ya shaida musu da wai wani aiki na gaugawa na tafi yi. Na yi tsaki.

- Ina ruwanshi da ni har da shirya ƙarya a kaina. Tanti, don yana a wurin ne ban je ba. Tanti! Ba na son shi, ba na son mai son shi. Tanti, yanda kuke ƙyamar jini ya taɓa muku fararen kayan nan naku, haka nike ƙyamar shi. Tanti ba na ƙaunar shi yau, ba na ƙaunar shi gobe, kuma ba na ƙaunar mai ƙaunar shi. Kazafin da ya mini, na bar shi da Allah. Kuma sai Allah ya saka mini. Tanti ta yi zugum tana sauraro na.

- Kin ida? Ina tsoro ki koma "da na sani". In ba ki son mutum kar ki yi mashi baki mana. Kuma kar ki mance da uban ɗiyanki ne fa? Kuma ko ba ki son shi don mi za ki ce baki son mai son shi?

Har zan buɗe baki na yi magana ta tare ni.

- Ina magana kina yi ko? Rishin kunya za ki mini kuma? Zan tafi wurin kan amarya. Kin je ma wurin auren ɗiyar Habsatu kuwa?

- Na je. Dazu har tana muku waya ma.Ta ce ku je tana son ganin ku.

- To, na tafi.

- A dawo lafiya.

Ƙarfe goma ina kallon wani film wai shi "Alatumi", labarin wata yarinya Wasila ɗiyar wani mai hannu da shuni wadda iyayenta suka mutu suka bar mata gado. To, Juma ƙaunar uban Wasila wadda suke uba ɗaya, ta mamaye dukiyar Wasila. Ta kuma aurar da ita ga wani saurayi mai sai da goro. Abin tausayi, har hawaye ya riƙa zubo mini. Sai na ji gidan ya mini girma. Ba yara, ba war na goge fuskata. Ba jikkar hannuna. Na duba ko'ina cikin Riyanatu, ba tanti. Na tashi na shiga ɗaki don na ɗauko mushu-ɗaki ban gan ta ba. Na koma cikin falo ba komi. Na buga ma Riyanatu waya, in ji ko cikin motarsu na bar ta.

- Bari, Bashir zai je ya duba maki, kwantar da hankalinki, inji ta.

- Ina na ga kwanciyar hankali duk takarduna suna ciki? Makullan gidan talabijin da na motata duk suna ciki. Kai Riyanatu ba abin da babu ciki. Duk kayan amfanina suna ciki.

Bashir ya dawo ya ce ba komi cikin motarshi. Ba na gaya miki ba lokacin da kika ɗauki Shamsiya daga wurin Farid tana sarka-fe gare ta.

- To sai da safe.

Da na aje waya sai na tuna,da kyar in ba cikin taksi na mance ta ba. Domin a lokacin, kukan Shamsiya ya tayar mini da hanka-li. Na buga waya a tashoshin radiyo masu zaman kansu ko ba a kawo waƙa ɓakar jikkar hannu da aka manta ba. Suka ce ba a kawo ba. Na sa a mini cigiya.

Ƙarfe goma sha ɗaya da rabi na dare tanti ba ta dawo ba. Na rufe ƙofofin ɗaki, na kashe wuta, zan yi shirin shiga barci. Sai na ji ana ƙwanƙwasa ƙofa. Na yi mamaki domin tanti tana da makul-lan kanta. To wane ne? Ko Abdul ne? To Abdul bai taɓa zowa warhaka ƙarfe goma sha ɗaya ba. Na sanya rigar barcina fara sal. Ban ɗauki mayafi ba. Gashin kaina ya zubo har a gadon baya. Har na so na ɗaure shi sai na bari. Na fita na kunna wutar falo na buɗe ƙofar, cikin fargaba da tsoro. Sai na ga Farid tsaye a ƙofa. Baƙin ciki da haushinshi ya kama ni. Ya ƙura mini ido har tsawon minti biyar.

- Malam lafiya?

Ya mini murmushi. Na turo ƙofar zan rufe sai shi ma ya ture ƙofar ya shiga.

- Ba ki isa ki hana ni shiga gidan tanti ba. Jikkarki na kawo miki. Sanarwa na ji cikin radiyo.

Na je na amso jikkata, ya kama mini hannu yana dariya. Na fizge hannuna na wuce.

- Farida akwai baƙin rai! inji shi yana dariya.

- Ba ni jikkata. Kuma ka fita. Kar na tara maka jama'a.Yanzu zan yi "ihu kwarto". Ya fashe da dariya.

- Farida kenan! Ai in kika ce ma wani namiji kwarto, gaskiya ne domin ba namijin da zai gan ki yanzu ya kasa cewa zai aure ki. Amma ni da matata za a ce mini kwarto? A unguwar ga ba wanda bai san da ni ne mijinki ba. In kin ce ɓarawo da dama. Ko wannan ma in suka iske ni haka ba a yi zaton ni ɓarawo ne ba.

Ga ni yaro kyakkyauwa, son kowa ƙin wanda ya rasa. Farid mijin Farida. Iye! Don Allah, ki yi mini irin murmurshin da kika saba mini, irin mai kwantar mini da hankali.

"To, Farid ko hauka ya yi? Ba dai har ya mance da makircin da ya mini ba." Na wuce na bar shi tsaye cikin falo.

Kwana biyu bayan dawowar Bashir, Abdul ya iske ni wurin aiki ya ce ya aika ƙanen babanshi da abokinshi neman aure na. Kar ki so ki gani yanda nike murna. Na koma gida na yi nafila don na roƙi Allah, baba ya karɓi sadakin. Karfe takwas da minti ashirin da biyu, na ji tsayuwar motoci uku a ƙofar gidanmu. Na yi zaton su Abdul ne da yan gidansu domin duk ƙarshen sati sai sun zo gani na. Na tashi da sauri na sa kaya a jikina domin na fito daga wanka ne. Sai na ji muryar baba ya ce: "Ba ta ma nan? To a kirayo ta." Gabana ya faɗi ras, ni da Bashir muka gamu ƙofar ɗaki. Ya game fuska kamar an aiko mashi da mutuwa. Na san da ba lafiya. Ina bin shi baya har cikin falo. Na iske baba da Alhaji da Hajiya da Farid da tanti. Na durƙusa na gaida su cikin ladabi da biyayya. Hajiya da Alhaji kaɗai suka ansa mani. Na zauna gefe ɗaya. Na sunkuyar da kai. Ba ni ma son mu gama ido da baba. Baba ya yi gyaran murya, tazbinshi a hannu yana ja a hankali.

- Yanzu Farida ba ki tsoron gamuwarki da wanda ya halice ki ko? Yanzu duk karatun da kika yi kin jefa shi a ruwa? Farida kin yi imani da Allah kuwa? Kin kaɗaitar da Allah guda ne kuwa? Haba Farida a ce kin fito daga gida mai mutunci kuma kina tabi'o'in arna? Yaushe aka taɓa gani? Kina da aure za ki ce ma wani ya kawo sadakinshi? Raba ki biyu zan yi ne? Ni ba ki isa ki zubar mini da mutunci ba. A matsayina na musulmi ba za a tabka irin wannan ta'asar a gidana ba! Wannan ai bala'i ne. Farida ina kika taɓa ji an ɗaura aure a kan aure?

- Baba, Farida ba ta da hankali ne.Idan ma kun samu saɓani tsakaninki da mijinki, ina ke ina yin wani saurayi? Wannan duk zubar da mutunci ne, inji Bashir.

In ba kuka ba, babu abin da nike yi. Wai yanzu ni aka ɗora ma laifi, kowa na faɗin albarkacin bakinshi. Alhaji ya dakatar da su.

- Wai kun zo gyara aure ne, ko kunzo ɓata shi ne? Malam, don Allah abin da Farid ya yi, mai mutunci ya yi shi? Duba fa malam baranyar matarshi ya aura kuma bai ma sanar da matar



ba. Mu muka matsa mashi ya sanar da ita. Nan fa ya kama ba ta kashi har ta yi ɓarin ciki. Malam gabanka ya ce cikin da ke ga Farida ba nashi ba ne. Har ƙin yin suna ma ya yi. Ba ni da kai muka yi sunan ba? To malam kawai a raba auren. Kawai bai dace su yi zaman aure ba. Ina sadakin Abdul? Farida ki ce ma Abdul ya turo magabatanshi gobe na ɗaura muku aure.

Haba! Farid ya tashi tsaye ya kama hannun baba.

- Baba ka yi magana mana!...

Ya koma wurin tanti ya sunkuya gabanta.

-...Tanti ku sa bakinku don Allah!

Alhaji ya tashi zai fita baba ya kirayo shi ya zaunar da shi.

- Alhaji kar ka maida kanka kamar wanda bai san komi ba mana. Na san Farid ya yi babban kuskure amma ba a yin saurin ba mace gaskiya gaban namiji, in ba bincike aka yi ba aka gano gaskiyar. Kuma zancen rabuwa bai ma taso ba. Yanzu za a sasanta ne a maida musu aurensu.

Baba ya yi sanyi. Da Alhaji ya tuno mashi wulaƙancin da Farid ya mini, kamar an zuba mini wuta. Na tashi tsaye.

- Baba wallahi ni ba na son auren, kuma ba na zuwa, sai dai in gawata za ku kai.

Kan na ƙare magana Bashir ya share ni da mari. Na je zan faɗi sai Farid ya yi tsalle ya taro ni. Nan da nan lumfashina ya ɗauke tsawon minti uku sai da suka zuba mini ruwan sanyi sannan na falfaɗo. Tanti ta zaunar da ni kusanta, ina shasshekar kuka.

- To, da ka kashe ta saboda wanda bai ma san ana yi ba.

Farid fa gaba da mu ma ya koma, gida ma ya daina zuwa. Yanzu da ya rabu da Fatsuma zai komo ya ce yana son ta. Gobe kuma in matarshi ta koma, wulaƙancin ya komo ko?!

Farid ya matso wurin Alhaji.

- Alhaji wallahi wannan ma ƙaddara ce. Na san na yi kuskure. Shi ne na fari kuma shi ne na ƙarshe, insha Allahu. Kuma kun san da magani ...

- Rufe mani bakinka mutumen banza. Kai da kanka ka san can da fari Farida ba ta son ka, domin tana da wanda yake son ta. Umurnin iyaye ta bi ta yarda aka ɗaura muku aure. Mun ƙunta-ta mata, Farida sai ki yafe mana.

- Alhaji don Allah ka bar tado abubuwan da suka wuce. Lattijo don gyara ake son shi ba ɓatawa ba. Yanzu kana faɗin haka sai ta ƙara ƙin yarda kuma.

- Kar ta yarda ta gani mana! inji Bashir.

- Kai wai kana lafiya kuwa? Taɓa ta ka gani. Wane irin rishin kunya ne gare ku kai da Farid. Ba ka jin kunya kana bugun ta gaban mu? Sake bugun ta in gani. Kai ku ma tashi ku fita maza! Na ce ku fita maza! Ko ba ku ji na ne?

- Bar su Alhaji. Kai ku zauna, inji baba. Alhaji abin da nike so yanzu a bar ɗauko zancen da ya wuce. Mu ma Farida gargaɗi, ta san irin abukkan da za ta yi. Mu ma Farid gargaɗi shi kuwa, ko zai yi aure kar da ya wulaƙantar da uwargidanshi. Hajiya da Hawa ku maida ta gidanta.

Sun yi awa guda suna bayani amma ni ban san abin da suka faɗa ba. Na ga dai sun shafa fatiya. Tanti da Hajiya suka shiga ɗakina. Nan da nan suka tattaro kayana. Farid da Bashir da Ali suka dinga ɗebo kayana suna sanya su cikin motar Farid, wata mota wai ita Pajero, mai launin baƙi. Tanti ta kamo hannuna, ta ta da ni, na tashi na bi ta. Ba su san niyyar da na ɗauka ba. Na san in ban koma gidan Farid ba zan ɓata da iyayena. To zan je amma ba a zaman matarshi ba. Tun daren nan zan fara gallaza mashi masifa. Na shiga motarshi ni da Hajiya a gidan baya Farid yana jan motar,har unguwar. Da yake, unguwa ce da ta fi duk unguwannin da ke birnin Yamai gidaje na gani a faɗa, wutar lan-tarki ko'ina. Sai ka yi zaton safe ne ba dare ba.

Gidan Farid gida ne wanda zan ce ba kamarshi a unguwar, duk da yake akwai gidajen da suka fi shi girma da bene. Domin

nashi hawa ɗaya ne. Karo fari aka liƙa ma gidan kambacin pan-tir, sai walƙiya! Muka shiga gidan, amma sai an danna ƙaraura-wa wanda ke cikin ɗaki ya zo ya buɗe ƙofar. Muka zauna cikin falon ƙas, jim kaɗan sai ya umurce mu mu hau bene. Shi ne ɗakina. Na bi su tanti muka hau. Na yi mamakin ganin yadda aka shirya falon. Kujerun ma wani abin a zo a gani ne. Sai ka ce don ado ne aka yi su, ba don zama ba. Kujeru huɗu da babbarsu mai ɗaukar mutum huɗu kamar gadon barci da teburinsu a tsakar su. Bayan kujerun, wani teburin cin abinci ne da kujeru shida kewaye da shi. Mayafin bangon, bula ne, ko'ina manyan hotuna, nawa da nashi, a kafe ga bango. Ɗakin barci uku da gwadala da kuma mangaza. Ga wani babban talabijin bisa teburinshi haɗe da bidiyo da ma'ajin faya-fayi.

Muka zauna cikin falon. Su tanti na ta mini nasiha. Amma ni ina a kan bakana. Tanti ta shiga da ni cikin ɗakina. Abin ya ba ni mama-ki, domin ba tsofin kayan ɗakina ko ɗaya, duk sabi ne: da gadon, da armuwar da kuwafez, da kujerun, da teburin, duk kala ɗaya ne; Har mayafin bango ruwan bula ne. Mutum huɗu na iya barci bisa gadon, ba su gogu ga juna ba. Har mamakin Farid na riƙa yi. Yaya mutum zai iya kashe waɗanga irin maƙudan kuɗi haka?

Bayan tafiyar su tanti na zauna bakin gado, tunanin Abdul ya riƙa zo mini. Tausayinshi ya kama ni, hawaye suka zubo mini. Yanzu ina yake? Yaya zai yi in har ya ji na koma gidan Farid? Sau biyu kenan Farid yake sa ni cin amana. Haka ya hana ni auren Idris wanda nike so kamar na mutu. Wanda ranshi kaɗai ne bai ba ni ba. Ga kuma Abdul. Kai duk wannan ai laifina ne.

Farid da Ali da Bashir suka shigo. Haushi ya daɗa kama ni. Bashir ya zo ya tsaya gabana. Na yi zaton bugu na zai yi. Na zabura na tashi cikin tsoro.

- Kai, kar ka firgitar mini da mata.

Farid ya ture shi cikin wasa.

- Farida, ki yafe mini da marin da na miki inji Bashir; wallahi cikin ban sani ne ba. Kuma don baba yana magana ne kina maida mashi gaban mutane. Ai bai kamata ba. Marin ba don ba na son ki ne ba. A'a don na sa ki ga hanya ne.

Bashir kamar ya yi kuka domin na ba shi tausayi. Ya sunkuyar da kanshi tsawon minti biyu. Sai ya fita bai ma yi sallama da mu ba. Ali yana wasa da makullan motarshi.

- Farida, kukan ya isa hakanan haba. Duba har kin sa Bashir kuka. To Farid ni ma zan bar ku domin ku ci gaba da amarcinku. Farid yaya za ka ci riba biyu-biyu haka? Ga sabon gida ga sabuwar amarya. To sai sati biyu.

- Balaguro za ka yi ne? Inji Farid.

- Kai dai ne za ka balaguro. Na san dai Farida ba ta barin ka ka fita yawo balle ma ka ɗauki hutun wata ɗaya. Kana harare na, ba gaskiya ba ne? Tuno da lokacin da kuka yi aure, sai in ni da Bashir mun zo ganin ka. Amma kai ba ka zuwa gidajen mu, daga gida sai aiki. Shi ma don ya kama dole.

- Ka gama? To jeka na raka ka.

Ina ta zagayen ɗakin ina kuka. Na jingina ga bango idanuna suka koma kamar garwashin wuta duk sun kumbura. Hawaye da ke kwararo ga idanuna suka hana ni gani. Ashe Farid ya shiga ɗakin, ɗauke da abinci ya zo ya tsaya gabana ya kama hannuwana.

- Farida daina kuka mana. Don Allah kukan ya isa haka nan zo ki zauna ga abinci nan na kawo miki.

Yana magana cikin murya mai kwantar da hankali.

Ban san lokacin da na fizge hannuwana ba don haushi. Na ture shi ya faɗi bisa gado. Kamar na dira bisa shi,na mafure shi har ya mutu. Domin a wannan lokacin ba na son ganin shi gabana.

- An ce maka ni yar yunwa ce? Na san irinmu talakawa ne. Amna ba ma saida mutuncinmu don talauci.

Ya kama baki yana mamaki na domin ban taɓa tsayawa gabanshi in faɗa mashi baƙaƙen maganganu haka ba.

- Malam ka dube ni da kyau, ni ba yar yunwa ba ce. Kuma abu ɗaya zan gaya maka fita daga harakata. In har ka ƙiya, na tona ma asiri, kana ji na? In ba ƙaddara ba mi zai sa na aure ka? yanzu don Allah kai namiji ne? Allah, mi na maka da za ka sa ni zama da ajali.

- Yanzu Farida ni kike zagi haka? Ba kunya ba tsoron Allah! Ni ne fa Farida!

- An zaga, sai kuma mi? Kai wa? Kai ja ba mutane wuri. kai duba, surutunka ya ishe ni hakanan. Fita ka ba ni wuri, ko ni na fita.

- Ya yi dariya ya girgiza kai.

- Yi zamanki, ni zan fita. Farida yanzu ni za ki wa korar kare?

- Kaɗan ka gani. Kunnuwan ne, jakan na baya. Ina amfanin zaman aure da kai? Kai da kanka, ka san umurnin iyaye na bi in ba haka ba ka san sarai da ba na son ka domin ina da masoyina: ka san Idris, ka san kuma Abdul.

Duk maganganun da nike ta faɗi sai wannan kawai ta masa ciwo. Ya ɓata rai, duk kamanninsa suka canza cikin gajeren lokaci.

- Farida? Farida!

- Mi? Ba na son ka, ba na son mai son ka.Ba na ƙaunar ka yau, ba na ƙaunar ka gobe. Ka fita zuciyata sam.

Farid da ke tsaye, sai da ya koma zaune. Ya dafe kai saboda abin da bai taɓa ji cikin kunnuwanshi ba.Na wuce zan fita sai ya kama hannuna.

- Zo ki zauna.

Na tafi.

Ya fita ya bar ni. Daran nan daga ni har shi ba mu yi barci ba. Shi dai baƙaƙen maganganun da na yi ta watso mashi suka hana shi barci. Ni kuma baƙin cikin komowa gidanshi. Raina ya yi mummunan ɓaci. Kuma na ɗau alƙawarin gallaza mashi masifa sai ya sake ni.

Da gari ya waye har na ɗau aniyar ba ni wanka gidanshi; sai na daure na yi wanka, don na samu na yi salla. Na shirya tsap ina cikin shafa jan baki,Irada ta turo ƙofar ɗakina ta shiga ta durƙusa ta gaida ni na amsa mata.

- Mama wai ku zo mu karya kumallo in ji baba. Lokaci ya yi kar mu makara zuwa makaranta.

- Ku tafi ku fara ci kamin in gama shiryawa.

- To Mama.

Ta fita da gudu. Na yi tsaki: wa zai ci abincin gidanka? Allah ya kiyaye mini. Da na gama shirina na fesa turare na ɗauki jikkata na rataya ina takawa ɗaya-ɗaya na sauka ƙasa. Da yake matattakarar benen cikin falon Farid take sai na tarar da su suna karin safe. Da Farid ya gane ni sai ya tashi ya gyara ƙujera a zatonshi na fito ne don mu karya. Sai kawai na wuce, ko kallon inda suke ban yi ba. Ya tashi ya bi ni da gudu.

- Farida, Farida ji mana. Farida don Allah to bari na ɗauko motata na kai ki; ba motarki tana wurin gyara ba?

Bai ma ishe ni kallo ba na yi tsaki na wuce shi. Na fita ƙofar gida yana biye da ni, yana ta maganganunshi. Ban san abin da yake faɗi ba domin ba ni sauraren shi. Na tsai da taksi na shiga, ya yi tsaye yana kallo na har taksi ta ɓace mashi. Haka dai na yi ta gallaza mashi har tsawon wata biyu. Tun da safe in na je wurin aiki sai barcin dare ke maido ni gidanshi. Wurin aiki nake wuni sai ƙarfe goma ko goma sha ɗaya na dare in na shigo gida.

Na shigo falo na gamu da shi za shi ya shimfiɗe Shamsiya domin tare muke da ita da Irada a bisan bene. Ɗakin barcinsu na kallon nawa. Farid da Shamsu kuwa a ɗakunan ƙasa suke barci. Ya kalle ni sama da ƙasa ya kalli agogon bango ƙarfe goma sha ɗaya har da minti bakwai tun fitar safe.

- Haba Farida in ba ki mini, ki ji tausayin yayanki mana yanzu ko abincin na ba su sai su ce ba su ci in ba ki zo ba.

Yana ta magana na yi banza da shi ina ƙoƙarin buɗe ƙofar ɗakina.

- Ashe ka san ɗiyana ne ko? To ƙyale ni da su.

- Farida don Allah abin da ya riga ya wuce a bar shi ya wuce. Wai ina kike wuni ne?

- Gidan wanda yake ƙaunata, Idris masoyina.

Da na faɗi haka sai da Shamsiya ta sulluɓe, da kaɗan ta faɗi, ya yi sauri ya caɓe ta. Na shiga ɗakina na buga ƙofar. Ji kake gam! Na ji wani dadi domin na fara faɗin abin da zai tayar mashi da hankali don na san shi da masifar kishi.

Bayan wata biyu da komowa na shirya za ni wurin biki tun da sanyin safe don in samu fatiyar sunan. Da yake ranar asabar ne Farid na gida na gamu da shi cikin falonshi ya fito daga cikin ɗakinshi, ga alamu daga wanka ya fito, yana ɗaure da sarbeti yana shartar kanshi, ya tari gabana.

- Farida ina za ki bayan na rigai na sanar da ke da za ni yin baƙi daga Sanagal? Kin san ko tun satin da ya gabata na shaida miki.

Na kalle shi na watsar, kallon wulaƙanci.

- Ba ka isa ba, kai wa? Na yi tsaki na ɗan ja da baya.

- Inda za ni kake so ka ji? To gidan Abdul za ni, ka san in na yi sati ɗaya gidan Idris, sati ɗaya gidan Abdul nake yin shi. Kar ma ka sa rai zan dawo. Yau wata yar tafiya za mu yi ni da Abdul. Ka san yau asabar, za mu je mu yi hutun ƙarshen sati.

So na yi ya ce mini "in kin je a kan aurenki", ko ya shiga ɗaki ya rubuta mini takardar saki.

- Malam in ba ta maka dadi ba, ba ni takarda kawai.

Ya buga kanshi ga bango har sau uku. Na wuce na bar shi na shiga mota, na ta da, har zan ɗaga sai ya ƙwala mini kira, muryarshi na rawa kamar mai kuka. Har na so na tsaya sai na ɗaga. Ina kallon shi ta madubin mota. Ya ruga da gudu ya bi motata sai talalaɓiya ta ɗauke shi ya faɗi rim, domin ba a yi minti biyar ba da maigadi ya ba furannin gidan ruwa. Na ɗaga motata sai na ƙara gudu. Na ji duk abubuwan da nake ma Farid don kawai ya ji haushi ne har ya yi fushi ya ba ni takardar saki.

Da na fito daga wurin bikin sai kawai na doshi gidan Umu gorata don kawai kar da na dawo gida da wuri. Don Farid ya ɗauka da gaskiya ne gidan tsofin samarina nake zuwa. Na kusa cim ma gurina domin Farid ya fara ɗauka gaskiya ne. A haƙiƙanin gaskiya, tun dawowata daga gidan Farid, sau ɗaya Abdul ya mini waya, shi ko ba mu yi ba wata doguwar hira, kawai barka dai ya yi mini da na koma gidan mijina. Idris kuwa ba ni da labarinshi, na ma mance da shi. Zolayar Farid kawai nake yi. Domin ba ni yarda in shaƙu da wani namiji wanda ba mijina ba.

Ƙarfe goma sha biyun dare, na shigo gida. Ina cikin gari don kar na zauna gida balle ma har in ma baƙinshi girki, wata ƙila rashin zamana wurin baƙinshi ya ɓata mashi rai ya rabu da ni. Shekaran jiya jikka ɗari ya bani don na yi ma baƙinshi girki.Na karɓi kuɗin kuma na fita. Yanzu da zaran na shigo zan mayar masa da kuɗinsa. Na tura ƙofar falon, na tsaya ina kallon jama'ar da ke cikin falon. Baƙin sun kai goma sha biyar har sun fara cin abinci. Ban san ba a ina ya samo abincin. Ya tashi ya tare ni ya rungume ni kamar ba shi nake ta gallaza ma ba. Baƙin ciki, kamar na bankaɗe shi. Sai wata zuciya ta ce mini na ƙyale shi domin na ga shi da nake ta ma wulaƙanci ya ɓoye faɗanmu, ya kalle ni yana ta fara'a.

- Abin ƙaunata, na yi zaton za ku kwana ne a can sai da saka-tariyarki ta buga mini waya, ta ce jirginku ya sauka. Amma don Allah ki yi haƙuri saboda ban samu damar zuwa ɗaukar ki ba.

Ashe ƙarya ya ma baƙinshi: da suka tambaye shi ina nake sai ya ce musu na je wurin taro ƙasar Togo. Ya juyo ga baƙin da ke abinci ya yi taɓi don jawo hankalinsu wajenshi.

- Ku ba ni hankalinku minti ɗaya. Jama'a ga uwargida Farida madubin rayuwata. Ita ce darakta ta gidan talabijin na ƙasa.

Sai baƙi suka ɗauki taɓi. Bayan mun gaisa da baƙin, sai Farid ya ɗauko mini abinci da lemun kwalba. Lemun dai na ɗan kurɓa na aje, shi ko don mutane suna kallon mu na sha shi. Haushi kamar zuciyata ta fashe. Na yi ta mashi hira don kar mutane su gane da ba mu shiri domin tun da na shigo yawancin baƙin duk sun maida hankalinsu gare mu, muna hira. Muna dariya kamar ba mu taɓa ɓata ma junanmu rai ba.

Sai daran nan na san da ashe gidanmu har da kamera wanda idan kana daga metir ɗari shida a kowane ɓangare na gidan, wanda ke cikin falon Farid zai gan ka. Domin, lokacin da muke hira na ga Farid ya tashi ya ma maigadi waya: ga wani ɗauke da kwalaben lemun kwalba a bar shi ya shigo. Sai na kalli inda yake kallo, na ga kamara. Don shi ne duk lokacin da na shigo zan tarar da shi zaune cikin falonshi yana jira na. "To mi ya sa haka?" ina tambayar kaina.Ga kamera gidanshi kuma yan sanda suke tsare da gidan? Haka kuma, Farid ko'ina yake yan sanda suna tare da shi.

Bayan minti talatin duk baƙin sun koma masabkinsu. Da muka raka su na dawo cikin gidan, yana bi na har da gudu-gudu, yana kira na.Na yi banza da shi. Ya bi ni har ƙofar ɗakina, ya kama hannuna yayin da nike ƙoƙarin buɗe ɗakina.

- Farida ina son ki mini alfarma ɗaya. Don Allah Farida ina son magana da ke ko da ta minti biyar. Farida ki saurare ni don Allah.

Idanunshi suka cika da hawaye. Na buɗe ɗakina ban tsaya sauraren shi ba, na shiga na turo ƙofar na kuble kaina. Ina jin shi yana ta bubbuga ƙofata na yi banza da shi na shiga wurin wanka na watsa ruwa, na fito na shiga gabatar da nafilolina. Na kwanta, barci ya gagare ni. Har na yi niyyar zuwa ɗakinshi sai tunanin abubuwan da ya mini ya fara yawo gabana sai na tuno da wani dare na kammala sallar nafila, ina jan tazbi, sai Farid ya shigo ɗakina ya mini sallama, na amsa mashi ya ce na tarar da shi ɗakinshi. Na yi kamar kar da na je domin na san halin Fatsuma, ba ta rabuwa da ɗakin barcin Farid. Na yi tsoron kar dai a ce wani makirci suka shirya mini. Sai na dibi muhimmancin bukatar miji a wurin matarshi, sai na saka rigar barci na nufi ɗakin barcinshi na tarar da shi kwance bisa gado. Ya umurce ni na zo na kwanta. Na

zauna bakin gado; ya tashi zaune ya jayo ni, yana ta rarrashi na.Cikin maganganun da yake faɗa, ban riƙe ko ɗaya ba. Mun fara hirarmu da wasarmu irin ta mata da miji sai ga Fatsuma ta shiga ɗakin, zindir haifuwar uwarta. Ta kunna wutar lantarki. Sai kawai na kama, Farid ya ture ni. Fatsuma ta sa Farid ya karɓi girkin daga hannuna. Wata tara rabo na da girki. Farid ya kuma hana ni na shigo cikin gida ta falo. Ya ce wai in dinga bi ƙofar baya.

- Farid cin amana za ka nuna mini a fili? Ina kai ina kawo ta ɗakinmu, har bisa gadona? inji Fatsuma. Farid ba kunya ba tsoron Allah, kawai ya ture ni na faɗi ƙasa.

- Tashi maza koma gidanku. Na yi ta korar ta ta ki fita. Don shi ne na bar ta, ki zo ki gani da idonki; yake ce ma Fatsuma. Tashi fita munafukar banza. So dole ne? Ki koma gidanku mana; yake ce mani da ya juyo gare ni. Na tashi na fita da kunyata.

Bayan na gama wannan tunani, sai na yi ajiyar zuciya: wai shi ne yanzu zai mini kukan ƙarya. An ce in maye ya manta, to mai ɗa shi ba zai manta ba. Na shiga bargona na yi barci.

Har na yi wata shida muna haka. Na ga Farid bai da aniyar sakina duk da ba na shan ko ruwan gidanshi. A zatona ya faɗa ma iyayena ko iyayenshi ashe ba haka ba. Hatta da Bashir da suke raba fara ɗaya da shi bai san irin zaman da muke ciki ba. Ya kamata na sake dubara. Ina cikin saƙe-saƙen hanyoyin da zan bi sai kwatsam Farid ya shigo falona.

- Gimbiya hutawa ake? Yara suka shaida mini da kina gida, injin dai lafiya da ba ki je aiki ba?

Na tashi tsaye cikin baƙin rai.

- Kai, ka dibe ni da kyau, ka san da ruwa ba sa'an kwando ba ne ko? To wallahi tsuntsayenka su kiyayi gonata kana ji? In ba ƙaddara ba ina ni ina auren ka, maye, bawa?

Ya yi dariya har ya zauna a ƙasa.

- Amma Farida kina ba ni mamaki.In ni maye ne da ke zan fara handama. Kuma ai an yi bauta tun lokacin Manzon Allah. Yanzu Farida na gane, ashe duk abubuwan da kike mini don na sake ki ne, to na ki. Yarinya kwantar da hankalinki ba na sakin ki. Zama da ke ko yanzu na fara sai illa masha allahu, sai in na mutu ko kin mutu. Farida ban aure ki don na sake ki ba. Na yi bincike daga Idris har Abdul ba wanda ke ƙasar nan don

kawai ki ɓata mini rai ne ko? Bari na gaya miki zage-zage da kike mini su suke ƙara mini ƙaunarki a zuciyata. Farida uwargidan Farid Allah ya bar mu tare, mu ci gaba da zaman aurenmu cikin kwanciyar hankali da lumana da jin dadi. Allah ya kuma albarkaci yayanmu, ya ƙara mana waɗansu yayan kamar goma haka ko?

Ya kama hannuna ya matse sai da na ji ciwo har cikin zuciyata. Ya buɗe tafin hannuna ya danƙa mani makullin mota.

- Mota na sayo miki. Bai kamata ba a matsayina a ce matata tana yawo cikin motar ma'aikata. Mu sauka ki ga motar ko ta miki. In ba ta miki ba in canza ta.

Na jefa mashi makullan ga fuskarshi.

- Kar dai ki fidda mini ido domin za a ce maki mijinki ido ɗaya gare shi.

- Mi zan yi da kayan bawa. Inji ni , harya yi dariya.

- Ai bawan ya gode ma Allah tun da yana aure da mata mai asili. Farida ki yi a hankali fa kar da ki koma "da na sani". Domin akwai ranar da zan maida martani zan kuma maimaita miki abubuwan da kike gaya mini.

Na tashi na shiga ɗakina na kuble.

An yi wata takwas Farid ko a ka bai ma san ko ina gallaza mashi ba. Yanzu kai abin ya ishe ni ya ishi raina. Na ce zan ɗauki hayar gida don na dinga kwana don kawai ya ba ni takarda. Ina shirya kayana, ina zuba su cikin akwatina, Farid ya shigo.

- Uwargida ina za ki ne?

Na yi banza da shi, na ɗauki akwatina na wuce shi. Ashe tun fitar da na yi ya sa ɗaya daga cikin yan sanda masu tsaron shi ya bi ni sai ya ga inda za ni.

Kwana uku na yi ban koma gidanshi ba. Sai ga shi hankalina ya yi mumunan tashi da na ga halin da yayanmu suke ciki lokacin da Farid ya zo da su. Kowanen su ya yi kuka har ido ya yi ja, suka zo suka faɗa bisa ni suna ta kuka. Ban san wanda zan rarrashi cikin su. Har za su sa ni kukan ni ma don tausayin su. Farid ya nemi wuri ya zauna kanshi a sunkuye da kyar na rarrashe su suka bar kukan. Farid ya ɗago kai yana kallo na.

- Farida ban ce don ni ba amma don Allah ki ji tausayin yayanki, ki koma gida ki zauna ko yaran su dinga ganin ki don su samu kwanciyar hankali.



Shamsu ya koma hannuna na dama Shamsiya ta koma hagun suna kuka.

- Mama mu tafi gida, Mama mu tafi gida.

Hawaye suka cika mini idanuna.

- Farid na koma don yara amma da sharaɗi ɗaya kar ka je gurin da nike.

- In dai wannan ne ta kwana gidah sauƙi. Ba na sake hawa benenki sai in kin ba ni izini. Ni dai ki koma gida.

Na yarda na koma.

Tun ranar nan Farid bai sake hawa benena ba. Haka ya ba ni damar zama cikin falona. Kuma yaran suna wurina, sai in Farid na son ganin su ko in lokacin abinci ya yi, ya buga mini waya su sauka wurinshi. Yanzu ni da shi ba mu ko ganin juna sai waya.

Haka dai muka zauna har tsawon shekara ɗaya da rabi.

Ina kwance bisa doguwar kujera, da misalin ƙarfe ɗaya na dare, ƙarar waya ta sa na farka, na ɗauka, ashe Farid ne.

- Farida ina wuni? Yaya aiki? Yaya gajiya?

- Allah ya sauke mini gajiya; wai mine ne? na faɗa, cikin fushi.

- Farida ba komai don Allah ina neman wata alfarma ɗaya gare ki. Don Allah Farida kar ki ce komai, ni ma ba da so na ba ne, ma'aikatarmu za ta shirya wata babbar liyafa ta cikon shekaru biyu da kafawa. To shi ne aka gayyaci kowane ma'akaci da matarshi. In ba ka da mata ba ka shiga wurin liyafar. Don haka Farida ki taimaka mini mu tafi tare ko da minti biyar za mu yi a wurin.

Farid ya kai sati biyu da kowane, Allah sai ya tambaye ni sha-warar da na ɗauka. Da na ga ya dame ni, wayar ta dameni, sai na amince amma da sharaɗin kowa ya je cikin motarshi. Ya yi farin ciki da jin labarin. Ana gobe ne liyafar sai ya ba Irada Ambalan ta kawo mini. Da na buɗe sai na ga katin gayyata da kuɗi jikka ɗari da hamsin da wata yar wasiƙa wai in sayi tufafin da zan saka. Na fidda katin gayyatar na ba Irada ambulan kin, da kuɗin ta maida mashi kuɗinshi. Renin wayo, wa ya ce mashi ina buƙatar kuɗin sayen tufafi, ko an ce mashi zindir nake yawo? Na yi tsaki. Na ɗauki katin na buɗa na yi mamakin ganin Farid ne shugaban sabon bankin da aka ƙafa. Na sha zuwa bankin domin a nan nake ajiyar kuɗina amma ban taɓa ji ba ko cikin hira an ce mini Farid ne shugaban bankin. Bankin ya shahara cikin ƙasashen duniya masu amfani da harshen faransanci. Daga nan na gane abin da ya sa yan sanda suke tsare da shi da gidanshi, har da kamara cikin falonshi.

Ƙarfe tara za a fara liyafar amma ni sai ƙarfe goma na shiga ɗakina na shirya. Kawai don in ɓata mashi rai. Na yi wanka na tsala ado. Na aje motata na fito. Wata budurwa da wani saurayi suka tarye ni cikin fara'a. Na nuna masu katina, suka raka ni har ƙofar babban falon Farid. Yana tsaye yana jira na. Ya tarye ni da fara'a, sai da ya ba ni tausayi da na ga kowa na ciye-ciye shi yana tsaye a ƙofar gidan. Muka je muka zauna inda aka rubuta sunanshi domin sun fi ɗari mutanen da ke wurin. Ba irin da babu domin duk ƙasashen da ke amfani da harshen faransanci na cikin ƙungiyar sun aiko wakilansu. An rubuta sunan kowa da maƙaminshi da ƙasarshi. Na tarar da teburinmu cike da abinci iri-iri, kowa na ci yana hira da matarshi sai mu. Na ɓata rai na game fuska don kar ma ya ga damar hira da ni. Don na ƙi ci shi ma bai taɓa komai ba ya yi zugum yana kallon jama'a. Farid ya umurce ni in tashi ya gabatar da ni ga magabatanshi. Na ƙi tashi kamar ya mini kuka.

- Ba kai za ka gabar da ni ba. Kuma bari in gaya maka ban zo a matsayin matarka ba a matsayin yar rakiya na zo kuma minti biyar kawai zan yi.

- Kai, Farida dama kin saba sa ni kuka yanzu kuma kukan za ki sa ni gaban dubun jama'a? Dama na sani masu mata aka gayyata ba ni ba gwabro. Abin da nike so da ke don Allah, don

Annabi in an zo ɗaukar hoto kar da ki kunyatar da ni domin hotona za a ɗauka, don Allah Farida ki taimaka mini mu ɗauka tare.

Idanunshi suka cika da hawaye, ya fidda wani ƙyalle ya shafe fuskarshi, ya sunkuyar da kanshi. Jim kaɗan ya tashi ban san inda ya je ba. Bayan minti shidda ya dawo sanye da tabarau.

- Farida ki sha ko da ruwa ne.

Na mashi tsawa sai da mutane suka kalle mu.

- Ba na sha!

- Farida don Allah ki yi a hankali, duba sai da kika sa kowa ya kalle mu.

- Su kalle mu mana.

Ina magana da ƙarfi don ya yi fushi. Da ya ga haka sai ya tashi ya ba ni wuri. Wani ya ɗauki mikuro ya ce a shirya za a fara ɗaukar hotuna. Farid yana tsaye baya na, ya dafa kujerar da nake zaune bisa ita, yana kallon waɗanda suke ɗaukar hotona. Ana ta kiran wakillan da ɗaya-ɗaya. Har na ɗau anniyar ƙin ɗaukar hoton da shi, sai dai na ji tausayin shi domin in na mashi haka kaina na ma. Da aka kawo gare mu Farid ya kalle ni, ya ƙara ba ni tausayi. Na tashi, ya kama hannuna muna takawa ɗaya-ɗaya. Sai mutane suka ɗauki taɓin da ban san dalilinshi ba. Na zauna bisa kujera, na ɗora ƙafa ɗaya bisa ɗaya, Farid yana tsaye a kaina ya ɗora hannunsa ɗaya bisa kafaɗata ɗayan ya saka shi aljifu. Da aka idar da ɗaukar hotuna, tunda yake dama shi ne ya tsai da ni, sai na ɗauki jikkata, ban yi sal-lama da kowa ba. Na zo daidai ƙofar fita kamar an ce mini Farida juyo ki gani: idanuna sai kan Farid da wata mace jar fata tana ƙoƙarin sumbatar shi. Ban san balaraba ce ba ko baturiya ce, da dai muka yi ido huɗu da Farid sai ya ture matar ya bi ni da gudu, na shiga motata na tuƙa. Daran nan daga ni har shi ba wanda ya yi barci cikin mu ba a minti biyar wayar da ke ɗakina ba ta yi ƙara ba. Ta yi ta ƙara har ya gaji ya bari. Da farin ya yi zaton ba na ɗakin ne sai da ya fita waje don ya ga ko na shigo. Motata na tsaye kuma yan sanda sun tabbatar mashi da ina cikin gida. Ƙarar waya ta dame ni na ɗauki kan wayar na aje ba daidai ba.

Washe gari tun da safe ya fito falonshi ya zauna yana jiran fitowa ta, yana sanye da rigar barci. Na fito ya tashi ya tarye ni.

- Farida ina kwana? Yaya gajiya? Farida don Allah ki manta da abin da kika gani jiya da dare, wallahi matar nan na rasa yadda zan yi da ita ne ta shafa mini lafiya. Na dakatar da shi.

- Kwantar da hankalinka malam, ba na son ka fa, don haka ban damu ba, ko ba ka san da wannan ne ba?

Farid ya dafa kanshi, ya zauna a ƙas. Na wuce shi.

Sati biyu bayan liyafar, ina gidan Mimi gorata sai cikin dare na tafi. Da zan zo gida sai na biya gidan iyayena don na gaida su. Ba kowa a gidan, sai da zan fita na gamu da Inna za ta shiga, na ɗan laɓe na ba ta wuri ta wuce.

- Sannu da zuwa Inna.

Ta amsa mini cikin fushi. Na yi mamakin haka, ta wuce ni.

- Yanzu Farida wane irin rashin mutunci ne wannan? Tun jiya da dare aka kwantar da mijinki asibiti har yanzu ba ki taka wurinshi ba, mine ne nufinki?

Daga jin haka, na ɗauki motata sai asibitin da aka kwantar da Farid. Na yi haka don gudun fushin baba. Na shiga na yi sallama, likitan na gyaran robar ƙarin ruwa ta ga Farid. Na tarar da baba da Alhaji da tanti Hawa suna zaune. Alhaji kaɗai ya amsa sallamar. Likitan ya mini murmushi.

- Madam ina wuni?

- Lafiya lau.

Likitan ya san ni domin shigar Farid uku kenan wurin kwantar da shi a asibiti, tun dawowata gidanshi. Farid yana barci na shigo na zauna a gefen gado ina kallon shi tausayinshi ya kama ni domin ya rame kamar icce, kamar ba shi ba.

- Sai yanzu kika samu damarzowa? Wallahi in ba ki yi hankali ba ke za ki zama cikin na farin ga shiga wutar gobe ƙiyama. A zuriyarmu ke kaɗai za ki zama yar wuta domin ba ki ma mijinki biyayya.

Baba ya yi ta zagi na har na yi kuka. Ta inda yake shiga ba ta nan yake fita ba. Na yi zaton ko Farid ne ya gama ni da shi. Sai da Alhaji ya saka bakinshi.

- Haba Malam ƙyale ta hakanan mana mi ne na zagin ta cikin asibiti?

- To Alhaji a kullum in an kwantar da Farid sai a ce mana ba a ga ciwon da ke damun shi ba. To Alhaji wallahi ba banza ba, akwai dai wani abu a ƙas.



Alhaji ya ja baba suka fita waje. Na yi tagumi, hawaye na ta zubo mini ina sa gefen mayafina ina shafe su. Sai can Farid ya juya, ya yi sauri ya buɗe idanunshi. Ya kirai sunana a hankali. Har zan ƙi amsa mashi sai baba ya shigo na amsa mashi.

- Na'am Farid ina jiki?

Baba ya nufo gadonshi ya harare ni.

- Ke, jakuɗa ma mutane, kukan mi kike? Kukan rishin kunya? Wallahi in har ba ki canza halinki ba, to zan ɓata miki rai, kina ji na? Duba uwarki, da kika tashi haka kika ga tana mini? Amma albasa ba ta yi halin ruwa ba? Duba har ya kwantar ta bisa robar ƙarin ruwan, ba, ki iya gyara mashi ita? Ke kina lafiya kuwa?

Ya ɗaga hannun Fárid ya gyara mashi ƙarin robar ruwan. Faɗace-faɗacen da baba ke mini ya ɓata ma Farid rai. Na gane haka ga fuskarshi. Baba ya koma inda suke aje kayan su, ban san abin da yake nema ba. Farid ya kalle ni ina kuka, ya girgiza kai.

- Farida ba ni ruwa in sha.

Na tashi na ɗauko mashi ruwan na ɗan ɗaga kanshi na kafa mashi kopin a baki ya sha. Da ya ƙare sha sai na mayar da kanshi ya kwanta yana ta aikin kallo na.

- Farida yanzu kika zo ne?

- Na ɗan jima.

- Ina barci ko?

- Kana barci ni kuma ban tashe ka ba saboda baba yana cikin ɗakin.

- Ba ki kyauta ba, don mi ba ki tashe ni ba? Farida kirayo mini dokta, ciwon nan ya dame ni.

Na tashi na fita na je na kirayo dokta muka zo tare, ya ƙara mashi wani magani cikin ƙarin ruwan, ya fita.

- Farid ni zan koma gida.

- Farida tun yanzu?

Na tashi na fita ba mu ko yi sallama da juna ba. Ina jin shi yana kira na, har na fita ban ko waiwaya ba balle na amsa kiranshi. Kwana uku Farid ya yi a asibiti, kullum sai na je ganin shi safe da dare don gudun fushin baba Amma duk lokacin da na je sai ya kama mini faɗa sai Alhaji ya sa baki. Abin ya ci mini tuwo a ƙwarya na riƙa jin kamar kar na je ganin Farid, tausayin ma da nake ji ya gushe.

"Yanzu Farid har da neman ya gama ni da iyayena! An sako shi, ya zo ya iske ni a nan," na faɗa cikin zuciyata.

Da aka sallame shi, baba ya mini waya ya ce da ni maza na zo na ɗauke shi. Duk da ranar ina da tulin aiki, na aje na je na ɗauko shi na kawo shi gida, ko "ina kwana" ban mashi balle ma na tambaye shi lafiyar jikinshi.

Da magariba Zainabu da mijinta Ali suka zo masa barka da samun lafiya. Bayan sun gaisa da shi Zainabu ta hawo bene ta zo wurina ina cikin falo ina koya wa yayana karatu domin malamin da Farid ya ɗaukar musu saboda karatun dare bai jin daɗin jikinshi.

Zainabu ta yi sallama, ta shigo muka gaisa.

- Farida, lafiya kina nan Farid shi kaɗai kwance cikin falo? Ita ba ta san irin zaman da muke ciki ba.

- Yanzu muka hayo bene.

Na tashi muka shiga ɗaki ni da Zainabu, na bar yara a falo.

- Farida amma komowarki ba ta ma Farid ba. Tun da kika dawo bai kwana uku bai yi rishin lafiya ba.

Na gyara zama na ɓata rai.

- Mi kike faɗa ne? Ban gane ba?

- Ke marar gaskiya, mi ne na game fuska? Na ce tun da kika taɓa shi.

- Inji wa ya ce ba na tattalinshi?

- Halan ni makamniya ce? Inda a da ne wallahi ba ki barin shi, shi kaɗai cikin falo kwance, bayan kin san ko ba ya da lafiya. Tuno a zamanin da ko ciwon kai ya yi kuka kike mashi tamkar ke kike ciwon ba shi ɓa. Ke don Allah wa za ki maida yarinyarki? Farida duk wanda ya san ku a da minti ɗaya za ya yi tare da ku ya san kun canza.

- Ba na son munafuci, kina ji na? Ina ke ina shiga harakar gidana?

- Allah ya huci zuciyarki, Allah ya ba ki haƙuri. An ce gaskiya barkono ce ko?

Da Zainabu ta lura da ba na son hirar sai muka canza zance muka shiga hirarmu ta duniya. Muna cikin hirar, Zainabu ta yi tagumi tana kallo na.

- Ke, in mayya ceke to ki ci kanki.

- Farida ba zancen maita ba ne ni wallahi ko da ba ki son na yi zancen. Farida ki ma Allah ki ma Annabi ki tausaya ma kanku. Duba yanda kuka zama ke da shi, abin tausayi kina takura wa rayuwarku. Don ba ki dibin kanki ne kin ga yadda ki ka koma kuwa?

- Ke, aiki ya muna yawa shi ya sa duk muka rame.

- A'a Farida ni fa ba yarinya ce ba na fa girme ki da shekara har wajen uku fa. Kawai rashin jituwarku ne.

- Wa ya ce miki muna tashin hankali?

- Farida duk ke ce ummal aba'isan ciwon Farid.

- Na ji na ɗauka yanzu don ki tona mini asiri kika taso daga gidanki kika zo nan?

Ta fashe dά dariya ta sa mayafinta ta shafe fuskarta.

- Farida ba ni da man shafawa tashi ki ba ni.

- Ba na ba ki sai dai na zuba a salanga.

- Haba yar bafullatana ni fa tabbashiyarki ce domin ni ba'ara ce. Ke, Ali ya ce ki ba shi ramcen jikka ashirin wai kunya yake ji ya tambaye ki. Baƙo muka yi daga Dogon Dutsi.

- Na san halinku arawa da rishin hankali. A ɗauko yar gujiya a zo maraya yau, a ce jibi za a koma gida kamar sun ba ka ajiya. Ba'aran mutum!

- Ke ba na son renin wayo kin ji?

A daidai wannan lokacin ne Shamsu ya ƙwanƙwasa ƙofa, Zainabu ta amsa mashi ya shigo tare da sallama.

- Tanti wai ki zo ku tafi in ji tonton.

Zainabu ta yi zumut ta tashi tsaye ta ɗauki mayafinta.

- Bari ki ga na tashi domin duk mace mai imani ba za ta yi abin da zai ɓata ma mijinta rai ba. Balle ma yanzu da duniya ta sake mata sun yi wayo suna neman illimi kuma ba wadda ba ta san dokokin aure ba, ta san haƙin mijinta ta kuma san nata. Yanzu kam ba wadda ba ta ma mijinta biyayya sai jahila, ko kuma sai wadda Allah ya ƙaddaro yar wuta ce.

Maganar Zainabu ta razana ni ƙwarai ba kaɗan ba. Na fito daga rakiyar su Zainabu na shigo falon Farid. Na tarar da Farid zaune kusan wayar tarfo. Ya miƙa mini wayar.

- Bashir ke son miki magana.

Na karɓi waya na zauna kan hannun kujerar da ke kusan teburin da ake aje wayar. Mun gaisa da Bashir kenan ya fara zagi na. Ba irin zagin da bai mini ba kamar na aje wayar. Hawaye na zuba tamkar an buɗe pampo. Bai ma ba ni damar na yi magana ba. Da na ce yaya Bashir sai ya kwaɓe ni. Na aje wayar ina ta kuka, Farid ya taso ya zo inda nake.

- Lafiya? Farida wani ya zama babu ne? Rasuwa aka yi ne?

- Ban sani ba! Ai fatanka kenan wani ya mutu to ba wanda zai mutu kwananshi bai ƙare ba.Ba ka ko jin kunya kamar ka kana ta gama ni da dangina. Ka gama ni da baba da Inna har da tanti, yanzu da Bashir za ka gama ni. To in ka gama ni da su sai kuma mi? Na ce ba na son ka ka je ka gama ni da uban da kake so.

- Ni kike zagi haka?

- An zaga Farid, maras mutunci.


Har zan sake magana ya kama hannuwana ya zaunar da ni. Na tashi tsaye ya koma ya zaunar da ni. A na ukun, ya zaunar da ni tun ƙarfi sai da ƙashin bayana ya amsa. Idanunshi suka rikiɗa suka zama jawur kamar garwashin wuta. Yana ta huci, tsoron shi ya kama ni.Gani nake yanzu zai hau ni da duka. Ya ɗora ƙafa ɗaya bisa kujerar da nake zaune yana nuna ni da yatsa. Na sunkuyar da kai gabana na dakan shida-shida.

- Wa kike zagi haka? Farida ko hauka kike yi ne? Ashe ba ki da wayo? Farida masifarki ta ishe ni. Ya faɗa tun ƙarfi, sai da na zabura.

Tsoro ya daɗa kama ni. Ya ta da ni tsaye ya damƙe mini hannuwa ya kalle ni sosai ina ta karkarwa ya ture ni na faɗi bisa kujera. Ya je ya buɗe taga yana kallon farin wata da tarmamu tsawon minti bakwai. Ya rufe tagar ya dawo wurina, ina ta kuka. Ya koma tsayuwar ta ɗazu. Tsoro tamkar na nutse cikin kujera.

- Farida ba wai ba na iya sakin ki ba ne. Ki san da wannan kuma duk abubuwan da kike mini wai ba ba su ci mini rai ba ne ba. Kawai girman baba malam da abokina Bashir nake dibawa domin a duk lokacin da kika ɓata mini rai har sai na ɗau niyyar sakin ki sai na tuna baya domin ban rena su ba. Kina sane da a hannun malam muka tashi. In na ce ya mini laifi sai in na masa ƙazafi kawai, Allah kuma na gani na. Abubuwan da baba malam ya mini ko ma'aifina bai mini su ba, ko rabin-rabin. Lokacin da muke makaranta in za mu yi jarabawa baba malam ni yake ma rokon Allah alhali ko tare muke da Bashir, ko fatiya bai masa, ni yake ma. Bashir sai in Inna ta mashi. Kan ya mini rokon Allah Bashir ya kamata ya ma domin shi ne ɗanshi, amma shi bai dibi wannan ba. Matsayin ga da nike da shi Allah ya ba ni shi da taimakon malam. Ina sane da wata ya yi ba ya barci, yana rokar mini Allah.Kin gani ga shi alhamdu lillahi na gode ma Allah.

Bashir tare muka tashi, tun muna ƙanana har zakkuwa yanzu akwai mutanen da ba su san ba mu ba yan tawaye ba ne. Ki san da tun ranar da kika zo duniya iyayenmu suka ɗau alƙawarin za su aurar da mu in har Allah ya ba mu tsawon rai. To alƙawarin



nan me ba ni son na rushe. Ko ma lokacin da muka samu saɓani da ke, lokacin da na auri shaiɗaniyar can, ban ce na sake ki ba ko na faɗa tsakanin ki da Allah? kawai cewa na yi ki canza gida.Ko ba haka aka yi ba?

Farida wulakancinki ya ishe ni hakanan. Shekara biyu kenan da kike gallaza mini masifa iri-iri. Ke ma fa mutum ce kamar ni. Ba ki tsoron wulakancin ya dawo kanki? Farida ban yi zaton za ki mini haka ba, domin ko ba komi aimun zama yan uwan juna, kuma ga yaya mun samu har uku. Shi ya sa duk abubuwan da kike mini ban damu ba domin ni na kama girman iyayen da suka haɗa mu. Allah ya yafe musu zunubansu ya kuma ba su tsawon rai mu zauna da su. Farida shekara biyu kika yi ko ruwan gidana ba ki sha, abinci ba ki ci. Tuna fa sarai, ɗiya mata abin da suka ga uwarsu ta yi shi za su yi su ma. Yanzu wannan irin tarbiya har ki bari yayanki su gani? Farida in matar Shamsu ta yi mashi haka yaya za ki yi ne? Tsawon rai dai gare ni, da na mutu. Kuma kin yi sa'ar samun miji mai haƙuri. In ba ni ba Farida, ba wanda za ki gallaza ma haka ya ƙi sakin ki. Na ji kin ce na gama ki da iyayenki. Haram! Haramiyata in riƙa gama ki da su. Ai ba yau ba ne domin shekara biyu kenan kawai suna gani ba mu shiri ni da ke. Kin san da sau uku aka kwantar da ni a asibiti, duk saboda ke. Gaya mini ranar da kika san da haka. Ba sai kin ji ba a bakin wani ba? Da zaran sun tambaye ni sai na shirya musu ƙarya. Kin san azabar da za a ma maƙaryaci gobe ƙiyama? Farida gurinki shi ne na ba ki takardar saki ko? Domin ala tillas sai na rabu da ke. In ba haka za ki kashe ni ko ki kashe kanki. Kin ga yadda kika koma, ni dai ina gani ina ji ba ni kai kaina mahallaka...

Ya tashi tsaye ya saka hannuwanshi cikin aljihu.

-...Kwantar da hankalinki, zan ba ki takarda kin ji. Ina roƙon ko don Allah ki yafe mini da takurawar da na miki. Na san da ba ki so na kika zauna da ni har tsawon shekarun ga da suka wuce.

Ya bar ni zaune ina kuka, ya shiga ɗakinshi.

Bayan tafiyarshi sai na yi minti talatin zaune ina kuka bai fito ba. Na tashi na hau bene na shiga ɗakina na kwanta. Barcin bai mini, na tashi zaune, na jingina ga kan gado, na ɗauki matashin kai na ɗora bisa cinyoyina, ina ta tunani. A gaskiya in na duba na san da ba ni da gaskiya. Na takura ma Farid domin ni na jawo su "la mama" har suka magance shi. Na san da ya ɓata mini rai fiye

da yanda nike zato domin mijin da za ka haifa ma ɗa kuma ya ce ba shi ba ne uban, ai lalle da ciwo. Amma ya kai sau dubu da yake roƙo na gafara na ƙi yafe mashi. Ya kai sau biyar a dai sani na, da yake sawo rago biyu ko huɗu ya ce mini in kai ma baba malam a yanka domin ina zargin shi da ƙin yin sunan su Shamsu. Ko Allah in muka mashi laifi yana yafe mana. Ko Allah ma ya ce, mutum in ya maka laifi, in har ya gane kurenshi, har ya zo ya roƙe ka gafara, to ka yafe mashi. To in na san da wannan don mi ban yafe mashi, kuma ai ba ma laifinshi ne ba. Duk abubuwan da ya mini, asiri ne suka mashi, suka wanke ni daga zuciyarshi. Farkon zuwan su Fatsuma gidanmu sai da Farid ya mini faɗa ya ce ina ni ina gorance da yan mata ga ni matar aure. Ya ce kar da na sake bari su shigo mashi cikin gida. Da ya lura na ɓata rai sai bai sake mini maganar ba. To yanzu in ya sake ni in su baba sun tambaye dalilin rabuwarmu mi zan ce da su? Na san ko daga sun tambaye shi zai gaya musu. Baba da Inna za su tsine mini.

Na tashi na gabatar da nafila raka'a goma sha bakwai don na nemi gafara ga Allah ya kuma tabbatar mani da alheri. Na zo na kwanta, barci ya kasa ɗauka ta, na tashi zaune ina rungume da matashin kai ina ta kuka. Na yanke shawara tun da safe in na tashi zan je na durƙusa gabanshi na roƙe shi gafara. Saboda da kuka har ba na iya ɗaga idanuna, kaina na ta mini ciwo. Ni kam ban ji daɗin zaman aure ba. Kullum ni ke nan cikin baƙin rai. Ina cikin kukan ne sai na ji an turo ƙofata a hankali. A zatona Irada ce domin ba ta rabuwa da ciwon ciki. Ba a kwana uku ba ta zo ta tashe ni da kuka ba. Ta ce mini cikinta ke ciwo. Don haka ban ɗaga kaina ba domin ba na so ta ga halin da nike ciki.

Ina sauraren shigowarta, ba ta shigo ba. Na ɗaga kaina don na ga ko wane ne. Farid ne tsaye yana riƙe da ƙofar yana kallo na. Gabana ya faɗi ras. Tsoro ya kama ni kar da a ce takardar rabuwa ya kawo mini. Na sunkunyar da kaina, hawaye na zuba tamkar an buɗe pampo. Bai ce da ni komai ba, yana kallo na. Ya yi ajiyar zuciya ya maida ƙofa ya rufe. Ina jin san takalminshi lokacin da yake sauka domin yana gudu ne. Ko tashi nike na je na roƙe shi gafara? Ina ta saƙe-saƙen abin da zan yi, ban san lokacin da barci ya ɗauke ni ba. Kuma in safiya ta yi ina da tafiya a ƙasashen waje.

Ƙarfe uku da minti talatin da uku na farka na tashi da sauri na yi wanka tare da alwalla don na gabatar da sallar safe ko da yake dai na makara. Ban tsaya wata kwalliya ba, na san ko cikin jirgi sai na yi. Na ɗauko ɗan akwatina da nake balaguro da shi na fara zuba kayan da na san zan yi amfani da su. Ina ta sauri kar da na makara. Farid ya turo ƙofar ɗakina. Ya shigo ya yi tsaye yana kallo na, da ya ga ina ta zuba kayana cikin akwati. A zatonshi bar mashi gidanshi zan yi. Ni kuma gabana na dakan uku-uku, ina cewa na san yanzu kam takardar ya kawo. Ga shi kuma zan yi tafiya, yaya zan yi ne? Ga tafiya ga rabuwar aure? Ba zan iya fasa tafiyata ba domin zuwana na da muhimmanci a wurin taron. Tun jiya ya kamata a ce na tafi tare da shugaban ƙasa, da yake ba wuri sai ni da ministan al'adu da motsa jiki, da ministan kiwo da noma da sakatare janar na ministan cikin gida muka zauna muka shiga cikin jirgin "Air Afrique" mai tashi yau da safe a ƙarfe bakwai da minti goma sha biyar. Farid ya yi maza ya tambaye ni cikin fushi inda za ni. Ya zo daidai inda nake.

- Kin iya gaya mini inda za ki haka?

Na ɗaga kai na kalle shi.

- Bamako za ni.

- Ba ... mi? Neman mi?

- Bamako, wurin taron shugabanin ƙasashen Afirika da shugabanin ƙasashen turai waɗanda suka mallaki Afirika.

Da na ba shi cikakken bayani sai ya zauna bisa gadona ya ɗauki ɗan akwatin kwalliyata da na mance ya sa mini shi cikin jika. Ya ƙura mini ido tamkar yau ya fara gani na sai da na gama shirye-shiryena, na rufe akwatina.

- Bari na kai ki filin jirgi.

- Na gode yanzu na ma direbana waya zai zo ya kai ni.

Kamin na ƙare magana sai muka ji tsayuwar motar.

- Ba ni adireshinki.

- Ni ma ba ni da cikakken adireshi ai in na jė can zan yo ma waya.

- To Allah ya kai ki lafiya ya kiyaye hanya.

- Amin.

Ya raka ni har wurin mota, ya buɗe mini ƙofar. Na shiga na zauna ya kire ni na fito na je wurinshi kaina a sunkuye.

- Da ma don mu yi ban kwana na Allah ya kai ki lafiya. Da wane lokacin jirgin zai tashi?

- A ƙarfe bakwai da minti goma sha biyar. Jirgin "Air Afrique" za mu shiga.

Da muka isa filin jirgi sai aka shaida muna da akwai jirgin da zai sauka nan da minti biyar yana ɗauke da yan ƙasar Italiya da yan Sanagal da yan Faransa. Don haka muka shiga jirgin tun da akwai wuri, domin jirgin "Air Afirik" sai ya biya wasu ƙasashen. Haka kuwa aka yi cikin mintocin da aka shaida muna jirgin ya sauka. Bayan waɗansu mintoci jirginmu ya tashi. Cikin jirgin ina zaune kusan wata mace ana ce mata Monik, yar Italiya. Ta shaida mini ita ce mai kula da hulɗa tsakanin ƙasarsu da ƙasashen duniya. Muna cikin hira sai tunanin Farid ya faɗo mini a rai. Na yi nadama don mi ban roƙe shi gafara ba? To yanzu in na mutu fa? Na shiga uku kenan. In na mutu a halin yanzu sai wuta. Ban san lokacin da hawaye suka dinga kwararo mini ba sai da Monik ta tambaye ni lafiya? Na shaida mata ba komai. Nan da nan ta shiga mini hira ta ban dariya har muka isa ƙasar Mali ban sake tunanin Farid ba.

Aka kai mu masaukinmu. Ina aje akwatina, ana mini waya. Mai girma shugaban ƙasa na son gani na. Na yi wanka na caɓa kwalliya na je otel ƙin da aka sauke shi. Ya shaida mini da yana son ganawa ne da waɗansu shugabannin na ƙasashen Afirika amma sai kuma na ba da shawarata. Nan dai muka yi ta aiki sai ƙarfe biyu na dare na koma otel kin da na sauka. Na so na buga ma Farid waya don in ba shi lambar wayata. Sai na ga dare ya yi; na bari sai da safe in buga mashi, kamin mu je wurin taron. Ƙarar waya ta tashe ni daga barci. Na yi miƙa tare da salati na ɗauki agogon hannuna: ƙarfe shida da minti tara. Na yi mamakin abin da yake sa ni rishin tashi da sauri. Na shiga ban ɗaki domin taron, ƙarfe shida za a buɗe shi. Don haka ba ni da lokacin buga ma Farid waya domin ko ba komi mu yan jarida mu ya kamata mu fara zuwa. In kuma mutum ya makara ko shi wane ne ba a barin shi ya shiga. Muna wurin taron har ƙarfe goma sha biyu na dare. Da aka ɗaga taron sai shugaban ƙasa ya shiga ganawa da wakilan ƙasarmu da suke da zama a ƙasar Mali, ɗauko daga yan kasuwa zuwa ɗalibai da sauransu. Ƙarfe uku na dare muka ci abinci muka shiga ganawa da sauran yan jaridu na ƙasashe daban-daban. Sai ƙarfe hudu na dare muka watse. Washe gari

ƙarfe bakwai muka sake shiga taron sai wajen ƙarfe huɗu na dare muka watse. Aka ce muna mu zauna mu huta sai ƙarfe huɗu na marece za a rufe taron gaba ɗaya. Da na kwanta sai ƙarfe ɗaya na rana na farka. Na yi na yi na buga waya a Nijar, na kasa. Don haka na tashi na ɗauki taksi sai gidan jikadan ƙasarmu a ƙasar Mali. Domin lokacin da nike barci na yi wani mafarki mai ban tsoro, wai Farid ya mutu, namomin daji sun yi ɗaya-ɗaya da shi, ina kallo. Da na isa gidan wayar sai suka shaida mini da wani babban iska aka yi shi ya tsinke wayar. Wata mace ta ba ni kan wayar na buga a ofishinshi. Ba wanda ya ɗauka domin suna aiki ne tun da safe har ƙarfe uku, su yi sauka ɗaya. Sai na tuna da wayarshi ta hannu, watau salula, ina jiran in ji muryar Farid sai kawai na ji ta Bashir, yayana. Haba gabana ya faɗi ras, cikina ya murɗa. Mi zan ji ne? Na tuno da mafarkina. Gumi ya karyo mini: ba shakka Farid ya mutu, shi da ko ban ɗaki zai shiga da wayar yake zuwa. Ina magana muryata tana rawa, hawaye suka fara zubo mini.

- Bashir mutuwa Farid ya yi ne? Mi ya same shi. Wayyo Bashir ya mutu ne. Na lalace, wayyo, wayyo ni kaina.

- Ke! ke kina lafiya? kwantar da hankalinki. Ina kika je ne, da ni da jakadan ƙasarmu a ƙasar Mali, ba yadda ba mu yi ba mun ƙasa samun ki ga waya.

- Bashir mi aka yi ne?

- Kina sane da hatsarin jirgin da aka yi na "Air Afrique" wanda ya kamata ku shiga? Ya yi zaton ko kina ciki ne. Sai ya ɗauki mota ya nufi filin jirgi...

Rigata ta jiƙe da zufa tamkar ruwa aka zuba mini.

-...Kin san jirgin bai fi minti uku da tashi ba ya kama da wuta. Yana cikin gudu injinshi ya kama da wuta.

Ban san lokacin da kan wayar ya sulluɓe mini ba. Na yi ihu sai da macen da nake kusan ta ta zo da sauri ta kama ni ta zaunar wayar.

- Farida kwantar da hankalinki bai mutu ba yana nan da ransa hi. Amma ya yi mummunan rauni domin jikinshi ba inda bai toye ba. Yanzu haka yana assibiti an kwantar da shi.

- Ina iya zantawa da shi?

- To ba za ki iya ba domin tun da aka kwantar da shi bai motsa ba, yana barci.

- Wayyo na shiga uku.

- Mi ne na ta ɗa hankali bayan na ce miki yana da ranshi. Yaushe za ku dawo ne?

- Yau da misalin ƙarfe huɗu taron za ya kammala amma mu da tawagarmu sai gobe za mu dawo.

- To sai kin zo.

Tun da na aje wayar na nufi masabkin shugaban ƙasa na shaida mashi tashin hankalin da nike ciki domin na san shi mutum ne mai jin tausayi wanda ya san da haƙƙin yan ƙasa na rataye a wuyanshi. Halayenshi suka sa yan ƙasa suka sake zaɓen shi a karo na biyu lokacin da wa'adinshi na mulki ya cika. Nan da nan ya buga ma takwaranshi na ƙasar Mali waya suka sanya ni jirgin soja. Cikin lokaci ƙanƙane ga ni filin jirgin Yamai.

Na ɗauki takasi sai asibitin da aka kwantar da Farid. Ban samu matsalar ganin ɗakinshi ba domin na gamu da Ali ya zo ganin shi zai koma sai ya rako ni har wurin su baba domin shi da Bashir ke jinyar shi. Na durƙusa na gaida su. Bashir kaɗai ya amsa mini, ya nuna mini kujera. Da kyar na samu na zauna bisa kujerar domin ban zo zama ba, ganin Farid na zo. Bashir ya miƙo mini kopin ruwa na kurɓa, na kasa haɗe shi sai kawai na zubar. Baba ya kalle ni ya girgiza kai. Bashir ya tashi ya ce da ni na bi shi. Farid ne kwance cikin ɗaki mai madubi. Duk jikinshi an naɗe shi da farin bandeji, ba inda kake gani ga jikinshi sai hancinshi da idanunshi da bakinshi su ma don ba shi damar magana da lumfashi da sauransu. Bashir ya shaida mini ba a fi minti biyar da aka fidda mashi iska mai taya shi lumfashi ba.

- Yanzu kam alhamdu lillahi domin ya fara lumfashi da kanshi, har motsi ya yi.

Na kalle shi daga ƙafafuwanshi har ga kai. wanga in mutum bai duba ba da kyau ba za ka ce ba mutum ne ba a miƙe. Shi ko motsi bai yi, tamkar bai da rai.

"Yanzu in Farid ya mutu mi zan ce ma Allah gobe kiyama?" na faɗa cikin zuciyata. "Ya Allah ka ta da mini mijina, ka koro mashi da lafiya.Yanzu saboda ni Farid ya shiga wannan mummunan halin?"

Na fashe da kuka na faɗi ƙasa lumfashina ya ɗauke. Da misalin ƙarfe tara na dare na farka daga barci, a zatona Bamako nake; sai kawai na gane ni kwance bisa gadona, cikin

ɗakin barcina. Da hankalina ya dawo gare ni, na tashi na je na shiga motar ma'aikatar don na koma asibiti, sai kawai na dinga hajijiya na fito na koma na kwanta. Allurar barcin da aka mini a kai ba ta ƙare aikinta ba.

Washe gari kamin ma a yi kiran sallar asuba, ina falke, da na gabatar da sallar sai na ɗauki motata sai asibiti. Gabana aka buɗe ƙofar, ina zaune cikin mota. Na shiga ban tarar da su baba ba, na san da suna masallaci. Mamaki ya kama su da suka tarar da ni zaune. Mun je mun ga Farid mun dawo, Bashir da baba suna hira, ina zaune kusa da su amma ban san hirar da suke yi ba domin ba na ma jin abubuwan da suke faɗi. Ƙarfe shida da rabi, Alhaji da Hajiya suka shigo ɗauke da karin safe. Suka yi, suka yi da ni na sha ko da ruwan shayi, na ƙi. Wajen ƙarfe bakwai babban likitan ya shigo; jar fata ne, wai shi David. Na ɗan ba shi lokaci ya kimtsa sa'annan na tashi na je bironshi, ya tarbe ni da fara'a domin ya san ni, don kullum asibitin ake kwantar da Farid, ya nuna mini wurin zama.

- David ina son ka ba ni hanya na je da shi ƙasar waje.

- Farida kwantar da hankalinki toyewar ga jikinshi ne kawai ta tsaya. Bai shiga cikin jikinshi ba. Ba abin da ya taɓa ƙwaƙwalwarshi, haka kayan cikinshi, kuma zuciyarshi na aiki daidai yadda ake so. Kar da ki samu damuwa nan da sati uku zai tashi. Yanzu ma alluran sa barci muke mashi don ƙwaƙwalwa ta huta.

Maganganun dokta David suka kwantar mini da hankali har na saki jikina muna hira da shi.

- Farida ki yi a hankali fa kar da ki rasa mijinki.

- To dokta David na ji.

- Farida, kwana yake yana kiran sunanki. Yanzu ma daga ya falka zai fara kiran sunanki.

Ya buɗe waɗansu takardunshi, ya fiddo mini sauran hotunana da ba su ida toyewa ba. Daga cikin aljifun rigarshi ya fiddo shi.

Abubuwan da Dr. David yake faɗa mini game da Farid ya sa na ji tausayi, na roƙe shi ya bar ni na shiga na gan shi don haka ya ba ni minti biyar. Na shiga na zauna dap da shi, ya buɗe idanunshi ya kalle ni, ya koma ya rufe su, tausayinshi ya kama ni. Na sumbace shi na fito na zauna kusan su baba sai ya ce da ni na tashi na kom i gida. Har kuka na yi domin ban ga ba abin da

zan yi a gida sai ganin tashin hankali. Ya bar ni in zauna ko in ina hira na mance. Na tashi na koma gida cikin ɓacin rai.

Da rana na dawo haka da dare ma. Haka na dinga sintiri tsakanin asibiti da gida. Na ma mance da abinci sai in na zo nike ko ruwa ba na sha. Tun da na dawo ni nike girki ina kai ma su baba a asibiti. Bayan sati ɗaya da dawowata, baba yana bari na na wuni tare da su sai in lokacin girki ya yi in koma gida. Yan uwa da aminnan arziki suka dinga zakkuwa ganin mu, suna taya mu jaje.

Ni da Riyanatu muna zaune gefe ɗaya, muna hira sai dokta ya leƙo ya kira ni da hannu, na tashi na bi shi sai ɗakin Farid. Ya buɗe mini ɗakin, na shiga na rufe. Sawun tafiyata ya sa Farid ya juyo muka yi ido huɗu da shi, muka ma juna murmushi. Na zauna bisa gadonshi na ƙura mashi ido. Na mashi irin kallon nan da na san ya fi so, wanda ya ce har rikitar mashi da ƙwaƙwalwa yake. Ya kira sunana a hankali.

- Farida ashe ba ki mutu ba, kina nan da ranki. Jiya dokta yake ba ni labari ashe ba ki cikin jirgin nan na "Air Afrique". Farida in da kin mutu yaya zan yi da rayuwata?

- Farid don Allah ka yafe mini abubuwan da na maka, na faɗa cikin kuka.

- Farida ni ya kamata na nemi gafara daga gare ki domin ni ne mai laifi ba ke ba. Ni kam na yafe miki ba komai Farida Allah ya yafe muna gaba ɗaya.

- Amin.

Ya yunƙura zai tashi na kwantar da shi. Na san da ya ji ciwo. Ya yi ajiyar zuciya, yana lumfashi ɗaya-ɗaya har ma lumfashin yana neman ɗaukewa. Na fita da gudu cikin firgita na kirai dokta David. Tun ranar nan dokta ya canza ma Farid ɗaki, ba mai ganin shi in ba Bashir ba. Sai da muka yi sati ba wanda ya gan shi. Na dukufa ga roƙon Allah.

Na sauko daga aiki na biya makaranta don na ɗauko yara, sai aka shaida mini da Hajiya ta zo ta tafi da su. Don haka ban yi wata-wata ba na je asibiti.

- Hajiya ashe ku kuka je kuka ɗauki yara?

- E! Tare muke, suna wurin babansu. Yanzu don Allah Farida, rishin lafiyar Farid ce ta sa kika lalace haka? Duba yadda kika koma.

- Har ma ta fi mai rishin lafiyar rama, inji tanti Hawa.

Riyanatu da Inna suka fito daga cikin asibiti. Riyanatu da kyar take tafiyadomin tsofon ciki ne da ita. Na gaida su, na ba Inna wuri ta zauna. Na tashi na koma kusan tanti muka ci gaba da hira. Bashir shi da yara suka fito daga wajen da su Riyanatu suka fito ɗazu. Su Shamsu suka zo da gudu suka faɗa bisa ni.

- Mama, Mama mun ga baba, ya ba mu bonbon.

Na ji wani daɗi kamar na tashi na yi rawa. Da ma Shamsiya ce mai yawan ɗumi amma Shamsu ba ruwanshi. Irada tana da surutu amma ba kamar Shamsiya ba domin in ta fara surutu sai in na ba ta kashi take bari. Haka Farid ma yake da ɗumi da son ba da dariya. In ya fara zance sai na yi barci na bar shi. Bashir yana kallon ta yana dariya.

- Farida ina jin duk cikin yayanku Shamsiya ce ta ɗauko surutun Farid.

- . Bari Bashir ba ka sani ba, ai Irada ta fi Shamsiya surutu.

- Tanti, Shamsiya ta fi Irada surutu. Ku da kanku kun sani sarai. Wai don mi ba ku shiri ku da Irada?

Na tambayi tanti.

- Yaya za a yi na shirya da kishiya?

- Iradar da ma jiya da zuwanmu ta tambayi innarki Kaltumi wai ta faɗa ma Alhaji ya karɓi motar daga wurina. Amma Irada kin ji daɗinki wai har da ce ma Alhaji ya kore ni. Na ce mata sai dai ya kore ni daga gidan. Amma motar ba dalar Alhaji ciki.

- To na ce Alhaji ya amshe motar ne domin in za mu shiga motarta wai sai kowa ya kwaɓe takalmanshi. Abin da motar ba ma tata ce ba take ƙwambo da ita.

- Ke, zan ba ki kashi yanzu. Sake magana na ji, yanzu ki yi kuka, na ce mata.

Ina mata faɗa sai su Hajiya suka mini ca, kowa na mini faɗa, wai in bar matsa mata. Bashir ya juyo gare ni.

- Na tafo na miki waya aka ce da ni kin fita. Farid ne ke neman ki.

Farin ciki kamar na zuba ruwa a ƙas na sha. Na kalli Riyanatu muka yi dariya har tanti za ta juyo na kwaɓe kaina. Kunya ta hana ni tashi, sai da ya fara magana sa'annan na tashi na bi shi. Ya ƙwanƙwasa ƙofar, Farid ya amsa. Farid na zaune daga shi sai guntun wando. Jikinshi ya yi kala biyu, da ja da baƙi. Tun da na

shiga ya ware hannuwansa wai na faɗa a ƙirjinshi ya rungume ni. Na tuna da muna tare ne da Bashir. Na kalle shi ya kauda kai. Na jawo kujera na zauna ya taso ya zo inda nake, ya zauna a kan hannun kujerar da nike zaune, ya rungume ni, kunya ta rufe ni kaina duƙe cikin kujerar. Shi ko Farid bai damu ba, wai har da mamaki.

- Mi?! Kunyar Bashir kike ji ne? Wa ya kawo shi? Kai Bashir ka san sarai da ba ka hana ni in wala da matata.

- Wallahi ba ka dai san kunya ba.

- Kai da ka san ta Bashir wace iri ce? Ja ce ko baƙa? Mutum ce? Ko dabba ce?

Bashir ya yi tsaki ya bar muna ɗakin, Farid na ta mashi dariya. Farid ya koma bisa gadonshi ya zauna, duk ban ɗaga kaina ba.

- Farida komo bisa gado mana.

Na ɗaga kai tare da yi mashi irin murmushin da na san yana matuƙar kwantar mashi da hankali.

- Farida komo bisa don Allah.

Yana magana cikin murya lallausa. Ya tsare ni da kallo tamkar rannan ya fara gani na.

- Farid, nan ma ya isa. Ina jiki?

Ya yi ajiyar zuciya.

- Jiki, bai ma kai a shaida miki ba, na gode Allah. Gobe da misalin ƙarfe bakwai za a sallame ni. Wuri biyu ne bai ida warkewa ba: ƙarƙashin hammatata da ƙarƙashin cibiyata.Kin san wurare ne inda iska bai shiga. Yanzu a gida likita zai dinga zuwa ya mini magani. David ƙwararren likita ne. Wallahi ya san aikinshi.

- Bari! Da na tarar da kai, na yi, na yi, ya bar ni na tafi da kai a ƙasar waje, ya ce mini ba komi ka warke cikin sati biyu.

- Farida mi ya same ki ne?

- Abin da ya same ni? Da aka yi mi?

- Da kika rame haka kamar ba ki da rai.

- Har ka ba ni tsoro! A gaskiya Farid, ciwonka ya razana ni har na bar cin abinci.

- Yanzu kam na warke.

- To tun daga ranar yau ki fara shan kayan ƙiba. Ba na son mace busassa. Ki dinga ci kina ƙoshi, kin ji Farida? Kuma ki dinga yi mini kwalliya kamar yadda kika saba yi mini a da.

Muna tsakar hira sai aka ƙwanƙwasa mana ƙofa, na amsa.Shugaban ƙasa ne ya shigo tare da masu rakiyarshi.Ya zauna muka yi kamar minti biyar muna hira. Sannan ya tashi ya koma. Tun da na dawo gida, ina ta faman gyaran gidanmu. Na wanke ɗakunan benen, na share su, ba inda ban gyara ba. Na canza labulen bango da na falon ƙasa da na falon sama. Duk wanda ya san gidanmu a da, in ya gane shi yau ba za ya ce shi ne ba. Na gyara ɗakinshi tsap na wanke duk illahirin tufafinshi, na mashi guga na fesa ma kayan turare, na saka su inda yake aje su. Na yi wanka na ci ado, na sauko a falon ƙasa, na shiga gwadala na fara girki don in shirya masu karin safe. Da misalin ƙarfe takwas da minti shida aka danna ƙaraurawar ƙofa. Irada da Shamsiya suka je da gudu suka buɗe ƙofar. Hayaniyasu ta sa na gane da su Farid ne suka shigo. Ina jin su, na ƙi fitowa, sai can na ji Bashir yana tambayar yara ina nake. Shamsiya ta zo da gudu wurina, na kamo hannunta muka shiga falon na durƙusa na gaida su baba da ke zaune. Na tashi na je na ɗauko musu karin-su na kai bisa teburin cin abinci. Da suka ƙare ci, sai Farid ya koma ɗakinshi ya ce Shamsu ya je ya kirayo ni. Kunya ta kama ni, na ga yaya zan yi in wuce gaban su baba na shiga ɗakin Farid? Sai na ce ya ce mashi ina zuwa. Bayan minti shida sai ga shi cikin gwadala sanye da farar jallabiya. Ina ta famar gyaran zabbi domin angona bai cin kaji sai zabbi. Ya yi tsaye ƙofar gwadalar, ya jingina ga bango.

- Farida ba ki ga Shamsu ne ba?



- Na gan shi.
- To aikinki ya fi kirana ko?
- Farid wallahi kunyar su baba nake ji.
- Ga ni ga ikon Allah! Kunya? Ko gabansu ba ni wasa da ke kike ji kike gani?
- Don Allah ka rufa mini asiri.
- Ina kika sa takalmana?
- Suna cikin armuwar.
- Da ma su nake nema.

Kan ka ce ƙarfe goma gidanmu ya cika maƙil da ɗan Adam, sai da Zainabu da Ummu suka taya ni girki. Da muka zuba musu abinci sai muka je falon benen muka yi abinci muka, shiga hira. Har ƙarfe goma sha biyun dare abukkan Farid suna cikin gidan-mu. Na yi wanka na bi lafiyar gado. Da yake na gaji tun da na kwanta wani barci mai ƙarfi ya share ni.

Ƙarfe ɗaya da rabi na ji ɗakina ya garwaye da ƙamshin turaren Farid. A zatona mafarki nake. Sai na ji saukar ruwa ga goshina. Na shafe shi cikin barci, ashe ruwan kanshi ne da yake sharcewa. Ya busa cikin kunnena, na sa hannu na murje kunnena. Ya sake busawa, sai na zabura. Ya riƙe ni yana dariya.

- Ina za ki ne? Tsoro! Ko barcin ya yi dadi? Tashi mu sauka ƙasa ina son yin magana da ke.

Na tashi na bi shi dai har cikin ɗakin barcinshi. Na zauna bisa gado, ya janyo kujera ya zauna gabana. Na sunkuyar da kaina, ya sa hannunshi, ya ɗago fuskata.

- Farida ji mana ina son ki saurare ni da kunnen basira. Ba zan ce in tono abin da ya rigai ya wuce ba, domin mun rigai mun yafe ma junanmu, ko ba haka ba? Farida na ɗauki alkawarin ba zan sake ɓata miki rai ba sai abin da ya fito daga wurin Allah, watau sai ƙaddara. To, haka nake so ke ma ki yi. In na miki laifi ki gaya mini take-yanke, don na roƙe ki gafara, domin ni ma haka zan miki. Kin fahince ni? Abin da nake so da ke mu koma zamanmu irin na da ko fiye da haka ma, kar da mu sake bin son zuciya kuma. Allah ya albarkaci aurenmu, ya kuma taimaka muna mu tarbiyantar da yayanmu don su samu horo na gari. Ya ba mu yaya kamar goma sha shida. Ko gimbiya Farida? Ba ki ce mini komai ba.

- Mi kake so na ce maka?
- Ba ki san abin da za ki ce mini ba?

Ya taso yana ja na da wasa. Na yi tsalle sai wancen gefen gado. Ya hau gadon ya kamo ni. Na koma inda nake, ya ƙara kamo ni, ina mashi gwalo. Har zan fita waje sai ya yi sauri ya kamo ni ya jefa ni bisa gado.

- To na kamo ki.

- Ai dai na ba ka wahala kan ka kamo ni.

- Ba dai na kamo ki ba. bari dai duk wuyar da kika ba ni tsawon shekara huɗu zan rama ta daren yau.

Gabana ya faɗi.

- Mi na maka? Ka ce shekara huɗu?

- Shekara biyu kika yi a gida, shekara biyu kika yi tare da ni kina gallaza mini. Amma Farida kin isa!

- Farid, ba yanzu ka ce mu bar tado abin da ya wuce ba? Fansa za ka ɗauka a kai na?

Ya yi dariya, ya dungure ni.

- Abin ƙaunata, kin san kin taushe mini hakkina tsawon shekara biyu. Shi ne na ce zan ɗau fansa daren yau...

Na yi raurau da idanu.

-...Tsoron mi za ki ji ne? Ke wasa nike, kwanta ki yi barcinki.

Karar talabijin da yara suke kallo ta ta da Farid daga barci, ya yi miƙa yana salati. Ya ɗauki agogo: ƙarfe bakwai da minti arba'in. Salatin da yake ya sa na farka.

- Farida, ba mu yi sallar asuba ba har yanzu ƙarfe bakwai da wani abu.

Na tashi na yi wanka, na fito falo na shiga shirya karin kumallo. Farid ya zo, muna girki tare.

Tun ranar nan Uda, har zuwa yau, ko gardama ba ta taɓa shiga tsakaninmu ba. Haka dai muke tafiyar da zaman aurenmu cikin farin ciki, da jin daɗi da nishaɗi. Uda, yanzu haka in muna zaune, ko tagumi na yi sai hankalinshi ya tashi. Sai ya yi zaton ko ba ni da lafiya ne, ko wani laifi ya mini bai sani ba.

- Amma Farida labarinki na da ban tausayi. Daga ke har Farid ba wanda bai sha wuya ba.

- Amma kin san na fi shi shan wuya.

- A'a Farida, ya fi ki shan wuya.

- Ke Uda, wuyar da ya sha ai tsakanin mu ne. Ni fa gaban mace yar uwata ya riƙa tozarta ni.

- To ni ban san abin da zan ce ba. Yanzu Farida har haka kuka sha wuya? Da ma an ce bayan wuya sai daɗi.

- Uda, wuya ai ni na sha ta, ba shi ba.

- Ashe? Ni mamaki nake yaya za a yi namiji ya so matarshi haka kamar yadda Farid ke son ki? Farida, kin san da babu biyunku duk faɗin duniyar nan!

- Akwai waɗanda ma suka fi mu, don dai ba ki gani ba ne. Uda, ya kamata labarina ya zamo miki gargaɗi, ya zame miki darasi. In kika ɗauki gargaɗina za ku ma wuce mu wajen more ma zaman aure. Domin ba wani abu ba ne mai wuya. Kawai biyayya ce da haƙuri. Shi ne maganin zaman duniya. Kin ga da Farid bai ɗau haƙuri ba, da mun rabu. Domin na rigai na gaya miki shekara biyu muka yi ina gallaza masa kuma ko ruwan gidanshi ba na sha balle abinci. Magana ma ba ta gama ni da shi ko "ina kwana". Tun safe in na fita sai lokacin da na shigo. Bai kuma isa ya tambaye ni inda na je ba. A haka ko ya zauna da ni. Dama an ce haƙuri shi ne so.

- Farida, da dai na so in koma ƙasarmu, amma tun da na ji haka, zan zauna in daure, in ɗauki haƙuri. Na ji bayyaninki na kuma gamsu da shi. Allah ya bar mu tare. Farida daga yau ko Taleb ya dunguri ƙeyata, ya ce in fita zan dawo na zauna.

- Madallah, Allah ya miki albarka, yanzu sai ki tashi ki koma gidanki ko?

- To Farida, sai an jima.

- Bari na ɗauko miki turaren wuta da sabulin wanka.

- To Farida, na gode.

Na hau bene, na ɗauko mata gwangwanin turaren wuta da sabulin wanka da turaren shafawa ga jiki, na saka cikin leda, na ba ta. Na raka ta har gindin motar da Farid ya sawo mini yau da wata uku da suka wuce. Na ba direba makullan, ya maida ta gida.

Na dawo na zauna ina nazarin rayuwar aurena: a gaskiya zaman aurena ya so ya gurɓace amma yanzu alhamdu lillahi na gode ma Allah. Farid yana so na, har bai da sha'awar wata mace. Da man gurin kowace ɗiya mace kenan. Ina matuƙar faranta masa rai fiye da yadda yake zato. Sai da na mamaye duk gurin zuciyarshi ba gurbin da wata mata za ta shiga. A farkon aurenmu Farid ne ke matuƙar so na. Ko na ce in nuna mashi so sai kunya ta kama ni. Amman yanzu na ƙware wajen nuna masa na fi son

sa da kaina. Haka ya sa shi ma in yana gari bai minti biyar bai buga mini waya ba. Allah kenan.

Karfe tara na dare muna zaune ni da yayana muna kallon talabijin sai waya ta yi ƙara, Shamsiya ta ɗauka ta yi ihu tana rawa.

- Mama, baba ne.

Na tashi da sauri na karɓi wayar.

- Alo Farid! Ina wuni? Ina gajiya?

- Gajiyar kam akwai ta gimbiya. Farida rishin ki kusana na matuƙar damu na.

- Farid ka ɗau haƙuri; ɗan kwanan biyu da za ka yi sai ya tayar maka da hankali?

- Farida, kwana biyun nan tamkar shekara biyu ne a gurina. Farida ki tausaya mini ina cikin ƙasar da ba ni da kowa a kusa da ni.

- Farid, na tausaya ma ni ma da nake Yamai sai na ga garin ya fita raina tun da ba ka nan tamkar cikin hamadar Tenere nake. Wayyo Farid! Allah ya maido ka lafiya, ka tarar da mu lafiya. Karfe nawa jirginku zai sauka ne?

- Karfe uku na yamma. Ina yara? Gama ni da su.

- E! Wallahi Farid, har zan manta. Ga su. Bari na fara da Irada.

- Ba ni Shamsu dai namijin duniya. Ba ga hannunshi na bar ku ba?

- Kai dai ga Irada. Ina alƙawarin kyautar da ka mata? Yanzun nan ta tuno mini shi.

- Alo baba, ni ce Irada. Ina wuni?

- Lafiya lau yar mama don mi ba ki tuna mini ba. Yanzu mi kike so na zo miki da shi?

- Duk abin da kuka kawo mini baba.

- A'a Irada fadi da kanki. Na san halinki kar na sawo miki ki koma daga baya ki ce ma mamarki bai da kyau.

- Baba duk abin da ka sawo mini.

- To na ji, ba ni ƙannenki.

Shamsu ya karɓi wayar.

- Assalamu alaikum baba.

- Wa alaikumus salam namijin duniya. Ka kula mini da gida, ka ji? Kai kaɗai ke namiji cikin su.

- To baba.

Yana murmushi, na kalle shi.

- Gulmata kuke ko?

- A'a Mama.

- Shamsu, kai da wane ne kuke magana? Inji Farid daga cikin talfo.

- Mama take tambaya ta wai ko gulmarta ake yi.

- Kai ƙyale ta. Kun je makaranta?

Wurin baba malam suke zuwa makarantar allo duk ranar da ba su zuwa makarantar boko.

- Mun je, amma baba malam ya tafi wurin zaman makoki.

- Allahu akbar wa ya mutu?

- Malam Sambo.

- Allahu akbar! Allah ya rahamshe shi, Allah ya sa kwanciya hutawa ce.

- Amin. To bari na ba ku Shamsiya.

- Assalamu alaikum baba! Baba, na ji da za ku tafiya kuka gaya ma kowa ban da ni, kuma kowa ya rubuta tsarabar da za ku kawo mashi sai ni. Baba wallahi ni ban yarda ba.

Farid ya yi dariya. Ya san da lallai da muke ce mashi Shamsiya na da surutu, gaskiya ne, don gashi yanzu ta fara, ta hana shiya maganta.

- Bari na yi magana mana. Ban gaya miki ba? Ai a lokacin ba ki gida kina wurin yawace-yawacenki...

Shamsiyya tazabura za ta magana, Farid ya tare ta.

-... Ke, ki bari in yi magana. Ni ba na son yawan surutu. Mi kike son na kawo miki?...

Ta ɓata rai ba ta amsa mashi ba.

- ...Shamsiya fushi kika yi ne? Haba yar baba ki yi haƙuri kin ji. Mi kike so na kawo muku? Kaya iri ɗaya?

- To wane iri za ku kawo ma Irada?

- Ina ruwanki? Ke dai fadi naki. To na ji, ba ni mamarku.

Na karɓi wayar.

- Farida kin ji rigimar da muke ni da Shamsiya? Pap-pap, amma akwai dimi gare ta. Cikin minti uku ta kai zance goma.

- Kai ta biyo, don ka san da ni ba ni da dumi.

- Ta fi ni. To zan bar ku nan ko? Ki saurare ni cikin mafarkin-ki, zan zo.

- To, ina jiran ka, sai ka zo.

Karfe biyu da rabi, ni da yara muka nufi filin jirgi. Muka shiga inda aka tanada don shaƙatawa, muka zauna, na saya musu

lemu. Muna sha sai ga jirgin su Farid muka tashi. Da ya rego kai sai yara suka kama kiran shi, suna ɗaga mashi hannu. Ya fito yana ta fara'a. Ya nufo mu, yara suka tarye shi da gudu. Ya ɗauki Shamsu da Shamsiya. Irada ta kama hannunshi, ina jingine ga mota. Da suka isa inda nake, Farid ya sumbace ni, muka shiga mota sai gida. Farid ya yi wanka ya fito muka shiga cin abincin da na dafa don saboda zuwanshi.

- Farida albishirinki.

Na aje koshiyata na kalle shi.

- Goro fari pas zan ba ka. Ka san dai ka wuce matsayin da za a ba ka goro ja. Ina jin ka.

Na ɗora hannuna bisa nashi, na lamgaɓar da kaina, ina kallon shi tare da murmushi. Ya yi ajiyar zuciya.

- Farida, wani babban albishir nake ɗauke da shi, inji shi, tare da ɗaga hannuwa sama yana godiya ga Allah: Allah! Allah na gode ma. Farida ƙasar Swis za mu koma da zama.

Na kalle shi cikin mamaki.

- Swis fa ka ce! Ban gane ba, Swis? Don Allah ka bari!

- Farida Swis! Domin tafiyar nan da na yi da ma wurin zaɓe muka je. Ban shaida ma kowa ba sai baba malam. Kuma Allah da ikonshi, da taimakon baba malam ni aka zaɓa cikin yan takara hamsin a matsayin mataimakin mai ajiyar kuɗi na babban bankin nan da kika sani.

Kaina ya yi wani nauyi. A zatona mafalki ne nake, sai da Farid ya maimaita mini tukwana na san da gaskiya yake faɗa. Hawaye suka yi ta zubo mini na tashi na faɗa bisan shi. Farid ya kamo ni ya rungume ni yana rarrashi na.

- Farida, ya kamata a ce kina farin ciki ba kuka ba.

Da kyar ya samu ya rarrashe ni na bar kuka. Da muka koma ɗaki sai ya ɗauki waya ya yi ta sanar da jama'a. Ina kwance ina kallon shi.

- A ƙarshen watan nan, na san kuɗin da za ka biya a gidan waya zai kai milyan.

Ran wata laraba da dare aka ma Farid waya, aka ce ana jiran mu.

Da Farid ya sanar da ni sai da na yi gudun dawa. Ba don komi ba sai rabuwar da za ni yi da iyayena da abukkaina. Ran juma'a da dare, ana gobe jirginmu ya tashi, ina kwance na ɗora kaina bisa ƙirjinshi sai wayar hannunshi ta yi ƙara, ya ɗauka.

- Bashir kar da ka dame ni fa, domin ina tare da iyalina.

- Kai, kaɗai kake da iyali?

- Ko kowa yana da iyali ai ni nawa na sani. Kai ba na ɗai son surutu, mine ne?

- Farid, don Allah ka zo da gaugawa ina son ganin ku don Allah, don Allah.

- Mi nene wai?

- Ba komi, kai dai ka zo.

Na tashi na shirya, muka shiga mota sai gidanshi. Ni nike jan motar, domin da zaran muna tare da Farid ni nike jan mota. Muka yi mamakin ganin an kashe wutar lantarkin da ke gidan su Bashir har mun kawo ƙofar falon ba kowa.

- Farid ko ba kowa ne?

- Ina za su? Mu shiga mu gani. Amma Bashir ya isa! Wane irin rishin mutunci ne wannan! Bashir ya rena mini wayo. Haka kawai sai ya kirai mu ya yi tafiyar shi!

Maganarmu ta sa ya fito waje. Farid ya harare shi.

- Ina wuninku?

- Ina ruwanka da wuninmu? Kai, ba na son renin wayo! Kiran mine ka mini?

Farid yana yiyana dariya. Ya kama hannunshi.

- Ina za ka da ni? Ka san gobe za mu tafiya, ka sake ni, gida za mu. Ke Farida mu je.

- Na haɗa baki ne da yan fashi su kashe ka, inji Bashir.

- Kana iyawa! Ba bahullace ne ba kai? Amma na san dai ba tare da ƙaunarka ba ko.

- Ku dukan ku.

Ni dai ina tsaye gefe ɗaya ina kallon su, ina murmushi. Bashir ya kama hannunshi na bi su har cikin falo. Daga shigar mu, Riyanatu ta kunna wutar lantarki, jama'a suka ɗauki taɓi. Ashe duk abukkanmu da yan uwanmu suka taru don farin ciki. Taɓin ya rikitar da ni domin ban yi zaton haka ba. Bashir ya nuna muna wurin zama. Ina ta mamaki. Bashir ya fara jawabi.

To yan uwa, domin ba zan ce abukkai ba, tunda mun zama yan uwa. Na gode da kuka cika alkawari domin mun gama baki cewa kar da wanda ya shaida masu wannan abin da muka shirya. Farid da Farida, Kamar yadda kuka gani, wata yar liyafa ce

na shirya muku albarkacin tafiyarku, ya kuma zo daidai da ranar cikon shekaru goma sha biyu da yin aurenku.

Ni da Farid muka kalli juna. Duk mun mance abbukanmu. Sun kai su ashirin kowa da matarsa. Cikin su ba wanda bai muna kyauta ba. Teburin da ke gabanmu ya cika makil da kyaututuka. Bashir da Riyanatu suka ɗauko wani babban kwali. Da kyar suke ɗaukar shi, suka aje shi gabanmu.

- A matsayina na surikinka ga tawa kyauta ni da uwargidata Riyanatu, inji Bashir.

- Ba kunya ba tsoron Allah! Kai duba, ni ba surinkinka ba ne, ka dai rike matsayin ka na babban aboki.

- Kai ku ji shi, ni ba yayan Farida ba ne?

Ni da Farid muka warware kwalin a hankali. Sai wata babbar ɗiyar wasa ta fito tana kukan jarirai. Haba mana! Sai kowa ya tuntsunre da dariya. Bashir na ta dariyar ƙeta har da hawaye. Farid ya je ya ja shi suka fara kokowa sai ka ce waɗansu yara.

Da aka ƙare muka koma gida muka zauna muna hira. Kowa na ba da labarin farkon hirarshi da yan mata. Muna ta dariya abin gwanin ban sha'awa kamar kar mu rabu.

Na gabatar da sallar asuba. Ina zaune bisa gado, na yi tagumi. Daidai lokacin nan ne Farid ya shigo ya dawo daga masallaci ya tsaya gabana, ya taɓa goshina.

- Farida kin sha maganin kuwa? Jikinki har yanzu yana da zafi. Farida kar ki tayar muni da hankali mana! Kar ki sa na ɗaga tafiyarmu mana.

- Farid duk wannan kai ka jawo mini shi. Rishin lafiyata ai laifinka ne.

Ya yi dariya.

- Na sani. Farida laifina ne. Rishin lafiyarki ai ta alheri ce ko? Tashi ki shirya, kar da mutane su zo ba ki shirya ba.

Da misalin ƙarfe bakwai da rabi, muna filin jirgi, sai ka ce kasuwa. Yan rakiyarmu sun fi arba'in. Ina ta kuka su Hajiya da tanti da Inna suna ta mini nasiha. Muryar wata mace ta ce: "Ana kira ga masu shiga jirgi da su je osfishin yan sanda". Muka je muka sa hannu ga waɗansu takardu. Bashir da Riyanatu da Ali da Zainabu da Umu da Uda da Taleb suka raka mu har gindin jirgi.

- Farid yaushe za ka dawo ka tafi da yara ne? Inji Bashir.

- Farida za ta dawo wurinsu. Ita ƙin ma sai in ta zo da sabon jinjirinmu.

- Da sabon jinjirinku? Yaya? Ban gane ba, ciki ne gare ta?

- To! Mi kake nufi, ciki ne gare ta mana. Kana zaton ni raggo ne ƙamar ka? Kun rigai mu yin aure amma da kyar ka samu yaya biyu. Raggon banza.

Kunya ta kama ni, na sa mayafina na rufe fuskata.


Bashir ya kai mashi ƙulli, suka fara kokowarsu sai dai ka ce yara.

- In na same ka sai ka gaya ma yan garinku.

- Yanzu Farida ciki ne gare ki shi ne ba ki sanar da ni? Inji Riyanatu take tambayata.

- Ba ki san bafullacen mutum ba da zurfin ciki, in ji Zainabu, muna dariya.

Muka yi ban kwana da jama'a, muka shiga jirgi. Na zauna kusan Farid. Ya jawo ni ga jikin shi, yana shafar hawayen da ke kwarara daga idanuna. Sai wata kyaukyawar budurwa, cikin masu hidimar jrgin, ta zo kanmu, ta shaida mana cewa mu ɗaura tankiyon kujera, jirgin zai tashi. Cikin minti uku jirginmu ya tashi. Da ya kai daidai unguwarmu, na nemi gidanmu, amma ina! Jirgin ya yi sama, daga mu sai gizagizai!





Salmu Hassan, an haife ta a shekarar 1972, cikin birnin Yamai. A halin yanzu, tana karatu a fannin falsafa na tsangayar adabi da nazarin halayyar ɗan Adam, a jami'ar Yamai. Sakamakon sha'awar da take da ita na karatun littatafan " *dandalin soyayya*", ta shiga rubuce rubuce cikin Hausa. Bayan wannan littafi nata mai suna ***"Bayan wuya"***, ta rubuta wani littafi mai suna "***Mahaƙurci mawadaci*** " wanda a halin yanzu yake kan hanyarshi ta wallafawa.

"Wata rana a sha zuma, wata rana a sha maɗacci!" Haka dai duniyar soyayya ta gada.
Ita dai Farida, ta fara sanin Farid ne a wani haɗarin mota inda ya banke ta. Bayan ta warke ne, Farid, abokin yayanta Bashir, ya nemi aurenta, aka ba shi, duk da ƙiyawar da ta so ta yi da farko. Suka kwashe lokaci mai tsawo suna zaman aurensu cikin girma da arziki, da girmama juna, da ladabi da biyayya, da jituwar gaske. Har aka kai lokacin da Farida ta ji tausayin wata ɣar marainiyar Allah, wadda ta mayar tamkar ɗiyarta ta cikinta. Ta yi ta mata abubuwan alheri, da goma ta arziki iri-iri. Amma uwar Fatsuma, da ta tashi gode ma Farida, sai ta ƙulla duk abin da ya sanya ta aurar da ɗiyarta ga Farid. Saboda makirci irin na ɣan gidan su Fatsuma, zaman lumana da kwanciyar hankali suka ƙaura daga auren su Farid da Farida.
Daga nan fa, Farida da Farid suka shiga wani mawiyacin halin rayuwa...

Rikicin soyayya 1



ENITEX

Launin zane

2PEB gtz

unicef